An dauko wannan littafi daga shafin www.arewanovels.com.ng ku ziyarci shafin na www.arewanovels.com.ng domin samun kayatattun littatafan hausa kama daga kan na yake yake dana soyayya

Marubuci ko marubuciya zasu iya turo mana da littatafansu mu dora masu a shafinmu kyauta don masoyansu su rika Downloading a online,

Sannan marubuta zasu iya turo mana da tarihin rahuwarsu da tarihin rubutunsu, dama sharhin littatafansu don masoyansu su gani kuma su karu da hakan
Domin turo mana da littafi ko tarihin rayuwar marubuci ko marubuciya sai ayi mana magana ta whatssap da wannan nambar +2347032707179

A lura dakyau - kyauta muke saka littafi a shafinmu bama amsan ko sisin marubuci, duk wanda ya amshi kudinku da sunanmu babu ruwanmu,

Alura dakyau - manazarta bama tura littafi ta private ku dena binmu private kuna neman mu tura maku littafi, duk mai bukatar littafi yaje website namu

Alura da kyau - Littatfanmu suna fitowa cikin manhajoji uku ne PDF,TXT da DOC amman munfi amfani da PDF da TXT masu amfani da wayar android ko tablet ko computer zai fi kyau ku riga dauko PDF da DOC

Masu amfani da kananan wayoyi java ko mara java TXT zakuna zaba don shine daidai wayarku

This hausa novel was uploaded and downloaded from www.arewanovels.com.ng
You can download more hausa novels there
Also you can send us your novel to upload it in our website for your fans to download it online
It is free we do not charge for uploading novel
Also if you are an Author be it online or Non online you can send us your biography including your book summary,commentary and others via this number +2347032707179 its free we do not charge for our services

Note that - we do not charge for our services we uploaded novels and posted biography free, any person that collect your money in our name is your fault do not blame us

Note that - pls readers stop calling us and be asking us to send you a novels we are not sending novels through whatssap or private our novels is public at any day, any time you can visits our site and download it

Note that - our ebooks came as PDF,TXT or DOC format but the popular format are PDF or TXT, those with android or tablet or pc we suggest you to download PDF or DOC
those with java phone or non-java phone we recommend you to download TXT

—
WHATSAPP NO:
+2347032707179

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 1

2:00pm
Jirgin yasauka a
Nnamdi Azikiwe International Airport
Tun daga matattakalar jirgin nake iya hango wata kyakkyawar yar matashiyar budurwa a kalla zata iya kaiwa shekara ashirin da biyar a duniya
doguwa ce sosai sannan tana da Dan matsakaicin jiki sai manya manyan idanuwanta da dogoyen eyebrows dinta masu matukar baki
Sai Dan madaidaicin lips dinta dayasha red lipstick .
English wears ne ajikinta masu matukar daukar ido Dan wainsu stones ne ajikin rigar da wandon da sukayi matukar matseta sannan sai Dan karamin gyalen data rufe gashin kanta dashi saidai hakan bai hanani ganin tsayin gashin ba .
Fuskanta a daure yake tunda tasauko daga jirgin sai rarraba idanuwa takeyi ko zata ga Wanda yazo daukanta
Dogon tsaki tasaki sannan naga tasanya Zara zaran hannunta acikin yar madaidaiciyar handbag dinta na kamfanin Gucci
Wayarta tacuro iPhone 7+ pink color sannan tafara kokarin danna Kira da alama tagaji da raba ido saidai kafin takai wayar kunnanta ta hangi wacce taketa jiran dogon tsaki takara tsaki akaro nabiyu sannan tawurga wayar acikin handbag takuma hade rai .
Matashiyar budurwar ce takaraso tace I'm so sorry pinky harara ta wurga mata sannan tace haba leema tun yaushe kikasan naketa raba idanu kozan ganki mutane sai bazamun idanuwa sukeyi mtsw takuma Jan tsaki wacce aka kira da leema tace yi hakuri Dan Allah yanzu dai muje Dan karamin akwatun hannun pinky ta amsa tana kuma bata hakuri atare suka jera suka karasa inda leema tayi packing motar ta wajen me zaman banza pinky tabude tashiga leema kuma dasauri tasa akwatun a booth tazagaya tashiga driver side ta tada motan suka bar haraban wajen.

Juyawa leema tayi tadan kalli pinky sannan tace pinky Dan Allah ki tsaki ranki kinsan fa babbar harka zaayi kuma dole ki dage wajen kara mallake zuciyar minister harfa kyautar mota

yamun Dan dai kawai in hada mai connection dake
Tsakin murmushi naga pinky tayi sannan tace da alama zan kwasa naira wajen tsohon ala kwankwan din daria leema tayi tace sosaima kuwa Dan inaga har Dubai sai kunje Dan da alama baicika son harka anan kasar ba
Murmushi pinky takuma yi dan har saida Dan dimple dinta ya losa sannan tace kafin dai inhadu dawani minister sai munje hotel nayi wanka nayi sallah sai mutafi OK leema tace !
kai tsaye Western Dreams Hotel suka nufa dayake daman leema tayi musu booking
Leema daidai inda zatayi parking tabige wata mota dake niyan fita daga hotel din ai dasauri tafaka motar tafita pinky ma haka ganin me motar sukayi yana duba inda aka bugar mai a hankali yadago yakallesu daga sama har kasa sannan yaja tsaki leema kam dasauri tace Dan Allah Kayi hakuri matsifa yafarayi yace inbanda rashin hankali da kamun kai mezaisa abugar mun mota pinky dogon tsaki tasaki sannan takalli leema tace muje Dan Allah idan kaso kada ka hakura Dan rainin hankali Ana bashi hakuri yana wani tada ma mutane jijiyoyin wuya kallonta kawai yakeyi zuciyarshi namai wani zafi dakatar da ita yayi sannan yace ke wacece juyowa tayi takalle shi tana wani karkada idanuwa tace sunana pinky sannan taja hannun leema sukabar wajen
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 2

Buga motar yayi dakarfi da hannunshi yace damn it takosan koni wanene lallai saina koyama yarinyan nan hankali
Kara kallon inda suka buge mai yayi yaji wani bakin ciki
Abunma dayafi bata mai rai favourite car dinshi ce and even the Color black tsaki yaja

yashiga motar yabar haraban hotel din
Room 105
Aka basu suna shiga pinky tace wash nagaji wlhi ita dai shuru leema tayi Dan taga lambar motar guy dinnan da alama Dan gidan mr president ne kallonta pinky tayi sannan tace hey what's wrong wit yhu kada dai kice mun a tsorace kike
Uhmm leema tace sannan tace yaron mr president nefa I think so tsaki pinky tayi tace so what ni kinga Bari inshiga in wasa ruwa tunkan kibata mun rai uwar tsoro .
Leema tace bazaki gane bane idan har shine Dan president wallahi zaman abuja sai yagagare mu ko tankata pinky batayi ba tashige bathroom tasakar ma kanta shower !
Dan ita Sam batasan tsoro ba Dan daidai take da uban kowa ma

Bata jima ba tafito daure da tawul a inda tabar leema tasa meta daria tafashe dashi tace kinban kunya wallahi banza leema tamata Dan ita a tsorace take
Tabe baki pinky tayi sannan tashirya cikin wainsu arnakun English wears riga da wando sunyi matukar fito mata da duk wata surar jikinta hijabi tasaka ta tada sallah tana idarwa tazauna zaman kwalliya .

Saida tagama tafeshe jikinta da alia sannan tadauki handbag dinta takalli leema data rafka uban tagumi tace baby am done muje danna kosa inji masu mutane biyu a hannuna dakyar leema ta tashi tamikawa pinky key car din murmushi kawai pinky tayi sannan suka fice.
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 3

Parking space suka karasa pinky tashiga driver side leema kuma tashiga wajen me zaman banza .

Sannan pinky ta tada motar sukabar haraban cikin hotel din
Saida sukayi nisa da hotel din sannan pinky tace uwar tsoro ina mukayi
Leema tace maitama OK kawai pinky tace sannan tayi hanyan zuwa maitama wakar Chris brown tasaka tadan kure volume a hankali take bin wakar har suka karasa maitama sannan leema tafara nuna mata hanyan daza tabi har zuwa guesthouse din minister
Daidai wani katafaran gida suka tsaya pinky tayi horn saida gate man din yaleko tukunna ya wangale musu gate din suka shiga cikin haraban gidan
A hankali pinky tace wow leema tace hmm ai saima kinshiga ciki tukunna pinky tace inaga karshen ta gidan nan zansa yabani daria leema tayi hade dacewa nasan Zaki iya
Murmushi pinky tayi ta karkada idanuwan ta

Saida sukayi parking sannan suka bude murfin motan atare suka fito ko wacce rike da handbag dinta pinky tawurga key car din acikin handbag din sannan takalli leema tace muje kinsan yanzu kuma kece yar jagora murmushi leema tasaki sannan tace wannan haka yake

Akusan tare suka jera suka doshi cikin kayataccen parlour din

Parlourn bakaramin haduwa yayi ba saidai ko kadan pinky bata tsaya bin parlorn da kallo ba waje suka samu a daya daga cikin kujerun parlorn suka zauna sannan leema tadauki wayarta dake cikin jaka tayi dialing din number din minister bugu daya yadauka daman kaman jira yakeyi

cemai kawai tayi gamu a parlour daga cen yace OK OK Ku hauro upstairs katse wayan tayi sannan takalli pinky tace yana upstairs muje bin bayanta pinky tayi har suka karasa cikin kayataccen parlorun da minister yake zaune yana ganin pinky yawani wangale baki yamike yaware mata hannayenshi yayi Mata alaman tazo wani mayataccen murmushi tasakar mai sannan takarasa tashige cikin jikinshi welcome yace mata sannan ta amsa cikin tsiririyar muryarta tace thanks dear .

Gyaran Murya leema tayi tace da alama honourable yamance dani anan tunda nakawo ma pinky murmushi yayi yace leema aikinki nakyau ki saurari alert zuwa anjima bude baki tayi tace nagode honorable Allah yabar ma pinky .

zama sukayi akan kujerun parlourn pinky kam har cikin zuciyanta tsohon ala kwakwan nan da alama zay takura mata dayawa gashi kato dashi kuma baki dashi gashi sai uban muni ita kam ta tsani mummuna a rayuwar ta

Amma yaza tayi tunda tana bukatar kudi wajen cikar burinta .

Kallonta minister yayi pinky ta kashe mai ido daya tana tsakar Mai murmushi

Kara jawota yayi zuwa jikinshi yace uhm Allah yayi halitta anan kifada duk abunda kikeso zan baki

Dadine yakamata acikin zuciyanta

Kallon juna sukayi da leema suka tsakar wa juna murmushi

Tabe baki pinky tayi sannan takara kashe murya cen kasa tace

Baby inda so samune sabuwar mota nake bukata yanzu da sai kuma tayi shuru irin jan ajin nan minister yace ke tawa ce kisaki ranki kifadi koma meye

Thank yhu pinky tace sannan tace gidan nan nakeso daria taji yasaki yace indai gidan nanne ayau zan mallaka maki takardun shi

Kasa magana tayi sabida batayi tunanin zay amince haka dasauri ba

Saida ta tattara nutsuwarta sannan tace wow baby thank yhu

You are too much sai tadan kaima peck a kumatu

Wani lumshe ido yayi sannan yace wace kalar mota kike so

Sai insa akawo maki Dan tabe baki tayi sannan tace range rovel 2017 black color hade da tic

Minister yace angama ranki yadade .

tun daga bakin gate nafarko aketa gaidashi hade da daga Mai hannu ko kallonsu bayyi ba duk da wulakanta mutane ba dabiar shi bace

Yau dinne ranshi abace yake

Bama inda ake parking yayi ba Dan ko parking space baya jin zay iya karasawa .

Ko kullle motar bayyi ba yayi hanyan katafaren shiga cikin gidan fuskarshi a hade kai tsaye part dinshi yawuce Dan yana bukatar kadaicewa ko zuciyarshi tayi sanyi

Fadawa yayi kan katafaren gadonshi kirar royal bed saidai wannan yafi Royal bed kyau dakuma girma

Rintsa idonshi yayi pinky kawai yake gani a lokacin da take gaya mai bakaken maganganu buga hannunshi yayi ajikin gadon dakarfi yace waye ubanki a kasar nan ni captain AJ saina koya maki hankali

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 5

Pinky tace magajia itace uwata itace ubana she's my family hawayene suka cika mata ido tace leema nasan rayuwar da mukayi bame billewa bace amma hakan ne kadai mafita a gare mu bansan iyayena ba magajia Kawai nasani ita kadai tunda natashi .

And sai bayan kinzo nakara ji nasamu wata family

Leema ita kanta magajia batasan asalina ba batasan kowa nawa ba itama tsinta ta tayi

Abun dake damuna WAYASAN ASALINA

Leema dafa kafadar pinky tayi tace koma suwaye iyayenki komin Daren dadaiwa Zaki San asalinki please kidaina sa damuwa a ranki

Pinky tace nadaina sabida burina yafara cika ina son inzama fitattaciya ta hakan ne kadai zan iya gano iyayena .

Sannan takai hannu tashare hawayen fuskanta tasaki murmushi tace next week fa zamu koma skool kinsan kuma lectures yawuce mu dayawa leema tace nasani amma kwana nawa zakima minister

Pinky tace ina tunanin four days ai yayi Dan bana son naci irin na tsofaffi .

Bata bari leema tace komaiba taja hannunta tace ke muzagaye gidan muga yanda yake dakuma irin rayuwar daza mufara yi aciki daria leema tayi tace irin wannan kosawa haka .

AJ kai tsaye part din su Mami ya nufa zaune ya tadda kannan shi a parlour suna pictures Mimi tana ganinshi tace yauwa  ga ya AJ pls ya kazo miyi snapping pictures ko so dayane tsaki yaja yace matsalar Ku tayi yawa wallahi yaran nan wai yaushe zaku gama hutun ne kutafi sumayya dake rike da camera din tace maybe next week

Sagir dake tsakiyan su yace pls ya AJ kazo mudauka koso dayane Mami ce tafito daga

bedroom tace haba alamin katsaya Ku dauka mana bata rai yayi yace Mami pls alama tamai daya tsaya kawai sudauka tsakashi sukayi a tsakiya yawani hade rai Mami murmushi tayi tace Alamin smile mana haba .

Dakyar yayi murmushi suka dauki pics din Mimi ce tace gaskiya duk gidan nan sumayya kinfi kama da ya sagir yace aiko a skool ne da anga Sumy zaace kanwar ya AJ wai sunfi kyau sumayya tace ehmana munfi kyau nida ya Dan da abba muke kama Mami tace oho wato kina nufin abbanku yafini kyau daria gabaki dayansu sukayi AJ yace haba ai Mami kinfi abba kyau .

Mami tace aina sani bama saika fadi munba daria su sumayya sukayi yana kallonsu kowa yayi tsit.

sannan yace Mami gobe zanje Dubai Abba yace bazay samu daman zuwaba zayyi baki gobe

Mami tace Allah yakaimu Mimi tace Dan Allah ya kaje damu akwai film din dazaa nuna a cinema ranan Saturday sumayya tace pls ya sagir ma haka OK yace sannan yace bana son takura kuma saiku shirya dawuri mami tace agida zaku sauka ko hotel AJ yace hotel dai ai gidan zay mana ba dadi tunda keda abba baku nan

Mimi tace ya amma dai kaima zaka cinema dinko galla Mata harara yayi yace inada aikin yi saiku tazama kuna cika ma Mami kunne

Daria Mami tayi tace nafi so suringa cikamun kunnan tunda kai bakason yin hira da kannan ka

Baice komai ba yafice yana murmushi yasaba da korafin Mami tuntuni part dinshi yawuce !

6:00pm

Minister yakira leema a waya yace Mata motar Pinky ta iso tana parking space baijira cewar taba yakatse wayan wani ihu leema tayi tace new babe tazo pinky dake shan ice cream tace bangane ba leema tace yanzu minister yakirani wai motarki tana waje pinky

Mikewa tsaye tayi tace OMG leema tace new babe pinky tace wannan yafi new babe nayi mamaki fa hannun pinky leema taja suka yi waje suna hango motar suka tsaki ihu suka rumgume juna wani Dan saurayine yakaraso yamika musu key car din yatafi ai dasauri suka karasa wajen motar suka bude suka shiga suna duddubawa pinky tashiga ta tada motar leema tace Bestie congrat

Komi is OK murmushi pinky tayi tace thanks dear

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 4

Dunkule hannunshi yayi yana fitar dawani iska me zafi

Daidai lokacin akayi knocking saida yadan dadai sannan yace come in

tsanye yake da bakar suit kansa aduke yace his Excellency yana Neman ka a office yanzu

OK yace sannan Dan Aiken yajuya yafita

Mikewa dasauri yayi sabida ko a wane irin Hali yake ciki yana gaggawan amsa kiran iyayenshi daidaita fuskanshi yayi sannan yafice daga dakin .

Tunda yafito ake gaidashi hannu kawai yake daga musu harya karasa office din mr President .

Knocking yayi daga ciki akace come in a hankali yaburda handle din kofan yashiga da sallama .

Dagowa abban shi yayi yakalle shi hade da amsa sallaman

Jan kujera captain AJ yayi hade dacewa barka da hutawa Abba

Yauwa yace sannan yace al'amin meeting nake so gobe ka Hallara a Dubai daza ayi tare da minister fawaz sabida akwai manyan bakin daza ayi zuwa gobe bazan samu hallara ba .

Dawuri yakamata katafi sabida a invitation card din hudu daidai nacen za a fara meeting din

OK AJ yace sannan yace Allah yakaimu goben lafia

Aameen mr president ya amsa dashi sannan yace

Al'amin ya maganar yar sarkin kano dafatan kun daidai kanku kasan banason adau lokaci baka ajiye iyali ba

Sosa keyanshi AJ yayi a kunyace yace eh mun daidai kanmu idan nadawo daga tafia ma cen zan sauka

Murmushi mr President yasaki irin tasu na manya yace that's my Boi Allah ya albarkaci rayuwar ka

Aameen Aameen mr President

Sannan yace Abba Bari indan leka wajen su Mami

OK mr President yace sannan AJ yabar office din!

Mikewa leema tayi tace bari inbar Ku haka wani mugun kallo pinky ta watsa mata

Minister yace aina zata nan zanbar muku kukwana tunda gida yazama mallakin pinky

Yana yi yana kallonta Dan duk tagama ruda shi sannan yace zuwa gobe inaga flight din 8:00am zamu bi zuwa Dubai idan kuma cen bai maki ba zamu iya chanza wata kasar .

Pinky kwantar da kanta tayi bisa kafadar shi tace babe ai duk inda kazaba daidai ne a wajena

Minister yace hakane daga mai Kai tayi alamar eh sannan tace yanzu dai zamuje Chinese restaurant mudawo

bude baki minister yayi hade dacewa duk abunda kuke bukata akwai anan akwai kuku na musamman leema tace gaskiya honourable kana shagwaba mana pinky dayawa

Wayar shice tayi Kara yakai hannu yadauka saida yagama wayar yakalli pinky

yace mekyau sai zuwa an jima yanzu zanje wani tarone sannan motarki zuwa anjima kadan zata iso ke kuma leema kijira alert zuwa anjima godia leema taringa zuba mai pinky kam thanks kawai tace .

Wayoyinshi ya kwasa yace zamiyi waya sannan yabar parlorn pinky taraka shi da harara saida suka tabbatar ya fita pinky da leema sukayi wani ihu suka rumgume juna pinky ta Dan dafe kirjinta irin najin dadi tace wallahi leema nayi mamaki mutumin nan akwai kayan harka sosai a wajenshi leema tace kadan kika gani indai minister ne

Sai kuma jiran flight zuwa gobe daria pinky tayi sannan tace yanzu dai mufara zagaye gidan mugani wayyo Allah na dadi sai anjima zankira magajiya in bata labari leema tace gaskiya Dan magajia tafi sonki fiye da duk wata mace da take gidan nan

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 6

Leema tace mukoma hotel mudauko kayan mu sai mudawo daga Kai pinky tayi sannan ta tada motar
Yanzu kam ko Dan gyalen karami da take tsawa tana rufe gashinta dashi bata Saba leema ma haka .
Hotel din suka nufa leema ce tafita tadauko musu akwatunan su sannan sukabar hotel din suka koma guesthouse din minister suna parking motar minister nashugowa cikin gidan

Saida suka jira shi yafaka motar shi sannan suka fito washe baki kawai yakeyi ita kuma pinky na tsakar mai wani mayataccen kallo
Suna karasawa tayi hugging dinshi tace thank you babe hannunshi yasa yakara janyota jikinshi yace kin cancanci fiye da haka mekyau sannan yace Mata ina zuwa motarshi Yakoma yadauko wainsu takardu yamika mata yace ga takardun gidan ki hannu tasa ta karba tace wow babe ka gama mun komai thanks
Leema kam sai murmushi takeyi tana taya kawarta murna
Minister yace yakamata in tafi daman sabida alkawarin Dana mikine yasa nadawo sai zuwa gobe idan munhadu a airport zansa driver yazo yayi picking dinki OK tace sannan yashiga motarshi yabar haraban gidan !
Juyawa tayi takalli leema ta kashe Mata ido daya tace bana tunanin intafi Dubai nikadai dole sai dake zare idanuwa leema tayi tace are yhu serious
Daga kai pinky tayi tace yeah m serious Allah dai yakaimu goben sannan suka jera suka koma cikin gidan !
Washe gari 7:00am suka gama shiri pinky tace basai mundauki kaya ba idan munje cen ma tsiya leema tace kina son kashe minister gaskiya
Riga da wando suka tsaka gabaki dayansu wandon pinky harda crazy a ta wajen cinyan gashi wandon yakamata sosai yauma ko gyalen basu saba suka fice .
Har airport driver din minister yakaisu sannan yajuya
Jirgi daban suka hau da minister Dan yana gudun zakin mutane
8:00am jirgin su yatashi zuwa Dubai
AJ tun 9:00am yagama shiri su Mimi kawai yake jira Dan sunma bata mai lokaci
Karfe goma suka shirya suna ganin AJ sukace wow ya kayi kyau uhm kawai yace sannan yayi gaba suka bi bayanshi
Mota biyu sukayi AJ da Sadiq Mimi da sumayya zuwa airport
Dayake private jet zasu hau suna zuwa suka wuce .
7hours 2min yakaisu Dubai agajiye ko wannansu yasauka duk wani namiji daza kagani

idanuwan shi akan pinky yake
Kusan lokaci daya jirginsu yasauka Dana minister
Driver yazo yadauke su zuwa palace downtown hotel Dan daman Achen minister yake sauka two rooms Yakama su pinky suka wuce daya shi yawuce daya
Suna shiga pinky tace wash nagaji fa Bari inyi wanka inyi sallah miyi ordering abunda zamuci.
Suma 7hours 2min yakaisu Dubai suna sauka driver dinsu na nan Dubai yazo yakwashe su
AJ yace palace downtown hotel zaka kaimu OK sir yace
Daki uku Yakama Sumy da Mimi sagir shi kadai AJ ma shi kadai.
yana wanka yashirya ko tsayawa cin abinci bayyiba yawuce wajen meeting din dayake a the H Dubai hotel zaayi meeting din
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 7
Dubai

Saida sukayi wanka sannan sukayi ordering abunda zasu ci
Suna gamawa pinky tace tashi kigani muje mutsiya kayan daza musa leema tace tunda minister yabaki enough Cash ba
Daga gira pinky tayi sannan tace ina tunanin a inda zamuyi shopping dinne
Leema tace kawai muje reel Dubai mall
Dan kinsan wancen karan ma da mukazo munfi tsiyayya achen pinky tace haka nefa .
Fita sukayi daga hotel din taxi suka samu yakaisu har reel Dubai mall
English wears kawai suka kwasa sai cosmetic
Dasu perfumes
Sannan suka koma masaukin su .

Ba AJ yadawo ba sai goman Daren Chen .
Yana shiga dakinshi yarage kayan jikinshi ya fada bathroom
Yawatsa ruwa yana fitowa yayi ordering abunda zayci
Bayan ankawo maine yamaida kofan yarufe
Pinky daga ita sai yar karamar rigar bacci me uban shara shara Dan har pant din jikinta zaka iya hangowa

Kinomo tadaura a saman rigan baccin hade dakara feshe jikinta da turare sannan tazubo da gashin kanta har gadon bayanta leema dake kwance tace cutee yhu murmushi pinky tayi sannan tadauki wayoyinta tace good night .

Leema tace OK fita tayi daga dakin tafara kokarin neman room 205 shikuma minister room 209 yace Mata amman tamanta gabaki daya daidai room 205 ta tsaya tayi knocking

AJ dake cin dinner yayi tsaki yace yanzu haka sagir ne zay dameni

Tashi yayi daga kan kujeran yanufi kofan yabude yace sagir mezan maka n...

Sauran maganan ne yamakale mai a makogaro sakamakon tozali dayayi da yarinyan da kullin sai yatuno ta ran shi yabaci itama kallonshi ta tsaya yi gashi ko riga babu ajikinshi

Saurin juyawa tayi tace I'm so sorry wrong room no

Dan ita ko gane shi batayi ba

Saurin barin wajen tayi

AJ yace hey ko juyawa batayi ba takara gaba text ne yashugo wayanta tana dubawa taga minister ne Yakuma tuna mata room no din

Ganin hey ko juyowa batayi ba yasa shi Jan wani uban tsaki yace I will find yhu young Lady saina gyara maki zama

Maida kofan yayi yarufe abincin ma kasa karasawa yayi sbd takaici

Acikin zuciyanshi yace Toma me tazoyi a Dubai kuma yanda yaganta kaman

Bai karasa ba yaja tsaki yace meye nawa nidai abunda nasani kawai saina gyara mata zama

Dakin minister tawuce bude ma kofan yake tana ko shiga yatashi ya yi hugging dinta .

Pinky nandanan tashiga rikitashi tana fada mai kazaman kalamai wutan dakin takashe tashiga rikita Tsoho .

Washe gari 10:00am tabar wajen minister takoma dakinsu leema dake kwance kan gado tana chat tace tawajen minister sannu dazuwa hmm kawai pinky tace sannan tafada gado baa jimaba bacci ya kwashe ta Dan Daren jia minister bay barta tahuta ba

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 8

AJ sha daya daidai yatashi yayi wanka yashirya cikin kananun kaya sunyi matukar masa kyau ordering breakfast yayi yana ajiye kan telephone din akayi knocking tsaki yaja Dan yasan su Mimi ne mikewa yayi yakarasa yabude kofan sannan yajuya Yakoma yazauna Mimi da sagir da Sumy ne .

Ko wanne su yaci uban kwalliya kaya iri daya da Sumy da Mimi suka tsaka

Tun kafin su zauna sukace ya ina kwana .

Lafia yace Mimi da tafi kowa surutu tace am ya daman safa park muke son zuwa tana gama fadan haka taja bakinta tayi shuru kallonsu yayi yaga ko wannan su yadukar dakai yagane me suke nufi Amma sai yace sai kun dawo

Marairaice fuska sukayi gabaki dayansu sukace please ya muje tare please .

Hannu yadaga musu yace OK naji

Saiku jirani inyi breakfast toh suka amsa dashi sannan Sumy ta dauki remote tachanza channel tasa Bollywood daidai lokacin kuma aka nuna time din da za a nuna raees a cinema ranan Saturday har zasuyi ihu suka tuna da AJ

Sagir a hankali yayi magana yace gashi Friday zamuje kallon noor a cinema kunsan ya dakyar yabari akoma ranan Saturday Mimi tace rokonshi zamuyi harsai ya yarda .

Saida yayi breakfast sannan yakalle su yace sarakan son yawo saiku tashi mutafi

Bayanshi suka bi suka fice daga dakin sagir kuma yakullo dakin sannan yabisu

Car park suka nufa AJ yace sagir Kai zakayi driving danni ba driver dinku bane sannan yawurga mai car key din

Mimi da Sumy baya suka shiga sannan AJ yazauna a wajen me zaman banza

Sagir yaja motar suka bar cikin haraban hotel din !

Mika pinky tayi hade dayin salati sannan tamike zaune leema dake gaban dress mirror tana kallonta tacikin madubi tace wai nikam jia bakiyi bacci bane pinky kallon leema tayi ta harareta sannan tasauko daga kan gadon tashige bathroom Dan taga tabbayar rainin wayo leema tamata tayaya zatayi bacci tunda tsohon banzan ce bai barta ba

Saida takusan minti talatin tana wanka sannan tafito tana goge jikinta da tawul.

Leema tace Dan Allah kishirya dasauri Mudan samu muzaga gari

Banza pinky tamata Dan idan da sabo tasaba da halin pinky

Saida tagama shiryawa tukunna cikin English wears wainda sukayi matukar Mata kyau da amsar jikinta sannan tace muje sarkin takura murmushi leema tayi sannan tace bafa kiyi breakfast ba pinky tace nasani

inda munfita nayi

Saida suka bar cikin hotel din sannan leema tace ina mukayi pinky yamutse fuska tayi tace safa park

Taxi suka samu suka gaya mai inda zasu

su AJ suna zuwa sagir yasamu waje yayi parking Mimi da Sumy suka fito

AJ kam ran shi ne yabaci ganin yanda mutane sukayi yawa shi kam bai fiye yawan son hayaniya ba

sagir ne yace ya AJ muje OK yace sannan yabude murfin Motan yafito

Atare suka jera suka karasa cikin parki din

Hotuna su Mimi suka fara dauka Mimi dagudu tasha gaban AJ tace ya Dan Allah just 1copy please auntie zuli zanma sending

Badan yaso ba ya karkace takashe mai pictures

waje suka samu suka zauna Mimi tace ya aunti zuli tace ka kara kyau yhu luk cutie

Kafin tagama magana har wayan AJ tafara kara yana dubawa yaga wifey akan screen din tashi yayi yabar wajen sannan yayi receiving call din dagacen tace cwt AJ kayi kyau murmushi yasaki yace thanks baby

dagacen tace jia me martaba ya tabbaye ni akan maganar biki

Shuru yayi kaman me tunani sai data kara cewa Cwt bakace komai ba

AJ yace baby daga nan kano zan taho idan nazo sai muyi maganar I love you

Bye baijira cewar taba yakatse wayan

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 10

Saurin karasawa bakin motan sukayi sagir yama motar key AJ yashiga wajen me zaman banza su Mimi ma saurin shiga sukayi Sagir yaja motan sukabar haraban wajen

Suna shiga cikin haraban hotel din tun kafin sukarasa parking space AJ yace drop me here dasauri sagir yaja yatsaya AJ yabude motar yafita a fusace

Su sumayya kallon juna sukayi

Sumayya tace ban taba ganin ya ranshi yabaci haka ba sai yau

Sagir yace nima haka amma ina mamakin sanin juna dasu kayi

Mimi tace amma fa ya bai kyauta ba banji dadin maganar daya fada Mata ba

Hada baki sagir da sumayya sukayi sukace gaskiya bai kyauta ba ai cin fuskane

Mimi tace uhm damuwa tama ban amshi contact dinta ba sumayya tace kedai bari Dan wallahi yau naga wacce tafi auntie zuli kyau

Sagir yace kada kubari yajiku Dan naga tsanar ta a idon shi!

Tsandarewa pinky tayi a wajen zuciyanta nawani tafarfasa saura kiris tafashe da kuka amma saita daure amma zuciyanta har wani tiriri yake mata leema da tagama zazzare idanuwa tace kingani ba abunda nake gaya maki kenan gashi yagaya maki magana yatafi

Murmushin dayafi kuka ciwo pinky tayi tace baici bulus ba wallahi sai yasan yatabo pinky

Dan baa tabani in kyale

Sannan tasuri handbag dinta tayi gaba !

Yana shiga dakinshi bathroom Kai tsaye yawuce ko kayan jikinshi bai cire ba yasakar ma kanshi shower

Bazay fara daukan mataki akan me bakar fuskanba sai yakoma gida Nigeria

Zansa a Kawo mun details akanta tabbas saina shayar da ita bakin cikin da bata taba tunani ba

Tunda batasan darajar Dan adam ba lallai batasan waye captain AJ ba

yauko wajen minister bata jeba sabida zuciyarta ba dadi koda yakira ta cemai tayi kanta naciwo

Ko baccin kirki takasa yi a ranan

A bangaren AJ kam baccin shi yasha Dan shi kadai yasan mezay mata

Washe gari su Mimi suna shiryawa suka wuce dakin AJ

Saida sukayi knocking harso biyu sannan yatashi daga zaunan dayake da koffi a hannunshi yakarasa yabude kofan yace badai tun yanzu kuke son atafi cinema dinba sumayya tace aa daman ya muna son muje shopping ne and pls yhu have too join us

Ganin yana kallon sune sukayi saurin hada baki wajen cewa please......

Alright yace sannan yajuya yace kuje ina zuwa yanzu

Murmushi sukayi sukabar room din
Kananun kaya yasaka sabida daman yariga dayayi wanka blue Jean's sai white riga
Bakaramin kyau yayi ba
Sannan yafesa turaruka masu kamshi yadauki wayoyinshi hade da ATM card dinshi na nan Dubai
Fitowa yayi daga dakin sannan yatafi downstairs yasauka yamika musu key room din sannan yafita
Tsassaye yasame su suna video girgiza kai yayi hade dacewa zanga ranan dazaku girma
Mimi tace ya yanzu fa harda masu kids snap chat sukeyi Kaine dai bakaso
Zaman wajen me zaman banza yabude yashiga yace niba kaman Ku bane sbd kunsan ni busy man ne bayan sun shigane sagir yatada motan sukabar cikin hotel din
Dubai mall sukaje sosai sukayi shopping dakyar sukasa AJ yayi ma zuly tsaraba
Ranan dai sunsha yawo sosai sai yamma gabda za a fara saida ticket nashiga kallon raees sannan suka karasa wajen duk ticket daya 50k haka AJ yacire yabiya suka shiga
Shi kanshi yaji dadin film din duk da shiba maabocin kallo bane yadai fi kwarewa wajen maida hankali a aikinshi
Basu suka dawo ba sai sha daya agajiye suka fito daga motar ko wannan su rike da shopping bag
Pinky tana tsaye ta window tana kallon mutane roban ice cream din data gama Shane tasakoshi kasa AJ kuma daidai zay wuce kenan robar ice cream din yafado mai akai sauran ice cream din dake ciki tuni yabata mai kaya
A fusace yakai hannunshi yayi wurgi da roban ice cream din hade dadaga kanshi yakalli upstairs don yaga wane illiterate dinne yamai wannan aikin
Pinky kam batasan taasar da tayi ba Dan ear peace ne a kunnanta
Tana jin wakar Nicki minaj tanayi tana kada kai tana tafa hannayenta
Idanuwan shine suka sauka akan fuskan pinky a fusace yace this idiot I will kill you
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 9
Dubai
Komawa yayi yazauna sagir yace bari in anso mana abun motsa baki
Harya juya AJ yace yhu knw m full basai ka anso dani ba tunda Ku ciye ciye baya muku wuya shagwabe fuska sukayi atare sukace ya ice cream nefa
Yace nasan ice cream ne ai Ku kenan kuringa shan abunda zay kara maku kiba
Murmushi sagir yayi yabar wajen
Aj yace aure zakuyi and you guys are still young
Amma kullin sai narka uban kiba kukeyi shuru sukayi Dan sudai sunsan jikinsu daidai yake !
sagir bai jima ba yadawo da three cups na ice  cream mika masu yayi sannan yazauna suka fara video ta snapchat

Daidai gate din park din taxi din yafaka suka fito pinky Tamika mai kudinshi suka jera suka shiga cikin park din

Rasa inda zasu zauna sukayi leema ce tahango su Mimi da suke pictures tace thank god ga yan Nigeria cen muje muzauna kusa dasu ko hira mayi

Yamutse fuska pinky tayi tace leema akwai ki dason janyo mutane ajiki wallahi mtsw taja tsaki sannan tabi bayan leema da tuni tayi gaba

Kusan dai atare suka karasa inda su AJ suke

Waje suka samu suka zauna a daya daga cikin kujerun wajen

Suna zama daga Mimi harsu sagir saida suka juya suka kara kallon pinky Dan tamusu kyau sosai

AJ latsa waya kawai yakeyi baima kula dasu ba saida yaji muryan Mimi tana ce musu sannunku sannan yadago da fararen idanuwan shi yakalle su saidai fuskan leema yasamu gani sabida ita pinky gyalen ta yarufe mata fuska girgiza Kai yayi yamaida hankalinshi kan waya Mimi kallon pinky tayi tace hello m Mimi murmushi pinky tasaki Dan sai taji sun kwanta Mata a rai

Cema Mimi tayi m pinky

A razane yadago da fuskanshi yakalleta ita ma lokacin tadago dakanta leema ma tuni tagane shi a tsorace tamike jikinta yadauki rawa

pinky kallonta tayi tace meye haka dakyar ta iya kai bakinta daidai saitin kunnan pinky tace Wanda kikama rashin m ne a hotel

Tsaki taja tace so what kasheni zayyi  dakarfi tayi maganan danya ji mikewa tsaye yayi yanuna da yatsa yace who do yhu think you are itama mikewa tayi tana binshi da harara tace Neman sani kakeyi

Su Mimi kam kallonsu suka tsayayi

Pinky tace daman Kaine nabawa hakuri subhanallah amma nacutar da kaina

sannan tatabe baki tace duk abunda zuciyarka tagayà ma akaina hakane Dan bazan bata bakina wajen baka amsa ba

Murmushin takaici AJ yayi sannan yace ko tantama bazanyi ba ke karuwar kan titice  Dan idan ba karuwa ba babu me irin wanñan banzar shigar Dan inaga rabonki da kai goshinki kasa harkiñ mance yana gama fadan haka yabar wajen a fusace Dan yasan ko bànza ya jagula ma me bakar fuskañ zuciya dasauri su Mimi suka mike suka kalli pinky da ranta yake abace sukace sorry sannan suka bar wajeñ dasauri

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE  11

Su Mimi sun razana sosai da ganin wacce ta wurgo roban ice cream din sunsan koh yau bazaa kwashe lafia ba yanda zuciyar ya take a yanzu !

A fusace yayi cikin hotel din ya haura upstairs su Mimi basuyi gigin binshi ba sabida gudun abunda zaije yadawo

Saida yakarasa upstairs tunaninshi ya tsaya cak ganin baima San room no dinba amma tunaninshi yafi kaiwa a tana room 105 yana zuwa bakin kofan yabuga da karfin tsiya leema dake kwance a firgice ta tashi tana zazzare idanuwa pinky kam bata Masan anayi ba Dan kunnanta toshe yake kara buga kofan akayi a karo nabiyu dirowa leema tayi daga kan gadon a tsorace jikinta duk yadauki rawa wajen pinky takarasa tacire ear peace din daidai lokacin AJ yakuma buga kofan da karfin tsiya zubewa leema tayi akasa jikinta narawa Dan ita kanta pinky ta tsorata amma sabida karfin Hali irin nata tayi wajen kofan zata bude leema tace karki bude bafa musan ko waye ba tsaki pinky taja mtsw batare da tayi magana ba takai hannunta kan handle kofan tabude

Tana budewa gabanta yayi mugun faduwa amma saita dake yana ganinta yakai dogon hannunshi yawanke Mata fuska da mari harso uku iya gigicewa tagama gigicewa Dan tunda take baa taba Marin taba leema tasowa tayi takarasa bakin kofan tana ganin AJ taja dabaya takoma

Pinky rike kuncinta tayi danhar wajen yayi mugun ja bata Ankara ba sai jin hannunshi tayi yajanyota yayi waje da ita baima kula da kayan dasuke jikin taba gajeran wando ne sai yar top da batada hannu janta yakeyi iya karfinshi

Saida sukayi nisa da room dinsu takwace hannunta dakyar tace kai mahaukacin inane dahar kake da daman sanya tafin hannunka a fuskanta kayi kuskuren mari na

Hannunshi ya dunkule da niyan Kai mata nushi kome yatuna sai yafasa murmushin takaici yasaki yace nagode wa Allah daya yini mahaukaci bayyini a karuwa ba sannan a zuciye yakuma damkan hannunta sukayi downstairs sai jaraban yasaketa takeyi amma ko sauraronta bayyi ba saida sukaje har inda roban ice cream din yake yayi wurgi da ita tafadi kasa su Mimi suna nan a tsaye har a lokaci mutane ne suka taru idonshi jajur yakalleta yace kinga waccen robar ice cream da kika wurgo mun da gangan wallahi tallahi sai kinyi dakin sani a rayuwar ki saina koya maki hankali

A tsiwace ta tashi tsaye tana goge hannunta daya Dan goge idonta tuni suka chanza launi batasan sanda hawaye yazubo Mata ba tsanar shi taji har cikin zuciyarta karasawa yayi inda su Mimi suke yace ke sumayya bani ice cream guda daya cikin ledar nan bakinta narawa tace ya me..... tsawa yadaka mata yace common curo kibani jikinta narawa tacuro babbar roba Tamika mai yana ansa yabude yakarasa gaban pinky sannan yace baa taba captain AJ ya kyale

Kallonshi kawai takeyi zuciyarta nawani zugi gashi takasa cewa komai

Akanta yakifa robar ice cream din tuni yan wajen suka dauki ihu murmushi yayi sannan yace sunana captain Alamin junaid yana gama fadan haka yabar wajen

Dasauri su Mimi sukabi bayanshi suna tausayin pinky

Hakuri akafara bata kuka tasaki dagudu tabar wajen tayi cikin hotel din room dinsu tawuce tana zuwa tafada gado tafashe dakuka dasauri leema tarufe kofan tasa key takarasa kan gadon
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 14

Zuly kallon AJ tayi daya maida hankalinshi gaba daya akan wayar hannunshi.
cikin tsiririyar muryarta tace durling kana tare Dani amma gabaki daya hankalinka yana kan waya
Ko yaba kwalliyata daka keyi yau bakayi ba hope dai ba laifi nama mijina ba
Kallonta yayi sannan yasakar Mata murmushi yakamo hannunta yana Dan murzawa kadan yace tayaya wifey zata yi laifi kuma kema kinsan koban fada ba ai kinsan kinyi kyau tunda har su Mimi sun yaba
Shagwabe fuska tayi tace amma Kai baka yaba ba ai and yhu have too
OK OK AJ yace sannan yace wifey kinyi kyau kamar yanzu in daukeki mutafi abj daria sosai tasaki shikuma yana kallonta yana murmushi !
A haka suka karasa katafaran gidan me martaba Dan fadan yanda gidan yake bata bakine ma sabida kyanshi da haduwanshi
Dan yawanci bangaren gidan ginin zamani ne hakan ya tabbatar mun dashi kanshi me martaba Dan zamani ne .
Har parking space suka karasa hade da firfitowa daga cikin motan su Mimi atare sukace Wash mungaji wallahi harara AJ ya zabga musu sannan yace kuma komin gajiyan daku kayi gobe zamu koma
Kallonshi zuly tayi saidai batayi magana ba sabida sanin halin mutumin nata shiyasa take mugun shakkan shi da tsoronshi
Matsawa gabda shi zuly tayi tace zaka shiga Ku gaisa dasu hajia ne yanzu kosai anjima
Girgiza mata kai yayi sannan yace yanzu hutawa nake son inyi su Mimi kam tuni sun shige cikin gida .
OK zuly tace sannan tace akaika dakin saukar bakine girgiza kai yayi
yace no baby zanje hotel inkwana bata fuska tayi wannan karan tace durling baikamata kaje hotel ba tunda nanma duk gidane
Bude gaban mota yayi yazauna sannan yace bazan iya kwana gidan sirikai ba m sorry zandawo an jima tunda akwai abunda yakamata mu tattauna sosai kafin inzo saiki gayama me martaba zuwana
Baijira cewar taba yakalli driver din yace muje
Tsayawa tayi kerere tana kallonshi har suka bar gidan
Tsaki tabuga sannan tayi cikin gida .
Kai tsaye tahir guest palace suka nufa dayake yariga dayayi booking online koda yaje key room din kawai aka bashi !
A gurguje pinky take shiri leema takalleta tace law ba wasa bane naga dukkin sukurkurce ne tsaki pinky taja tace bana son inyi missing test din yau wlhi tunda nayi missing guda uku kuma kinsan yanda nadauki karatun nan da muhimmanci
tana gama maganar tasuri car key dinta dasauri tafice leema ma tabi bayanta dakanta tayi driving dinsu a sabuwar motar nata har zuwa uniabj
Tun daga bakin gate student suke kallon motar dayake akwai tic basu gane ko waye aciki ba tana parking tayi saurin fitowa rike da hang bag dinta takulle motar tuni kallo yadawo kanta atare suka jera itada leema suka wuce danko kallon mutanan wajen basuyi ba
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

PAGE 13

Murmushi tasakar musu hade dabude Dan karamin bakin nata tace ah bakomai yawuce ai Karku damu

Sosai pinky ta birge su yanda tanuna musu bakomai bane abunda AJ yamata .

Leema ce tace da alama dai kaman ku yaran Mr President ne idan banyi kuskure ba

Murmushi suka tsaki a tare hade dakallon juna sukace yeah hakane nanfa suka fara hira saidai basosai pinky take samusu baki ba daga baya kuma sukaje sukayi breakfast .

Anan suka bata lokaci har zuwa 3:50pm sannan pinky tamike tsaye taduba agogon dake hannunta kamfanin Rolex tace leema time fa yana tafia kuma kinsan flight din karfe biyar zamu bi dasauri leema tamike su sumy suka bisu dakallo pinky tadan kallesu tayi murmushi tace bye bata jira cewar suba tabar wajen leema kam saida sukayi musanyan lamba dasu Mimi sannan tabi bayan pinky dasauri!

Koda suka koma room dinsu wanka pinky tashiga bata jimaba tafito leema ma tashiga doguwar riga pinky tasaka amma me haannun vest cream color tadaure gashin kanta tayi sannan tayafa wani Dan karamin gyale dako gashin kanta baigama rufewaa ba

Handbag dinta ma cream color ne sai takalmin kafanta ma haka

Leema ma doguwaar rigar tasaka suna gama shiri suka kira aka daukan musu akwatunsu suka fice taxi suka samu har airport .

Koda suka isa hudu dawani abu zama sukayi a kujeru Suna Dan taba hira har aka fara kiransu biyar daidai jirginsu yatashi zuwa tsararin samaniya!

7hours 23min yakaisu kasa Nigeria driver din minister ne yazo daukansu basu zarce ko inaba sai gidan da minister ya mallakawa pinky

Suna shiga cikin parlour suka rike baki Dan sunyi mamakin sauyawan gidan gaba daya achanza komi ansa sabo komi pink and white a tare sukace wow pinky tace minister na neman kasheni irin wannan Bari dakudi haka murmushi leema tayi tace indai minister ne bakiga komaiba

Saida suka bi suka zagaye dakunan suma komi anchanza dakin dayafi ko wanne girma pinky tadauka leema kuma nacen wajen karamin parlour tadauka saida sukayi wanka sukaci abinci sannan sukayi sallah!

Washe gari private jet su AJ suka hau zuwa Nigeria baa ajiye su ako inaba sai a kano!

Dayake zuly tasan da dawowansu

Suna sauka suka hangota murmushi suka tsaki AJ yahade fuska

Doguwar abaya ne sanye ajikinta black color sannan ta Nada red veil abunka da farar mace kada kuso kuga yanda tayi kyau kuma abayan yazauna mata sosai sai kace irin larabawan Kuwait dinnan

Takalmin kafan tama red color ne me matukar tsini da tsawo doguwa ce amma basosai dinnaan ba tana da dogon hanci sai kananun idanuwanta saidai ba kananu sosai ba

Karasawa wajensu tayi tana murmushi cikin tsiririyar muryarta dagaida AJ tsakin fuska yayi kadan sannan ya amsa gaisuwan su Mimi sukace auntie zuly kinyi kyau murmushi tasaki hade

dariko hannunsu sukayi gaba AJ yamara masu baya shida zuly suka shiga gidan baya driver yajasu sukabar wajen sannan su Mimi suka shiga daya sai mota biyu dasuka bisu abaya
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 12

A hankali leema tace pinky kiyi shuru please

A fusace pinky takalle ta tace leema just lyv me alone pls

Girgiza kai leema tayi tace pinky yhu have to stay away frm dat guy wata rana zay iya maki abunda baki taba sammani ba pls

Kallonta pinky tayi ta galla Mata wani uwar harara sannan tace hm leema haryau bakisan zuciya taba ko

Toma shi waye dahar kike tsoron sa wlhi koshi waye sai namai mafiyin abunda yamun har yànà kirana da karuwa yeah I know ni karuwa ce

Kuma karuwar da tafi ko wace karuwa iya karuwanci

Lallai saina nuna mai nidin karuwace amma me lasisi !

Shuru leema tayi Dan tariga data sani AJ yawuce da sanin pinky shidin ba kasafai yake yafiya ba Dan tasan labarinshi sosai

Tashi pinky tayi tashiga bathroom tasakar ma kanta shower

Shikam tuni zuciyarshi tayi fes ganin yasa me bakar fuskan kuka yau murmushi kawai yake ta tsaki shi kadai

Dan har saida yakira Zuly sukasha soyayya !

Bayan fitowanta wanka kayan bacci tasaka sannan tadaura kinomo akai tafesa turaruka Dan tuntuni minister yake kiranta

Ko saida safe bata ma leema ba tawuce Dan leeman ma haushi take bata

Duk da ranta babu dadi haka ta zage ta nuna ma minister soyayya Dan zuwa gobe take son barin kasar sabida duk ya isheta !

Washe gari da farin ciki sosai ta tashi sabida yarda da uzurinta da minister yayi sannan yamata transferring 1.5 million a acct dinta sannan yamusu booking jirgin karfe 5:00pm

Godia tamai sannan tabar room dinshi tawuce nasu tana shiga ta rumgume leema tana murna tace minister yawuce da tunanina kinsan 1.5million yatura mun zuwa acct dina leema ma ihu tayi tace amma gsky naji maki dadi thanks pinky tace sannan tafara cire night gown din dake jikinta tace yaufa zamu tafi Dan flight din yamma zamubi saimu fara shiri

Leema tace bangane ba daga gira pinky tayi tace nariga nagama magana da minister m living today bazan iya kara kwana a garin nanba .

Daga ita sai pant da bra tashige bathroom cikin jacuzzi tashiga Dan tariga tasaka sabulai masu kamshin gaske

Saida takusan Kai hour daya sannan tafito daure da towel

Saiko zuba kamshi takeyi

Leema ce tajuyo tace  yanzu nagama waya da yan skool wai lectures yafara kankama fa pinky tace  nasani yanzu dai zandan je pool indawo or yhu wanna join me leema tace yeah. Shiryawa pinky tayi  cikin wata yellow gown daya saya Mata iya gwuwa babu abunda tadauka slifas kawai tazira takalli leema tace muje leema ma daga ita sai yar gown suka fice kai ba ko Dan gyale .

Suna tafe suna hira jefi jefi har suka karasa bayan hotel din inda nanne swimming pool din yake mutane ne da dama kuma kala Kala murmushi pinky tayi ganin wainsu suna rawa

Waje suka samu  suka zauna pinky tace  jikina har suma yakeyi fa kinsan ni da rawa daria leema tayi tace kiyi joined dinsu mana

Girgiza kai pinky tayi !

Daidai lokacin su Mimi sukazo leema ce kawai tagansu amma AJ  bai tare dasu

Karasowa su Mimi sukayi inda su pinky suke  zama sukayi leema ce tadan taba  pinky da hankalinta gaba daya yana wajen masu rawan nan a hankali tajuyo takalle su tasakar musu murmushi

Su Kansu su Mimi sunyi mamaki hakuri suka fara bata akan abunda AJ yamata

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE  16

Washe gari waya AJ yama su sagir yace su same shi a airport

10:00am suka  karasa airport din   .

Dayake private jet ne suna zuwa jirginsu yatashi

kafin 12 harsun Isa villa ganin motoci dayawqa shiya tabbatar musu da har yanzu bakin Mr president suna nan danko part din Mami basu Jeba Dan sunsan matan gomnoni suna cen kowa sashin shi yawuce

Aj saida yayi wanka yaci lunch sannan yadauki wayarshi yakira daya daga cikin yaranshi

Ko minti biyar baayiba ya iso yana shiga parlorn yasara mai hade dacewa sir wajen zama AJ yanuna mai daga cikin lunsuma lunsuman kujerun parlorn

Bayan yazauna ne AJ yace jafar aiki nakeson kamun daga zuwa gobe nakeson ka samo mun information akan wata yarinyan pinky

Komi da komi nakeson Sani akanta understand yes Sir AJ yace sannan AJ yace mai zaka iya tafia .

Pinky tunda sassafe tashirya danyau suleja zata ganin magajia

Tagama shiryawa kenan leema tashugo dakin tace kefa nake jira juyowa pinky tayi tace nagama ai muje key car dinta tadauka sai handbag dinta sannan tabi bayan leema suka fice har wajen parking space

Driver side pinky tashiga sannan leema tashiga wajen me zaman banza pinky taja motar sukabar haraban cikin gidan kai tsaye hanyan suleja suka dauka

Lokaci kankani yakaisu har kofan gidan magajia
Bin Matan wajen pinky da leema sukayi da kallo sannan suka fito daga cikin motan suka yi cikin gidan matane kala kala birjik acikin gidan saidai babu Wanda sukama magana har suka karasa dakin da magajia take tana ganinsu tasaki murmushi tace beauty murmushi pinky tayi sannan takarasa tazauna akusa da ita saida suka gaisa pinky tace mama munzo mutafi dake nefa Dan kinsan yanzu na mallaki gidan kaina sannan ayau idan munkarasa gida ki taimakeni kigaya mun ta yanda akayi kika tsinceni
Fans kumun hakuri wayata wallahi hukkin takeyi Amma zaku jini zuwa anjima insha Allah
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 15

saida yayi wanka yahuta sannan yayi ordering abinda zayci yana gamawa yakira driver .
Fita daga cikin hotel din yayi yakarasa parking space dasauri driver din yasauko zay bude mai bayan mota AJ yace jeka kawai nagode .
Dasauri driver yakoma wajen mazaunin driver AJ yabude wajen me zaman banza yashiga yazauna hade da janyo kofan

Kai tsaye gidan me martaba suka nufa tun kafin sukarasa cikin gidan yakira zuly yace tamai iso wajensu hajia
Jikinta har rawa yakeyi takarasa bangaren hajia
A dakin hajia ta tadda kannan ta dasu Mimi suna taya hajia hira karasawa tayi inda hajia take tace hajia yanzu Alamin zay shugo murmushi hajia tasaki tace yar nema shiyasa naga sai faraa kikeyi murmushi zuly tasaki ta dukar da kanta Dan akwaita da kunya tashi tayi tabar dakin Farida tace Dan Allah auntie zuly idan ya AJ yashugo kigaya mun juyowa Zuly tayi ta harareta tace iyakarku gaisuwa Dan hira zamuyi tana gama fadan haka tayi saurin barin dakin
Nata dakin ta tafi cikin sauri tasanya hadaddiyar wata abaya baka me manya manyan dutsuna agaban rigan sai hannayen kuma irin wainsu dutsuna ne kanana masu kyalli sannan ta Nada veil din abayan tazira flat shoe sliver colour saii wayarta iPhone 7 golden colour sannan tafeshe jikinta da turare daidai lokacin wayarta tayi ruri
murmushi tasaki sannan tayi picking call din dagacen AJ yace ina waje OK sir tace sannan yakatse wayan saurin barin dakin nata tayi tafice a natse take tafia harta karasa inda AJ yake murmushi suka tsakarwa juna AJ yace wow my wifey looking beautiful
murmushi tasaki tace thanks durling sannan tace mukarasa daga ciki atare suka jera zuwa cikin parlourn babu laifi sun danyi kyau atare amma basu wani dace sosai ba saida sukayi tafia me Dan nisa sannan suka Isa katafaran parlorn nikaina nakasa ganin karshen parlourn hajia ce dasu Farida saisu Mimi har cikin parlourn suka karasa AJ yazukunna har kasa yagaida hajia

cike da ladabi da faraarta ta amsa sannan ta tabbayesu su Mami Farida dake gefe tace Haba ya AJ my crush ko tunawa da yar kanwarka bakayi ba hararar wasa yasakar mata yace ina gudun surutun kine Farida bata fuska tayi tace ya kenan nazama parrot daria su Mimi sukayi AJ yace Nina isa sorry crush

Zuly tace abba fa yana jiran ka mikewa yayi sannan yamasu hajia sallama Farida dasu Sumy sukace ya gayan rakiya kun samu Zuly ce tajuyo tace hajia gaskiya kice suyi zaman su hajia murmushi tayi tace baruwana kunfi kusa .

Dayake yabar fada sashin shi sukaje suka sameshi suka gaisa daga nan sukayi parlour su Farida suka koma sashin hajia!

Suna zama aka fara shugowa da kayan motsa baki ruwa kawai yasha sannan yafuskanci Zuly yace zulaiha akan maganar danace sai nazo zamuyine nima abba yadameni sosai akan zancen toh inaga next week zaa Kawo kayan nagani ina so hade da kayan Sa Rana hope hakan yamiki murmushi tasaki tace hakan ma yayi sbd Batada burin daya wuce taga ta mallaki AJ

Hira sosai sukasha bai tafi ba sai goma dawani abu nadare sannan yakoma hotel

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 17

dogon ajiyar zuciya magajia tasaki hade dacewa Allah yakaimu Aameen suka amsa dashi gaba daya sannan leema tace mama tashi mutafi kinsan fa bamuson dadaiwa acikin gidan tashi magajia tayi da kyaar sabida tafara manyanta sosai Dan a kalla zata Kai shekara hamsin da yan kai

Kaya tafara hadawa pinky tayi saurin cewa aa mama basaima kindauki komaiba murmushi magajia tasaki sannan tace dole indauki wani Abu sabida yanada matukar muhimmanci wata jakar kaya tabude tadauko wani kullin kaya sannan tayafa gyalenta tace masu pinky muje leema ce ta amsa kullin kaya sannan suka fice daga dakin

Babu Wanda suka kula har suka fice daga cikin gidan

Pinky dakanta tabudewa magajia kofan baya tashiga tazauna sannan suma suka shiga picky taja motar sukabar unguw yaukam daga ita har magajia sunyi bakwaana da suleja

Lokaci kadan yakaisu cikin garin abuja saida pinky tasaya tayi shopping sannan suka wuce gida.

Sai da magajia tahuta taci abinci sannan takalli pinky tace .

1991/22/August

Rana ce da bazan taba mancewa ba Dan a lokacin inada kuruciya sosai sannan sosai ake ribibi akaina

A ranan nadawo daga wajen Alh Tanimu ina sauka a mashin nafara jin kukan jariri nama Zata acikin abokan harkane wata tahaihu saidai ina dosan kofar gida naci karo dawani kwali kuma naci gaba dajin kukan jaririn saida na nutsu sannan na tabbatar da acikin kwalin nanfa nakejin kukan dasauri nazukunna nabude kwalin naci karo da jaririya cikin kayan alfarma Dan

daga ganin kayan masu sadane sannan sai kunnanki dankunnan diamond ne ganin kina kuka yasani kai hannuna dasauri nadaukeki nafara jijjigaki sannan nakara duba kwalin ko akwai wani Abu amma bakomai hakan yasa nawurga kwallin cikin kwata .
Tun daga ranan nafara rainonki saidai a dalilinki Ko wane saurayi yadaina zuwa wajena nikam hakan bai dame niba tunda nasameki sbd tuni nadade dajuya mahaifata
Dakudin Dana samu abaya dashi nake biya maki kudin makaranta sabida bana so kifara harkar danayi .
tana kainan takalli pinky dake hawaye tace saidai nayi bakin ciki da fadawanki wannan harka kuka picky takeyi sosai cikin muryan kuka tace mama harkan nan ita kadai tafi dacewa dani tunda itama wance tahaifeni ta wannan harkan tasameni tunda harta iya ta yarda ni a titi
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 18
pinky tace mama koda ayau zanhadu da iyayena na asali bazan taba yanda dasu ba kece kadai uwata kuma ubana Dan inada tabbacin iyayena basu sona tunda har suka iya yanda ni hawaye magajia tashare pinky tace wannan yazama sirri a tsakaninmu kece mahaifiya ta mama ke Kadai tana gama fadan haka ta tashi dagudu tawuce upstairs tana kuka leema ma kukan takeyi dan tafara tunawa da rayuwar ta itama .
tashi leema tayi tace mama muje inuna maki dakinki Dan kinsan kedin yar gatar pinky ce komi tasa maki a dakin .
Daren ranan ko hirar dasu keyi basuyiba sbd zuciyoyinsu ba dadi !
sai zuwa bayan isha sannan baki suka tafi hakan yabawa su AJ daman zuwa bangaren Mami achen ma suka tadda Mr President waje suka samu suka zauna suka gaidasu AJ yace Abba munyi magana da zulaiha yanayi yana Sosa keya Mr President yace dazu munyi waya da shi me martaba Mami tace gwanda ma kayi auren ka tattara ka koma cen gidanka kabar kannanka su tsake ache shi kullin mutum bakin rai Mr President yace so kike yayita wage baki kannan nashi su raina shi
Daga Kai AJ yayi yace yauwa abba gaya mata wurga mai jarbin hannunta Mami tayi dasauri yatashi yace da alama dai Abba ne kadai keyi dani good night yana gama fadan haka yafice yana murmushi .
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 19
washe gari karfe goma jafar ya isa bangaren AJ saida yayi knocking wajen so biyar sannan AJ ya yaye katon blanket din daya rufa dashi yakarasa yabude kofan sannan yajuya Yakoma kan

gado jafar Sara mai yayi daga kai kawai AJ yayi sannan jafar yace sir ansamo information akan yarinyan

Daga Kai AJ yayi alaman yana jinshi sannan jafar yaci gaba yace pinky ba boyayyiya bace Dan duk inda kaje sai kaji Ana hiranta tana maitama guest house din minister danya mallaka mata gidan a dai yanda naji zaman kanta takeyi sannan tana karatu anan gwagwalada wani murmushi AJ yasaki danni kaina bansan maanar murmushin ba

kallonshi yayi Weldon zakaji alert ynxu sbd naji dadin aikin ka godia jafar yayi sannan yakara Sara mai yabar dakin .

Yanzu tunanin irin muguntan dazay mata yafarayi tashi yayi yashiga bathroom danko baccin bazay iya komawa ba

Yana fitowa yashirya cikin blue din suit bakaramin kyau yayi ba Dan akwai taron da aka gayyace shi a gwagwalaada bakaramin kyau yayi ba Dan side box dinnan nashi sosai yake kara mai kyau saida yagama shiryawa yawuce dining yayi breakfast sannan yawuce part dinsu Mami

A dining ya taddasu suna breakfast Jan kujera yayi yazauna sannan yagaida iyayen nashi sannan su Mimi suma suka gaidashi duk da yau sunga sai faraa yakeyi

Mami ce takalleshi tace alamin kayi breakfast kuwa

Rike ciki yayi yace Mami nayi breakfast Dan cikina ji nake kaman zay fashe Sumy tace Kai ya sai kace mace harara ya zabga mata yace an gaya maku ni irin kune me uban cin abinci Mami tace kai kenan fada Abba yace dole yayi fada tunda su bakinsu bai shuru mikewa AJ yayi yace wlhi kushirya on Friday Ku koma skool Mami tace Ko baka ceba Dan before Friday ma zasu koma

OK yace sannan yace abba natafi taron da aka gayyaceni saina dawo gabaki dayansu suka mai adawo lafia sannan yafita .

Mota daya yashiga shi kadai sai driver sannan sai motoci biyu agaba biyu abaya.

Kai tsaye uniabj suka nufa

pinky tace yau bakida test ne leema dake kwance a parlor tace yeap pinky tace OK saina dawo mama sannan tafita yau dayar motar ta tadauka BMW shima black color kuma yasha bakin tic

wangale mata gate din me gadi yayi tabar haraban cikin gidan

Wakar Beyonce tasaka tadan kure volume tana driving tana bin wakan har takarasa cikin skull .

daidai inda taga manyan motocin nan daidai wajen tayi parking sannan tafito daga cikin motan tayi hanyan department dinsu

Allah yasa yau test dayama gareta

taro akayi akan cigaban makarantan dadai sauransu atake a wajen yamusu transfer din 7.5million godia suka fara mai sosai

Sha biyu suka baro dakin taron kuma a wannan lokacin pinky takaraso wajen da tayi parking tana kada key car din hannunta .

Key car dinne yasubuce yafada kan motar su AJ shikuma lokacin idonshi yasauka akan fuskan pinky

dasauri security suka karasa ganin tayi banna amma ko a jikinta saima karasawa da tayi tadauki key car tayi wajen motar ta

AJ kam yagama kuluwa lallai yanzu zay gyara mata zama cikin Isa da takama yakarasa inda take yace hello a hankali tajuyo takalleshi bataako Ankara ba saijin yatsun shi tayi akan fuskanta harso biyu sannan yanunata da yatsa yace r you illiterate kobakiga abunda kikayi bane harararshi tayi sannan a fusace tace banganiba ko angaya maka Dan kawai nayi kuskuren goge akwalar motar naka zaka Kai kazamin yatsun ka kan fatar fuskata toh wlhi bashi kaci sai kaga abunda zanmaka AJ da zuciyar shi ke kuna yace good kafin kedau mataaki ni yanzun nan zandau mataki baijira cewar taba yakalli securitys din yace kubani karfe babba kuma nakeso dasauri suka dauko suka mika mai pinky na tsaye tana jiran taga abunda zay aikata aiko bata Ankara ba sai gani tayi yatarwasa mata glass din bayan mota idanuwa taware tana kallonshi saida yafasa dika glass din bayan motan sannan yayi wurgi da karfen yakalleta yace ina jiran sammaci

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 20

baima jira jin meza tace ba security suka bude mai bayan mota yashiga yazauna suka maida kofan suka rufe sannan driver yaja motar sukabar cikin makarantan .

Ko kallon mutanan wajen batayi ba tashige cikin motan ta a fusace ta tada motan tabar haraban makarantan dagudu saida tayi nisa da skool din sannan tayi parking abakin hanya takifa kanta akan sitiyarin tafashe dakuka tace I hate you illiterate i hate you sannan takuma fashewa dawani kukan saida tayi me isan ta sannan ta tada motan tabar wajen .

Saidai har takai gida tana tunowa da marinta da AJ yayi mata agaban jamaa sannan ya wulakanta ta hawaye kawai taji yana zubo mata ahaka takarasa gida tana parking tafito danko handbag din ta takasa dauka a parlor ta taddasu mama da leema batare data musu magana ba tawuce upstairs mama tace maza tashi kibita Dan naga idonta ya kumbura kinsan kuma ban iya hawa sama dasauri leema tabi bayan pinky .

Tana shiga tafada kan gado tafashe dawani sabon kuka leema takarasa dasauri kan gadon tace pinky meya sameki meya faru

Shuru pinky tayi taci gaba da kukanta Dan a halin da take a yanzu bazata iya magana ba ganin hakane yasa leema ta kyaleta harta gama kukanta sannan tace pinky kigaya mun abunda yafaru dakyar pinky ta iya dago idanuwanta takàlletàa tace leema kinji na rantse miki ko wàllahi tallahi bashi yadaukar wa kansa Dole saina rama abunda yamun tunda tafara magana tasan da wanda pinky takeyi amma sai tace wai waye cikin muryan kuka pinky tace wanene kuwa banda yawuce wancen mahaukacin AJ din leema ta rafka salati tace meya maki Marin daya mata tanuna mata sannan tace yakuma fasa mun glass din mota yawulakantani abainin jamaa wlhi baici bulus ba .

Good night sai kunjini zuwa gobe insha Allah

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

AJ yace babu wahalan dazan bata matan ne sai a hankali daria Faisal yayi yace itama zuly dandai karsu Mami su dame kane amma ba kalar macen da kakeso bane tunda kadadai kana fada mun kafi son ka aura mace me kyau wacce tafika kyau ko kuma kuzo daidai amma Zuly ko kafanka bata kawoba wajen kyau .

Tsaki AJ yasaki yace kaji ka dawani magana nibari intashi inyi gaba

Dan na biye maka saika bata mun mood dina girgiza kai Faisal yayi yana murmushi sannan suka mike suka fice AJ yace kai kadai kaman maye sai yaushe su mummy zasu dawone Faisal yace ina tunanin cikin week dinnan sudawo AJ yace gwanda ma kadage Kayi aure Dan naga zaman kadaicin zay dameka Faisal yace sai kafara aure zanyi duk da kaidin jarumi ne da alama saika auri mace fiye da daya bata rai AJ yayi yace Allah ya kyauta ai zuly ta isheni .

Bayan mota aka bude mai yashiga yazauna faisal yace kagaida su Mami inaga inshigo zuwa gobe OK AJ yace sannan aka wangale musu gate din suka bar haraban cikin gidan.

Cikin yan kwanakin nan gaba daya pinky da leema basa zama sabida bikin wata kawarsu daza ayi .

Daidai gate din gidan faiza tafaka motan sannan tadauki wayarta takira bugu daya aka dauka tace pinky fito ki amshi kayan Dan sauri nakeyi mum najira na agida

Pinky daga cen tace ganinan fitowa

Tashi tayi daga kan kujeran da take kwance tace ma mama magajia tana zuwa daga ita sai yar gown tafita takarasa inda motar faiza take tace amarya murmushi faiza tasaki tace daga wajen tailor nake hannunta Tamika baya tadauko wata katuwar Leda Tamika ma pinky tace Dan Allah Frnd kizo gobe kikuma zo dashiri Dan kinsan gobe za a Fara event

Pinky tace naji sai minyi waya kigaida mum .

Sannan tajuya takoma cikin gida.

a Daren ranan taje saloon aka gyara mata Kai aka mata design ba ita takoma gidaba sai sha daya .

Washe gari hudu na yamma faiza ta dameta dakira doguwar riga na material tasaka sannan tayafara Dan karamin veil akanta sai karamar akwatin da tasa kayanta sannan handbag dinta tare suka tafi da leema .

Kai tsaye asokoro suka nufa tun daga bakin gate din gidan mutum zaysan gidan babban attajiri ne har cikin gidan suka shiga da mota suka yi parking sannan suka fito hanyan shiga parlour suka nufa har daki suka Shiga suka gaida mum din faiza sannan suka wuce part din faizan .

suna shiga faiza tace wlhi fushi nake dake tun dazu yakamata kizo gashi har frnds din nasir sunzo sun tafi kuma kinsan kece gaba gaba akomai

Hade hannayenta pinky tayi waje daya tace afuwan amaryar nasir bagani nazo ba.

. hararar wasa faiza tawasa mata tace 7:00 zasu dawo daukan mu no African time Dan nasan

Hali tabe baki pinky tayi tace kema kinsan nikaina nasani African time .
Wardrobe faiza tabude tacuro wainsu hadaddun materials Tamika ma pinky tace naki daya na leema daya nakine me pink flower
Daidai lokacin ferry meyin makeup tashugo tace bride are you ready murmushi faiza tayi tace yeah m ready.
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 21
Leema tace rabuwa dashi shi zay fiye maki zama alkhairi sabida duk wani hukunci dazaki dauka akan AJ wlhi abanza Dan zay maki mafiyin shine kiyi hakuri kawai ki kyaleshi .
Wata uwar harara pinky tama leema sannan tace tashi kitafi kawai ina bukatan zama nikadai tana gama fadan haka takuma kifa kanta akan gadon taci gaba da hawaye.
Leema kam tashi tayi tafita Dan tasan dakyar pinky tadau shawarar ta koda tasauka downstairs gayama mama magajia komi tayi hade dacewa mama kifa mata magana inba hakaba babu abunda AJ bazay iya mata ba.
A bangaren AJ kam kai tsaye gidan aminin shi yanufa shima anan maitama yake .
Har cikin gida suka shiga sannan yasauko daga mota yayi sashin Faisal
Handle din kofan yarike yabude kofan sannan yashiga Faisal yana ganinshi yamike yace irin wannan zuwan bazata haka captain murmushi AJ yayi hade dafadawa kan lallausar kujerar .
Faisal yace da alama dai yau kana cikin farin ciki meye sirrin AJ yace nothing kawai ina cikin farin cikin ne yau Faisal shidai bai yanda ba Dan iya saninshi da AJ ba kasafai yake murmushi ba sai yayi mugunta .
Amma saiya share kawai yakalleshi yace sai Hutu kakesha abunka Shafa kanshi AJ yayi
yace kuma wlhi hutunma ya isheni sbd ko yanzu din bana hutawa sbd yawanci Abba idan angayyace shi wani taro ni yake turawa
Murmushi Faisal yayi yace ina gadai nan gaba siyasa zaka koma mawa dasauri AJ yace Kai ina ai bana shaawan yin siyasa yanzu dai dazu nasir yaturo mun da invitation card na bikinshi hope kaima zaka Dan kasan bana son zuwa biiki bikin nan Dan kawai nasir ma Nada mutunci a ido nane shiyasa zanje
Faisal yace gaskiya dole kaje blue shadda ne zaasa ranan dinner da red hula
AJ yace OK nafara ma tunanin kiran zuly tazo tarakani sbd tsaro
Daria Faisal yayi yace wahala dai kawai kakeson bata
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 23

Zama pinky tayi akan stool ferry tabude katon makeup kik dinta tafara sansarawa amarya kwalliya tun Ana Mata pinky tafara daukanta pictures ana gama Mata faiza tace saura ke pinky

Zuwa tayi tazauna ferry tafara mata kwalliyan tun Ana mata su leema suka Fara zuzuta kyaun da tayi sai Takara kyau ga purple gown din da tasa Ana gama mata aka Nada mata head duk da an nade gashin kanta sai daya tabo wuyanta faiza tace wow gaskiya ferry pinky tafini kyau daria sukayi cikin hadin baki sukace waya gaya maki anafin amarya kyau .

Leema ma anmata makeup din zama sukayi ferry tadaukesu hoto .

7:00pm daidai frnds din groom suka fara zuwa saida aka kwashe mutane dika sannan bride and groom saisu pinky sai wainsu frnds din groom su kadai suka rage motar couples dinne asakiya haka suka karasa har cikin

Ralmeton hotel wow abunda nace kenan da naga saruwan wajen

Komi purple and white ne amaryan ma shigan purple tayi shikuma ango white shadda sai hula me rantsi rantsin purple ajiki frnds din ango kuma ash shadda sai hula me ratsi ratsin purple .

Tun daga bakin gate zaka fara jin tashin kida a tsakiya sukasa couples din har suka karasa cikin katafaran hall din wajen zaman bride n groom suka karasa suka zauna sannan kowa yasamu gu yazauna

Faisal ne yabude taron da addua sannan yakoma wajen zamanshi yadauki wayarshi yakafa a kunne yace AJ kana inane dagacen AJ yace ynxu zanshugo .

MC ne yafara gabatar da taron sannan yabukaci babban aminin ango yafito yafada tarihin ango .

Takardan dake hannunshi Mc yakalla sannan yace captain Alamin junaid tuni wajen yadauki tafi shikuma daidai lokacin yashugo da irin shigar da sauran frnds sukayi

Zan iya cewa kayan sunfi yima AJ kyau tuni matan wajen suka tsare shi da idanuwa Dan guntun tsaki yaja sannan cikin takama yakarasa ya amshi MA kel phone a hankali yafara jawabi Yakuma fada yanda masoyan suke son junansu pinky tunda takalle shi so daya tadukar da kanta taci gaba da latse latsen waya .

Bayan yagamane yakoma kusa da Faisal yazauna sannan Mc yace yanzu Zamu kira babbar kawar amarya tazo tafada mana tarihi akanta

Paper din hannunshi yakara dubawa sannan yace pinkylecious

AJ dake zaune yace pinky

A yagance ta tashi daga kujerar tafara tafia duk Wanda yake wajen saida yakalleta banda mutum daya da yaketa tsaki shi kadai

Cikin tsiririyar muryarta tafara magana tagabatar da dangantarkar ta da amarya dakuma irin shakuwar da sukayi sannan tafada yanda lovers din suke matukar son juna daga karshe tamusu fatan alkahri hade dabarin wajen raf raf kawai kakeji awajen .

Waka aka tsaki sannan couples sukaje suka yanka cake daga nan kuma DJ yasaki sauti kada kuso kuga yanda abokanan ango da kawayen amarya suke cashewa pinky saida ta daidaici hankalin AJ yana wani wajen ta tashi daga inda take takarasa wajenshi kaman zata fita lemun dake kan table din a bude ne tasaya hannunta tadan tureshi sannan tabar wajen

Sanyi yafara ji ajikinshi dubawan dazayyi yaga bakin cocacola ajikin wandoshi dakuma rigar shi dasauri yamike tsaye pinky dake gefe tana kallonshi hotuna tafara mishi tana daria kasa kasa.

Takaicine ya isheshi dasauri yabar hall din daria tafashe dashi sannan takarasa itama tafara cashewa .
Dan tuni ta tayi searching dinshi a instagram ta tura mai pictures din hade da rubuta gifts harda Dan heart ta tura mai dakuma abun daria sannan ta rubuta pinky
Dayake data dinshi a bude yake yana fita yaji shugowan text wayar yadanna sannan yashiga instagram din bude DM din yayi da hotunan shi yafara cin karo rufe idonshi yayi zuciyar shi nakuna yace wane childish dinne yamun haka kasa yayi da hotunan yaga ansa pinky baisan sanda yayi wurgi da wayar ba yakoma cikin hall din afusace
Pinky kam tuni tayi cikin motar ta tasa key
Dubata yafarayi ganin bai ganta bane yasashi karasawa wajensu faiza nasir yace AJ meya bata ma kaya haka tsaki yaja yace ina pinky faiza tace tana nan kaduba ta tsaki yaja yace wlhi sai na daureta inga urban da ya tsaya mata Faisal ne yakaraso yace meke faruwa su nasir sukace pinky wai yake nema da alama matsala suka samu leema dake gefe dasauri tabar wajen tafita pinky tana ganinta tabude mata tace shugo mutafi leema nashiga pinky taja motar sukabar wajen saida sukayi nisa tafashe da daria Dan harda hawaye
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 24
Wayarta tadauko Tamika ma leema tace duba mun kigani kaman yafashe dakuka .
Daria takuma fashewa dashi leema tace pinky kinsanko wannan Karan babban mataki zay dauka akanki Dan cewa yayi saiya daureki dogon tsaki pinky tasaki mtsw tace mafashi Dan rainin hankali kawai harya isa yakulleni mtsw takuma Jan tsaki daidai lokacin wayarta tayi ringing sunan faiza tagani pinky tace leema answer kisa mun a loudspeaker yanda tace haka leema tamata dagacen faiza tace pinky kina inane pinky tace I'm so sorry kawa wani aiki nayi shiyasa nabar wajen ina gida faiza salati tazuba tace pinky wlhi AJ baida kirki komi zay iya aikatawa tsaki pinky tayi tace saikun dawo sannan leema takatse wayan gidansu faiza suka wuce tana parking tawuce part din faiza a upstairs leema tabi bayanta tana shiga tafada gado taware hannayenta tace woo happy me .
Leema tace kina Daison Sa kanki a balai manyan idanuwanta pinky takada tace kadan ma yagani dani yake zancen
shugowan tsako taji a wayanta tana budewa taga DM aka mata tana budewa taga sakone daga AJ
I will catch you kawai yarubuta hade da turo da hoton hannu .
Dogon tsaki taja tace aikin banza mikewa tayi tafara rage kayan jikinta tana wakan Selena Gomez
A bangaren AJ kam a fusace yabar hall din Dan tabbas daya kama pinky yau na lahira sai yafita jin dadi amma koba yauba zasu hadu kuma saiya nuna mata kuskurenta.
sha daya aka tashi a frnds day din .
yaukam kwanan farin ciki pinky tayi

Washe gari ranan picnic ne kananun kaya ko wanne yasaka pinky kam ansha madaran kyau bayan ishai aka fara zuwa daukansu zuwa wajen picnic din

Nasir yace pinky wancen motar Zaki shiga pinky tace aa a motata zani nasir yace yaudai kihakura da motarki sbd anhada kowa da partner dinshine OK tace sannan takarasa wajen motan tabude tashiga wani kamshine yabigi hancinta lumshe ido tayi tana shiga akayi locking motan cikin tsiririyar muryarta tace sannu fa shuru taji tabe baki tayi tashiga latsa wayarta tada motan akayi sukabar haraban cikin gidan saida sukayi nisa

Me tuka motan yace kece da sannu danni yau kwanan farin ciki zanyi daram taji gabanta yafadi a hankali ta daga kanta takalleshi tuni cikinta yaduri ruwa

Kokarin bude kofan motan tafarayi jikinta narawa muryarshi taji yace yarinya kin makaro aiyau me kwatanki sai Allah yau sai kwanan kurkutu wani zufane yaketo Mata duk da ac din motan a kunne yake

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 25

Ko kallonta bayyiba yaci gaba da driving dinshi .

Area ii suka nufa abakin gate din katafaran gidan yatsaya yayi horn baa jimaba gate man yawangale gate din

Cikin tane yawani kada kululu har cikin gidan yanufa sannan yayi parking.

Yafito afusace yazagaya yabude wajen me zaman banzan yariko hannunta dakarfi Dan har saida ta danyi kara .

Jan ta yayi dakarfi har zuwa cikin parlorn gidan yayi wurgi da ita akan kujera Dan saima data bige da stool din dake kusa da kujeran auch tace hade dakai hannunta kan goshinta daya fara fitar dajini kadan kadan.

Ko lura bayyi da ciwon da taji ba yace yau Allah kadai zay kwaceki badai bakida Tarbia ba bakisan kuma darajan mutane ba .

Yaukam zan nuna maki iyakarki tashi zakiyi kifara tsallan kwado tun daga wajen dining dincen har wajen kofa

Dasauri tace tsallan kwado kuma niban iya ba

Murmushin mugunta yayi yace koki tashi kiyi ko kuma yanzun nan insa bindiga in harbe maki kai kuma babu uban daya isa ya tinkareni akan nakashe karuwa kamarki hannunshi yakai bayan wandonshi yadauko bindigar .

Ai batasan sanda ta tashi tsaye ba jikinta yadauki rawa dakyar tazukunna kasa tafara tsallan kwadon wayarshi yadauko yafara mata video tanayi yana murmushin mugunta saida takai na ashirin tafadi a tsakiyan parlorn asume .

gashi jini baibar zuba agoshin taba hakan yasashi tashi cikin Sauri yakarasa inda take yakai

hannunshi ya  ciccibeta yayi upstairs da ita wani daki yanufa da ita yakwantar da ita akan katafaran gadon sannan yafita daga dakin bada jima waba yadawo rike da   first air box a hannunshi yakarasa yayi treating dinta sannan yafice daga dakin yana tsakin tsaki amma ai komin banza  yahorar da ita yau kashe wutan gidan yayi gaba daya sannan yafito daga parlorn yasa key yarufe hade dakarasawa wajen motar shi daidai lokacin wayar hannunshi tayi ruri murmushi yasaki Dan yasan pinky zasu tabbayeshi

Daukan wayan yayi yakafa akunnan shi tun kafin yayi magana nasir dagacen yace fisabilillahi ina kakai pinky wani malalacin murmushi yasaki sannan yace nasace ta .

Nasir dagacen yace kawa Allah AJ ka rabu da yarinyan mutane daria yayi yace saina koya Mata hankali tukunna ai tunda na rantse kuma shikenan sannan yace saida safe .

Baijira cewar shiba yakatse wayan yashiga motarshi yabar haraban cikin gidan ai good 7weeks dinnan sai tayi shi dani take zancen

Kuyi hakuri yau banyi posting dawuri ba banajin dadine amma insha Allah zuwa an jima zankaro maku

[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE  26

Wakar DJ khaleed yasaka yasa volume dan daidai sabida shidin ba maabocin jin wakoki bane wata rana yakan sane sabida nishadi

Cikin kwarewa yake bin wakar DJ khaleed harya karasa gida

Shikam yasan yau baccinshi zayyi me dadin gaske tunda yau komin banza yayi maganin me bakar fuskan ace warshi.

Karfe biyu daidai tabude idonta saidai dakin mamaye yake da duhu tsorone yakamata jikinta yadauki rawa dakyar tabude blanket tarufe duk  jikinta dashi danko fuskanta bata bari ba

Jin haushin karninka shiya kara tsorata ta batasan sanda tasaki fitsari a wando ba hade da hawaye

Cikin zuciyanta kam ta tsinewa AJ yafi so dubu daman haka yake mugu

Saida taringa zuba adduoi sannan bacci barawo yasaceta

Su leema kam hankalinsu yakasa kwanciya sunkira wayarta harsun gaji amma aka she.

Idonta biyu aka fara kiraye Kirayen sallah Dan dadi taji saidai bata sauko daga kan gadon  ba har saida gari yafara haske 7:00 am daidai tasauko daga kan gadon saidai dasauri takoma tazauna tana rike cinyoyinta tana  hawaye a hankali tace Allah ya isa wallahi .

Da rarrafe tashiga cikin bathroom tacire kayan jikinta tayi wanka  tadaura tawul din dake bayin sannan tafito tana tafia dakyar harta karasa bakin gadon tazauna tana hada uban zufa sabida azaban da cinyan nata yake Mata .

Kwanciya takoma tayi tarufe idonta tuni bacci yayi awon gaba da ita.

Karfe Tara da rabi yatashi daga bacci .

Wanka kawai yashiga  yana fitowa     yashirya cikin kananun kaya
Sànnan yakarasa dining yayi breakfast
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE  27

Yana gamawa yadauki key car dinshi da wayoyinshi yafita
Bangaren su Mami yawuce a bedroom yasameta tana aiki a system
Kan kujera yaje yazauna yace Mami good morning antashi lafia
Dagowa tayi tace lafia kalau sannan tace hidimarka nake tayi tun dazu ina zaban kayan akwatun inlw na .
Murmushi yayi hade dashafa kanshi yace Mami kina ji da Zuly fa murmushi tayi tace ko wace mata zaka aura haka zan sota .
Tashi yayi    tsaye yana Shafa kanshi yace Mami zanfita   OK tace hade dacewa zuly ta turo mun list din event din da zaayi before then yakamata ayi booking din dika   hotel  sbd baki kuma
AJ yace Mami bikin nanfa saura one month ai akwai sauran time ni sai nadawo dasauri yabar dakin yawuce parking space dasauri securitys suka bishi saurin tsayar dasu yayi yace thanks yau ni kadai zanfita OK sir sukace sannan yashiga cikin motanshi yabar haraban cikin gidan Kai tsaye area ii yanufa yana zuwa bakin gate din yayi horn megadi yawangale mai gate din yashiga  yasamu gu yayi parking sannan yafito
kai tsaye hanyan shiga parlor yanufa yasanya key yabude hade dashiga da sallama
parlorn yabi dakallo a tunaninshi ko pinky tafito upstairs yanufa yasanya hannunshi yabude kofan hade dashiga cikin dakin.
Kwance ya tadda ita tana bacci daga ita sai Dan tawul din data daura kuma baigama rufe Mata cinyoyin taba
gashin kanta ko yayi baza baza akan gadon gashi bakikirin saida yagama kare Mata kallo yayi saurin cewa auzubillah daidai lokacin pinky tabude idonta shikuma yayi saurin juya bayanshi Dan bazay jure ganin wannan halitta ba .
Cikin tsiririyar muryar ta tabude bakin tace  ina bukatan kayan sawa batare daya juyo yakalle taba yace kisameni a downstairs yanzu baijira cewar taba yabar dakin .
Bayan fitanshi da minti goma tamike dakyar tasa hannunta tayo da gashin kanta gaba sannan tagyara daurin tawul din tafita dakyar take tafia harta karasa downstairs juyowan dazayyi suka hada ido mikewa yayi dasaurii yace bakida hankaline zakii fito haka .
Shagwabe fuska tayi kaman zatayi kuka tace to to ba kayana bane ya lalace
Tsigan jikin shine yaji yawani tashi sosai yanda tayi maganar  ya birgeshi sosai yana son Mace me shagwaba .
[10/8, 18:10] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 28

Kara narkar da murya tayi tace auch nifa yunwa nakeji Dan ban taba ganin inda ake horo da yunwa ba tana maganar ne tana nufan wajen fridge ...

Baisan sanda yayi saurin dakatar da ita tahanyan kiranta dakarfi ba yace pinky .

Gaban tane yawani fadi tajuyo a tsorace tana kada idanuwanta hanyan upstairs yanuna mata da hannu

Marairaice fuska tayi tace wlhi harka tsoratani da muryan naka sai kace na dorom .

Kasa magana yayi gaba daya

Hanyar upstairs tanufa tana tafia dakyar harta karasa daki tazauna a bakin gado tana turo Dan karamin bakinta

Dakyar ya iya takawa yafice daga parlorn yashiga motarshi yabar gidan

A hanya sai tunowa yakeyi da yanda yaga pinky tahadu yarinyan ba laifi sai kace yar India dankyau dakuma gashi har gadon baya

Duk cikin zuciyanshi yake maganan nan saidai yarinyan tabata kyaunta tunda har tayi amfani dashi wajen rudar maza

Daidai xclusive boutique yafaka motar shi

Yama ci saa bakowa acikin boutique din hakan yabashi daman zaban mata dogayen riguna guda goma hade da flat shoe

yana gama tsiyayyan yabada ATM aka cire kudin sannan aka kaimai kayan har cikin mota .

daga nan chicken capitol yanufa yatsiyan mata abunda zatayi breakfast dashi hade Dana lunch kuma .

daga nan kai tsaye gidan yakoma koda yaje baisa me ta a parlor ba saiya haura upstairs knocking yayi pinky dake kwance tace come in Dan ita bataa damu daya ganta a yanda take ba .

Ganin batada niyan bude kofan ne yabude ya ajiye Mata kayan sannan yakoma downstairs yasamu gu akan kujera yazauna yana danna wayarshi.

Mikewa tayi dakyar ta dauki ledar da fito da kayan

Babu yanda ta iya haka tazira daya daga cikin rigunan kuma yayi mata kyau sosai saiko Jan tsaki take Dan rigar tamata nauyi acewarta .

Daure gashinta tayi sannan tasauka downstairs takarasa har inda yake zaune ta tsaya tarike kugu tana wani kada idanuwa tace Dan Allah horon kuma harda tsiyo mun wannan rigar me nauyin tsiya.

Kallonta yakeyi yanda taketa wani juyi a gabanshi ganin bazay jure ganin ta bane yace breakfast dinki yana dining uhmm tace hade dacewa nifa nagajii inbanda muguntа irin naka zaka wani Kawo ni nan ka ajiye saikuma tafara hawaye tace tafia ma dakyar nakeyi sbd mugunta ko sai takuma fashewa dakuka tafara tafia

Tana harde kafa aiko tazame AJ dake kallonta dasauri yatashi yataro ta tafada jikinshi .

[10/8, 18:11] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 29

hada ido sukayi ta saki tsaki tace ni wallahi daka barni nafadi hannu sai kace dutse .

Murmushin mugunta yasakar mata hade dasakinta tafada kasa Tim kakeji ihu tadan tsaki shiko juyawa yayi Yakoma yazauna yadauki wayarshi yaci gaba da latsawa yahade rai .

Ganin bai kallon tane tamike dakyar tace mugu daman duk soja mugune

Sannan tayi gaba takarasa dining taja kujera tazauna

Tashiga bude take away din .

Chips n egg ne sai chicken wings da titus fish hade da white rice .

Dayar ledar kuma sausage combo ne

Chips n egg din tafara ci kadan taci tabar sauran tasaka su acikin food flask din dake kan dining din sannan ta taka kafarta dakyar takarasa cikin parlour tayi wajen TV tace nidai ba kurma bace dazaa hanani kallo idan wani kurmane toh nidai ba ita bace

tsaki AJ yaja yatashi a fusace yanufeta yajanyota suna fuskantan juna yanunata da yatsa yace in bakiyi wasa ba sai kin kara tsallan kwadon nan yau fiye ma Dana jia Dan haka ki kiyayeni kuma tunda ba daya daga cikin yan iskanki suka tsiya tvn ba bazaa kunna ba.

Pinky tace naji saika tsakar mun hannu kada ka karyani Dan jikina sadane dashi sai yan iskana suke rikewa.

Wannan karan kam tafara shakar dashi baisan sanda ya murde hannunba ihu tasaki hade dafadawa fadeden kirjinshi.

Jiki dasauki nagode sosai da kulawarku masoyana

[10/8, 18:11] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 30

Cikin tsiririyar muryarta tace AJ akwai zafi fah

Tsakinta yayi sannan yace ki Kama kanki inbaso kike ki kuma tsallan kwadon nanba yau .

Yana gama fadan haka Yakoma yazauna

Pinky tace wayata fa Dan ina bukatar amfani da ita .

Wani mugun kallo yawatsa mata sannan yace na tsiyar .

karasawa tayi tazauna gabda shi tace dadin abundai bakai ka tsiyan mun wayarba yan iskana suka tsiyan mun Dan haka Kawai kabani wayata Dan kira zanyi wani horone harda kwace waya .

Harya bude baki zayyi magana wayarshi tayi ruri answering call din yayi hade dakafa wayan a kunnanshi yace wifey dagacen zuly tace baby bakaga text dina bane AJ yace bangani ba amma zanduba Zulu dagacen tace OK kagaida munda Mami OK yace sannan yakatse wayan

Pinky kam idanuwa ta tsura Mai cikin zuciyanta tace wai wani wifey

Text message din yabude list din event din daza ayi ta turo mai kuma ko wanne da kalar

kayan daza asa
Wani dogon tsuki yasaki afili yace ai wannan hauka ne .
Pinky tace badai Dani kakeyi ba mugun kallo yawatsa mata sannan yamike tsaye yadauki key car dinshi yayi hanyan fita ganin hakane yasa pinky mikewa tace ina zaka tafi kabarni banza yamata
Ganin hakane yasata fashewa dakuka tace in banda muguntа niba mayya ba sai atafi abarni nikadai
Tsayawa AJ yayi cak batare daya juyo yakalle taba yace waya Sani koke din mayyace kuma hakan yana cikin horon Dana ke maki yana gama fadan haka yabude kofan yafita sannan yasa key yarufe.

Tana hangoshi ta glass har yabar cikin haraban gidan komawa tayi tazauna akan kujera ta rafka uban tagumi .

Su faiza kam sun kira wayan pinky harsun gaji nasir kuma koya Kira AJ baya dauka .

Da dare dakyar bacci yadauketa a bangaren AJ kam daya rufe idonshi kyakkyawan fuskanta yake gani dogon tsaki yasaki hade dacewa meye amfanin hakan .

gashi yakasa daukan wani babban mataki akan yarinyan toma meye amfanin barinta agida na gobe zanmaida ita inda na Daukota da wannan tunanin
Captain ⚓ alamin junaid yakwana
Good night fans
[10/8, 18:11] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚

SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 31
Washe gari tun 8:00am ta tashi tayi wanka tasanya daya daga cikin dogoyen rigunan hade da parking din gashin nata sannan tazira slifas .
Tasauko downstairs
Tsaki tasaki data tuna jia yakulle tane tasone tazagaye gidan taga yanda yake tabe baki tayi hade tajuya wa tayi wajen dining wata kofa tagani da alama kitchen ne dasaurinta takarasa taburda handle din kofan tabude tashiga
Wow tace Dan kitchen din yamata kyau sosai gakuma color din blue n White yana daya daga cikin favourite colours dinta .
Wajen fridge tanufa tabude saidai babu komai aciki maidawa tayi tarufe sannan tanufi wata kofa saida tasanya hannunta tacire sakatan sannan tabude kofan
Wani murmushi tasaki hade dafita daga kitchen din a fili tace badai ka kulle kofan parlorn ba dankar infita gashi nasamu hanya Mafi sauki tafia tafarayi tana zagaye gidan harta karasa wajen swimming pool wow wow tace hade dacire doguwar rigar jikinta ta ajiye agefe daga ita

sai pant sai bra tafada cikin ruwan yanda kukasan kifi haka take ta wanka cikin ruwan tana wasa dashi .

Yana cikin breakfast ne yatuna da wayar pinky daya dauka acikin Jakarta tashi yayi yanufi bed side yadauki wayan sannan yakoma yazauna kunnan wayan yayi yafara dubawa tsintar kanshi kawai yayi dashiga cikin gallery dinta

Da hotunanta yaci karo birjik daya bayan daya yafara kallon hotunan kuma ko wanne cikin kananun kaya tadauka wayarshi yadauka yatura picture dinta guda biyu da alama sunfi ko wanne kyau .

Abunda yabashi mamaki bai wuce ganin yawancin apps dinta abubuwan addini bane dakuma complete Qur'an

yana gama breakfast din yatashi yakwashi wayoyin yafice Dan yau ko bangaren su Mami baije ba sbd Mr President baya kasan yaje ganawa da sarauniyar England .

Mami kuma yau sammakon zuwa gidan marayu tayi

Yau ma shikadai yafita saida yabiya jevinix restaurant yatsiyan mata abunda zata ci sannan yawuce yana karasawa yayi horn megadi yawangale mai gate din yashiga cikin farfajiyan gidan yayi parking sannan yafito.

Megadi ne yarugo dagudu yace oga tsayawa AJ yayi yace ya akayi gate man yace ina tunanin dai akwai spirit acikin gidan nan tun dazu nakejin motsi murmushi AJ yasaki hade dacewa babu komai acikin gidan nan baijira cewar gate man ba yayi hanyan shiga parlor sanya key yayi yabude yashiga hade da karasawa dining ya ajiye abincin sannan yawuce upstairs budema ya tadda kofan koda yashiga baigan taba tsayawa yayi a tunaninshi tana bathroom ne saida ya kusan mintina biyar a tsaye yaja tsaki yace pinky shuru yaji kuma ba alaman motsin ruwa karasawa yayi yabude kofan yaduba baigan taba dasauri yabar dakin yasauko downstairs yana kwala mata kira amma shuru cikin kitchen yanufa ganin kofar baya abude ne yasashi fita yana kwala Mata kira harya karasa wajen pool din

Tsayawa cak yayi ganin ta cikin ruwa gashi komi nata yabayyana tsigan jikin shine yawani tashi dasauri yace auzubillahi sannan yajuya baya yabude bakinshi dakyar yace pinky .

Juyowa tayi takalleshi tace sojan ruwa ya akai

AJ tsaki yaja yace kifito kishiga wancen dakin akwai tawul inkin gama ina parlor tabe baki tayi sannan tafito daga cikin ruwan tana wakar Nicki minaj saurin barin wajen yayi a zuciyanshi yace yarinyan nan nema take ta haukata ni .

[10/8, 18:11] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 32 Dakin daya nuna Mata tashiga tadauki tawul tadaura sannan tadauki wani Dan karami tagoge gashin kanta dashi sannan tafito daga dakin tanufi inda ta ajiye rigarta tadauka sannan tawuce ta kitchen tabi tana tafe tana goge gashin kan nata harta karasa cikin parlour . Zaune ta taddashi yana latsa waya cikin tsirriyar muryarta tace sojan ruwa antashi lahia. Dagowa AJ yayi yakalleta sannan yamaida kanshi kan wayarshi yace breakfast naki yana dining idan kingama kishirya zanmaida ke inda nadaukoki. Dasauri pinky tace aa aa nifa nafara jin dadin gidan nan kawai kabarni tana maganar ne tana nufan wajen dining baikula taba saida Takara cewa sojan ruwa nifa babu inda zani sannan yadago yakalleta yace tunda ba gidan ki bane dole kibarshi Jan kujera tayi tazauna sannan tajuyo takalleshi ta tabe Dan karamin bakin nata tace ai daman bance gida na bane tana gama fadin haka ta murguda mai

baki tajuya tafara bude ledojin .     AJ yace kinada matsalar rashin kunya kumani raini ne banso Hadiye chips din bakinta tayi tadan juyo tace nikuma matsala ta da sojajin ruwa naci da takura gaskiya m sorry too say duk matar da ta aureka tabani tashiga uku ta lalace Dan wata Rana inaga harbeta zakayi.   dan bakin ran naka yayi yawa juyawa tayi taci gaba dacin chips dinta tana daria kasa kasa Dan tasan ta tabo captain alamin junaid kam     .      A fusace ya tashi yakarasa inda take yacapko gashinta ihu tasaki yanuna ta da yatsa yace kisani mata sunfi dubu dasuke nemana amma ni zuciyata Mace daya kawai naba mawa kuma ko kasheta zanyi zata iya zama dani Dan haka kisan yanda Zaki ringa mun magana da respect m not ur mate .
[10/8, 18:11] Mrs Zaki: 📚 WAYASAN ASALINA 📚                SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 33
Tsakar mata kan yayi hade Dakara cewa kitashi kishirya Dan inada abunyi .
Fuskarta a murtuke ta tashi tawuce upstairs Tana turo baki
Doguwar rigar tasaka hade da Dan karamin gyalen sannan tasa flat shoe din
Tasauko downstairs a tsaye tasame shi yana ganinta yayi gaba tabi bayanshi
Mota yashiga yazauna sannan yamata key a hankali takarasa tabude wajen me zaman banza tazauna sannan tarufe .
Tada motan yayi sukabar haraban cikin gidan tunda suka Fara tafia babu Wanda yama wani magana har suka karasa maitama sannan batare daya Kalle taba yace inane gidan naku da hannunta take nuna Mai gidan har suka karasa bakin gate yayi horn megadi yawangele musu gate din suka shiga.
Yana parking tayi saurin bude murfin kofan tafita tana tsuke fuska leema ce tafito dasauri daga parlor taje tayi hugging din pinky tace ina kika shigane tsaki pinky taja tace wancen mugun sojan mana .
Bata jira cewar leema ba tabar wajen tana cika tana batsewa
karasawa leema tayi inda motar AJ take tace ina wuni batare daya kalle taba yace lafia sannan yaja motar shi yabar gidan.
tana shiga mama magajia ta taso tace beauty ina kika shigane kullin sai munkira wayanki amma akashe
Murmushi pinky tasaki tace wani mugun nasamu yasaceni leema ce tashugo tace bada jimawa ba minister yabar gidan nan shima kullin saiya Kira wayarki akashe
Upstairs pinky tawuce tace yanzu zanfita duk da ba waya a hannuna tana shiga dakinta tacire doguwar rigar dake jikinta tayi wurgi dashi sannan tanufi wardrobe tadauko wainsu kananun kaya tasaka hade da feshe jikinta da turare.
Hill shoe tasaka sosai tayi kyau sannan tasauko downstairs tace leema key car dina fah
Tashi leema tayi tanufi dakinta bataa jimaba tadawo rike da key car din Tamika mata
Pinky tace mama saina dawo mama magajia tace adawo lafia
Pinky tace leema ki kira minister kice ina hanyan zuwa guest house dinshi..
Fita daga parlor din tayi tanufi parking space Tama motar key tashiga tabar haraban gidan.
Saida yayi nisa sannan yace OMG namance ban bata wayar taba juya kan motar yayi yakoma gidansu pinky horn yayi aka bude Mai gate din yashiga
Yana parking leema tafito shima fitowa yayi daga motar leema Tana karasowa yace pinky fa .

Leema tace yanzun nan tafita
Wani dogon tsaki yasaki baisan sanda
yace gidan ubanwa taje daga dawowa zataa Kara fita
Kenan tazama kazar kowa ita dai leema kallonshi kawai takeyi daidai lokacin mama magajia tafito
Baima kula da ita ba yace ina taje leema data gama tsorata tace nima bansaniba .
A fusace yace karya kikeyi koki gayamun ko indau babban mataki akanki.
Bakin leema narawa tace guest house din minister .
Hannunshi ya dunkule yabugi motarshi dakarfi sannan yashiga mota yabar cikin gidan a fusace .
Zuciyarshi nawani tiriri hanyar wuse II yanufa saikuma yaja birki yatsaya
Yadafe kanshi cikin zuciyanshi yace meke damuna haka akan yarinyan nan .
Sorry fans Baku jiniba sai ynxu luv yhu ol
[10/9, 10:40] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 34
Wayar pinky din yakai hannu yadauka tsaki yaja yace daga kunna waya yau har anyi mata misscall yakai ashirin .
Tsintar kanshi yayi da duba miss calls din tsaki Yakuma ja dayaga kusan misscalls din duk mazane ciki ko harda minister .
wurgi yayi da wayar tafada bayan mota sannan yatada motan yabar wajen yawuce gida!

mintina kadan pinky tayi awajen minister Dan cemai ma tayi tafia tayi kuma tana bukatar tahuta shiyasa yabarta ta tafi gida sannan yacika mata Jakarta da kudi.
ana kiran sallan azhar takarasa gida.
Zaune ta tadda leema aparlor tana kallo .
Kujera tasamu tazauna hade dacewa kai nagaji gaskiya leema tace uhmm sannu
Kallon rashin fahimta pinky tamata tace meye na uhmm leema murmushi tasaki tace nidai fitan ki dazu yaja mun balai Dan kina fita captain yashugo gidan nan
Tsaki pinky tasaki tace sai akayi yaya leema tace ina cemai kinfita yahau balai ke kamarfa yaduke ni Dan harsai dayasa nafada mai wajen Wanda kikaje.
Wani kallo pinky tawatsa ma leema sannan tace amma kinban kunya da girmanki dakomai sojan ruwan kike tsoro .
Mikewa tsaye tayi hade da daukan handbag dinta tayi gaba tace nazauna anan sai jinana yahau kuma wallahi zamu hadune Dan sai yabani wayata leema kam ido kawai tazuba ma pinky Dan tasan duk zance takeyi itama tsoron AJ takeyi yanda baida mutuncin nan!
da dare kasa rintsawa yayi Dan tunanin pinky ne ya addabe zuciyarshi danko zuly dasuka jima tare yake kuma sonta baya tunaninta haka a yan kwanakin nan to meke shirin faruwa!

Washe gari karfe goma pinky ta tashi bayan tayi wanka tasanya three quarter ash color sai riga Me hannun vest sannan tayi parking gashinta tafeshe jikinta da turare

sannan tasauko downstairs leema tasamu da mama magajia suna breakfast karasawa tayi itama taja kujera tazauna hade dagaida mama magajia sannan takalli leema tace aro mun wayarki.

Daukar wayar leema tayi Tamika mata

Pinky ta ansa tayi dialing din number dinta saiko taji yana ringing saida yayi ringing harso biyu sannan aka dauka .

shima Dan yaga ansa leema ne shiyasa yayi picking.

Pinky a tsiwace tace da Allah malam ka kawo ma mutum wayarshi tunda bakai ka tsiya munba .

Tsaki AJ yasaki dagacen sannan yace bazan kawo ba sai naji Shaka .

pinky tace dadin abundai kasan bana kashe mutane balantana na shakeka nidai kawai ka kawo mun wayata ahe tana gama fadan haka ta tsinke wayar ta ajiye tanajan tsaki leema da mama magajia kallonta kawai sukeyi.

AJ bin wayan yayi dakallo yasaki murmushi daman yau dason ganinta yatashi yarasa dalili tashi yayi kawai yazira takalimin shi yadauki wayoyinshi hade da key car yafice ..

Yau wata babbar jeep yashiga Kai tsaye maitama yanufa

Mama magajia tace beauty kifa bi mutumin nan ahankali Dan naga alaman zay iya aikata komai turo baki pinky tayi hade dacewa kar yakawo mun wayata yagani .

Bai jima ba yakaraso gidansu pinky abakin gate din yatsaya yayi horn megadi yabude mai gate din yashiga.

leema tace inaga minister ne pinky tace m not in the mood ynxu kije kice mai bazan samu fitowa ba.

Murmushi leema tasaki sannan ta tashi tafita mamaki ne yakamata da taga AJ ne acikin motar fitowa yayi yace pinky fa leema dakyar ta iya bude bakinta tayi magana tace tana ciki AJ yace zan iya shiga dasauri leema tace why not bismillahh gaba tayi yana binta abaya

Har suka karasa cikin parlorn cikin azababbiyar muryarshi yayi sallama dasauri pinky tajuyo suka hada ido tawani saki tsaki hade da juya wa taci gaba dayin break dinta

Leema wajen zama ta nuna mai yamutse fuska yayi hade dazama kamar wanda aka takura mawa

Karasawa dining leema tayi tace ke ga AJ fa pinky a hasale tace Aina ganshi kice mai ya ajiye mun wayaata yatafi.

Mama magajia dasauri tace dakanki zakije ki amsa bata rai pinky tayi hade da turo baki .

mama magajia ce takaraso parlorn AJ yana ganinta yayi saurin saukowa daga kujeran yana gaida ita cikin tsakin fuska ta amsa Sannan tawuce dakinta

Leema ma upstairs tawuce yarage daga AJ sai pinky a parlorn dakyar ta tashi takarasa parlorn tana wani hade rai

Wajen dayake takarasa ta tsaya hade da mika mai hannunta tace ina wayata take .

Dagowa yayi yakalletaa duk sai yaji haunshinta yakeji daya Tuna jia.

Mikewa yayi tsaye yakarasa inda take Dan har suna iya jiyo numfashin juna ..

A hankali yace jiya ina kikajee tsuki tayi tace babu ruwanka da inda naje nifa banson sa ido kara matsawa yayi gabda ita itama tafara matsawa har saida sukaje karshen

bangon parlor yasanya hannayenshi yadafe bangon sannan yace tabbayenki nakeyi ina kikaje jiya .
batare dawani tsoroba ko shakka tacee wajen saurayina naje ko akwai wani abune
Idon shine yayi wani ja sannan yace good kibada hamma yana gama fadan haka yasaki bangon yakarasa yakwashe wayoyinshi yabar mata nata sannan yafice .
Tabe baki tayi tace matsalar kace tunda nidai ka kawo mun wayaata tanajin fitan motanshi taja tsaki tace sojan banza kawai sai mugunta fal ciki !
[10/9, 20:22] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 35

Driving kawai yakeyi amma zuciyar shi zafi take mai da radadi kuma yarasa dalilin jin hakan dogon tsaki yaja sannan yadau hanyan zuwa gida !
Daukar wayar tayi tafara duba miss calls tsaki tasaki Dan ganin yawan miss calls din number din faiza ta danna bugu daya faiza tayi picking .
Pinky tace hello amaryar nasir dagacen faiza tace bawani amaryar nasir wayarki kullin akashe tsaki pinky tasaki tace kema kinsan ba laifina bane abokin mijin ki dinnan baida M.
Faiza dagacen tayi daria tace indai AJ ne yanzuma kuka fara Dan baida hakuri ko kadan pinky tace ai daidai nake dashi Dan rainin hankalin !
Faiza tace yanzu dai yaushe zaki shugo Dan ko gidan baki saniba pinky tace nanda kwana biyu zaki ganni kigaida munda ango OK faiza tace sannan sukayi sallama!

Koda yakoma gida part dinshi yawuce Dan yaga mami nada baki .
Yana shiga dakinshi yarage kayan dake jikinshi yashiga bathroom yana fitowa yagoge jikinshi bayan yashafa mai da perfumes yasanya three quarter hade da singlet .
Sannan yakarasa dinning bude kulolin abincin yafara yi tuwon semovita ne da miyar agusi saiko zuba kamshi takeyi dayar kulan kuma daya bude ferfesun kan sane yasha kayan kamshi!
Sosai yazagey yaci tuwon Dan favourite food dinshi kenan !
Yana gamawa yawanke hannunshi sannan yadauki wayarshi yakoma parlour yazauna .
remote yadauka yachanza channel zuwa na Ball
Tunanin pinky yafado mai arai dasauri yadauki wayar shi yatura mata DM ta instagram Kaman haka
hope dai baki fita ba Dan kika tsake kika fita saina dauka babban mataki akan danna fahimci kanki narawa :
Tana kwance akan gado DM din yashugo hannunta takai tadauki wayan tabude tsaki tasaki sannan tace akwai saidai kadau babban mataki akaina Dan yauma ba gida zan kwana ba .
Kuma Dan Allah bana son sa ido dan na fahimta sojojin ruwan nan akwai shisshigi hoton gwalo ta tura Mai
Yana karantawa yayi wurgi da wayar tafadi akasa tafashe .

Lokaci nata tafiay gashi yau saura two weeks bikin AJ da zuly kuma ayau ranan

Saturday zaa fara event har zuwa ranan daurin aure!

AJ wata hadaddiyar blue suit yasaka yayi matukar yin kyau Faisal ne yashugo dakin yana murmushi yace ango angama shirya amarya fa tsaki AJ yasaki yace inbanda sherri irin na zuly wai Dan hauka wani event ne fiye da guda goma sai kace hauka .

Faisal yace nidai muje dan kai take jira gaba AJ yayi Faisal yabi bayanshi.

Karasawa yayi inda amarya zuly take tare da wayayyun kawayenta yaran manya ita kuma tsanye take da hadaddan Blue material sai kyallli yakeyi dayake da darene yana yakarasawa yamika mata hannu ita kuma tasanya hannunta a nashi suka karasa wajen motan da aka bude musu suka shiga sannan aka maida murfin kofan aka rufe a tsakiya aka sasu kai tsaye Zeus paradise hotel suka nufa .

Gaskiya hall din ba karamin haduwa yayi ba dan fadan kyaun wajen bata bakine Dan ankashe kudi wajen saruwan wajen abunku da bikin manya sosai event din yayi kyau Dan duk wani meji dakanshi saida yaje event din.

Ranan Friday
aka daura auren captain alamin junaid da amaryarsa zulaiha fariz dabo!

anan Kano dinma saida akayi event wajen kala biyu sannan washe gari suka dunguma zuwa Villa achen ma anyi shagalin biki sosai sannan zuwa dare kuma aka tafi dinner a the glam hall ranan dai anyi barin daloli !

Pinky dakyar ta iya tashi daga kan kujeran zuciyarta ba dadi leema ce tadago takalle ta tace amma gaskiya bikin yayi kyau ashe dai captain yana murmushin tsaki pinky tasaki tace toh ina ruwana dashi tana gama fadan haka tawuce upstairs tashige Dakinta tafada gado saidai Sam tunda aka nuna bikin AJ jikinta yawani chanza tsuki tasaki tace uhm meye damuwana dan ya Aura wancen mummunan !

Bayan antashi daga dinner kai tsaye amarya gidanta aka wuce da ita dake efab estate subhanallahi nikaina bazan iya fadan saruwan gidan ba Dan gari gudane kuma irin ginin turawan nanne Tunda su suka kera abunsu.

Ana kaita kowa yawatse aka barta ita kadai Bayan tafiyansu bada jimawa ba AJ yashiga dakin amaryar sa !

yana shiga dakin wani kamshiy yabigi hancinshi murmushi yasaki ganin zuly zaune a tsakiyan katon royal bed din a hankali yataka yakarasa har inda take yazauna hade dakai hannunshi yaye gyalen dukar da kanta tayi alamar jin kunya cikin rikitacciyar muryarshi me rikita ma mata lissafi yace wifey kunya ta kuma kikeji murmushi tasaki daukarta yayi yakaita har bakin bathroom Sannan yadireta yace kishiga kiyi alwala ina zuwa .

Bayan shigan ta bathroom ne yafita daga dakin yawuce wani part yarage kayan dake jikinshi sannan yashiga bathroom yawatsa ruwa hade dayin alwala sannan yazira wata milk color din jallabia sannan yabar part din yadawo nata part din yashiga kitchen yadauko gasasshiyar Kazan da aka gasa musu tako sha kayan kamshi dansai kamshi takeyi me dadi sannan yadauki fresh milk da cups yawuce bedroom zaune yatadda ita .

Saida ya ajiye tray din yace wifey taso miyi sallah tashi tayi hade dabude wardrobe

tadauko hijab sannan suka tada sallan suna idarwa yamata tabbayoyi akan addini kuma daidai gwargado tasani takuma bashi amsa.
Daga nan kuma yaciyar da ita dakanshi harta koshi sannan shima yaci yana gamawa yakai tray din kitchen yawanke hannunshi sannan yadawo!
a Daren ranan dai bakaramar soyayya yanuna ma zuly ba Dan yasameta a cikakkiyar budurwa .
[10/10, 11:03] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 36
washe gari bayan AJ yadawo daga sallan asuba dakanshi yadauki zuly yakaita bathroom yagasa mata jiki sannan yafito yakyaleta tayi wankan tsarki.
bayan tafito ne tasanya wata doguwar riga da AJ yafito mata fashion ta tada sallah !
tana idarwa ta dukar da kanta kasa tace baby ina kwana antashi lafia
AJ dake zaune kan kujera sankowa yayi har inda take yazukunna hade dakai hannunshi yadagota yana tsakar mata murmushi yace lafia qalau wifey
Hope kema kintashi lfy murmushi tasaki kawai hannu yakai yacire mata hijabin sannan yadauketa cak kaman wata baby yakaita har kan gado yakwantary da ita sannan shima yakwanta suka koma bacci.

dakyar ta iya tashi daga kan gado tana bin agogon Dakinta dakallo wani dogon tsaki tasaki Dan tasan har tayi missing lectures guda !
Tashi tayi tashiga bathroom tawatsa ruwa dasauri tafito tana cikin shiri leema tashugo dakin harara pinky tawatsa mata hade dacewa kinfa san Inada lectures yau karfe tara amma koki tasheni murmushi leema tasaki hade dacewa afwan kokin manta bagida nakwana ba dawowana kenan pinky tace ina zan sani tunda ina bacci kika fita .
leema tace hakane fah da alama dai yanzu kinhuta da takura captain tunda yayi sabuwar amarya pinky batasan sanda tasaki tsaki ba tace matsalar shice danni harna manta dawani AJ .
Murmushi leema sannan tafita
Yau doguwar riga na atamfa pinky tasaka kuma bawata kwalliya tayi sosai ba amma tayi kyau sosai kam Dan karamin gyale tayafa kalar kayan sannan saita tsaka flat shoe hade da daukan handbag dinta tasauko downstairs dakin mama magajia tashiga tagaisheta sannan tawuce parking space tama motar key tashiga sannan tabar gidan!

Sati daya sukayi suna shan amarci
Dan hutun shi saura kwana biyu yakare kuma tare da zuly zasu tafi!

Da dare suka shirya zasu gidan su zuly ta damu AJ subiya shoprite zata tsiya abu babu yanda ya iya haka Suka biya yana parking motar pinky ma tana shugowa kusan waje daya sukayi parking saidai Sun riga pinky shiga ciki !
Duk da itama abu dayane kawai yakaita zuly wajen saida perfumes tanufa AJ yace saline gayamun perfumes kikeso dasai insa akawo maki .
juyawa fuskanshi yayi gefe dan matan wurin Sun cikashi da kallo yana juyawa yahango pinky daga ita sai yar yellow din gown daya Tsaya mata iya gwuwa sai dan

karamin gyale baisan sanda yasaki tsaki ba yayi wajen da take dasauri yana karasawa yakai hannunshi yajanyota gefe inda ba mutane kallon juna suka farayi pinky tayi saurin kwace hannunta tace meye haka hannunta yakara rikowa yace wane irin rigane kikasa haka kiko san wannan shigan arna ne sbd duk ilahirin jikinki abayyane yake idan har bakison zaman garin nan ya gagareki dole kiringa sa kayan mutunci bata fuska pinky tayi tace irin kayan danake dasu kenan kuma ni nasha gaya maka bana son sa ido !
Dayan hannunshi yakai yaja mata baki dakarfi sannan yace rashin kunya na dawainiya dake nadai gaya maki keba kyauba saison sa kayan masu kyau yana gama fadan haka yasaketa yabar wajen yakarasa inda zuly take ya amsa basket din pinky tana kallonsu har suka je suka bada ATM aka cire amount din kudin nandanan taji ranta yabaci.
dan taga sai nan danan yakeyi da zuly tsaki taja tace Dan rainin hankali kawai matar taka aiba kyau tafini ba !.

Daga nan gidansu mami suka wuce
[10/10, 21:03] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 37
a parking space yafaka motar Sannan yasanya hannunshi yabude murfin motan zuly ma haka perfumes din data tsiya tadauka kallonta AJ yayi yace tsarabar su mami ne kenan daga mai kai tayi alamar eh sannan suka jera sukaayi part dinsu mami!
da sallama suka shiga cikin parlorn dagudu Mimi da sury suka tashi suka taro zuly hade da amsan shopping bag din hannunta gaishe da mami tayi cikin ladabi sannan tasamu gu tazauna !
AJ ma waje yasamu yazauna hade dagaida mami !
Atare su mimi suka ce ya ina wuni lafia qalau yace sannan yace Waiku bazaku koma skool bane marairaice fuska sukayi sukace ya AJ this week zamu koma tunda muna final year ne .
Mami tace daga zuwanka zaka fara takura ma yara sosa kanshi yayi hade dacewa Abba yana office ne mami tace yana office amma yana tare da baki !

tana Gama tsiyan abunda yakaita tabar wajen tana driving amma gabaki daya tunanin AJ takeyi sbd yanda taga yama gama raina mata wayo tayaya ma Zayce mata mummuna bayan tafi matarshi kyau Allah yakuma hadata dashi tabbas saita gaya mai magana daidai bakin gate tatsaya tayi horn gate man yabude mata gate tashiga haraban cikin gidan !

Tana parking tafito hade da daukan handbag dinta dakuma shopping bag din tayi cikin gida mama magajia kawai tasamu Dan yauma leema ba gida zata kwana ba '

zama tayi a parlorn suka dan taba hira da mama magajia sannan ta tashi tawuce upstairs tana shiga dakinta tarage kayan jikinta tashiga bathroom tawatsa ruwa Sannan tafito Dan karamin rigar bacci tasaka red color hade da feshe jikinta da turare dan pinky akwai son kamshi fadawa kan gado tayi tajayo bargo sannan takara gudun AC .

hira sosai akeyi saidai sam hankalinshi baya tare dashi tunanin yarinyan yadame shi ko yanzu takoma gida oho ji kawai yayi bazay iya zama ba saiya je yaga kota koma gida !. Dagowa yayi yakalli zuly yace wifey Bari inje indawo mami tace alamin ina kuma zaka bayan goma takusa ai gida yakamata kutafi yanzu !

shafa kanshi yayi dandai baisan karyar dazay ma mami ba hakanan babu yanda ya iya Mami tacewa zuly ta tashi su tafi har wajen motarsu suka rakasu saida sukabar haraban gidan sannan suka koma cikin gida!

shi kam har ga Allah yaso yaje yaduba ko takoma gida toma meyasa ban amshi phone no dinta ba duk acikin zuciyarshi yake wannan maganar baisan sanda yasaki tsaki ba a fili zuly tayi saurin juyawa takalleshi tace baby lafia batare daya kalle Taba yace lafia !

Koda suka koma gida part dinshi yawuce zuly ma tawuce nata bangaren dan ita ba irin me kula da mijin nan bane sam Amma akwai ladabi !

Saida yayi wanka sannan yadauki wayarshi yakira zuly yace takawo mai coffee .

Dasauri tawuce kitchen tahada mai hade da daurawa akan Tray da cups guda biyu sannan tawuce sashin shi zaune ta taddashi akan kujera ya lumshe ido aje Tray din tayi hade da cewa baby ga coffee din Dan wallahi bacci nakeji kasan kwana biyu bana samun bacci sosai bude idonshi yayi hade dacewa baki samun coffee dinba kuma zaki tafi karasawa tayi tasa Mai sannan ta ajiye tace inka gama kasameni bacci ne a idona kallonta Kawai yakeyi Dan sam sai yanzu yasan bai auri kalar macen daya keso ba shiyafi son wacce zata ringa bashi Kulawa amma ita komi sai ansata harta juya zata fita saikuma tajuyo tana murmushi tace baby dazu nagama waya da daddy yace yashirya mana honeymoon zuwa Paris zuwa nanda jibi yakamata mutafi dagowa yayi yakalleta sannan yace babu Paris din daza aje shagwabe fuska tayi tace haba baby umarnin daddy nefa kuma kasan burina kenan miyi honeymoon dinmu a Paris tsaki yasaki yace inbiki mutafi nikuma inbar aikina kenan toh bazay yuyuba saidai idan ke kadai zaki tafi hawaye tafara yi ganin hakane yasashi cewa tafi dakinki idan kuka zaki mun dan ko kukan me zakiyi babu inda zaaje tunda ni nake iko dake ba daddy dinki ba dasauri tabar dakin tana shashshekan kuka !

Tana fita yaja wani dogon tsaki daman yasani dole yasamu irin wannan matsalan nan dan dabiun yan gidan sune duk abunda me martaba yakeso shi ake yi dogon tsaki yakara tsaki akaro nabiyu yace badani zaayi haka ba ni na banbanta dasauran dan babu wanda ya isa ya juyani .

[10/10, 21:38] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 38

Saida yagama abunda yakeyi sannan yakwashi wayoyinshi yawuce sashin zuly Dan yama samu har tayi bacci shima kwanciyan yayi hade da jawota cikin jikinshi !

Washe gari dason ganin pinky yatashi saida sukayi breakfast sannan yafita !

yau manyan kaya yasaka kuma sunyi matukar yi masa kyau batare da tunanin komai ba yadauki hanyan zuwa gidan su pinky abakin Gate din yatsaya yayi horn megadi

yawangale mai Gate din yashiga yana faka motar shi yakai hannunshi yakira me tsama flowers ruwa yasashi yamai sallama da pinky bada jimawa ba yadawo ya ritsina yace gata nan fitowa OK AJ yace hade dakai hannunshi aljihu yacuro kudin dabaisan adadin suba yamika mai godia yaringa zubawa sannan yabar wajen yana tsaye leema tafito takarasa inda yake tsaye tagaida shi fuskanshi ahade ya amsa sannan leema tace aiko pinky bata nan batare daya tabbaye ta inda taje ba yashiga motar shi yabar gidan a fusace leema bin motar tayi dakallo lallai taga alaman yau captain sai a hankali komawa cikin parlor tayi

tsaki yaketa tsaki shikadai harya fita daga maitama afili yace basai nakara zuwa gidan ba yarinya sai son gantali da sassafe takama tafita ranshi kam yau yabaci dan wallahi yaso ganinta kafin yabar garin !

Sai cen yamma pinky tadawo aparlor tazube tana nishi alaman gajia leema tace aiko akwai gajia tunfa safe kika fita gashi yau kinyi babban bako kuwa .

Kallonta pinky tayi tace babban bako kuma waye shi murmushi leema tasaki tace waye kuwa banda yawuce captain AJ ina cemai baki nan ko magana baimun ba yashiga motarshi yabar gidan nan afusace tsaki pinky tasaki tace matsalar shice pinky tace aiko yau ran abokin fadan naki abace yake saidai fa nafara tunanin wani abu tsareta da idanuwa pinky tayi sannan tace mene leema tace naga tsantsar soyayyarki a idon AJ

Bata fuska pinky tayi hade dacewa Allah ya tsareni tayaya ma mugun nan zay fara sona Tab kinko san tsanan da mugun nan yakemun hmm haka fa jia Danya Raina mun hankali yake cemun wai banda kyau kuma namaga matar nashi wata mummuna da ita dan nafita kyau saidai da alama tsanar da nake mai yashafi matarshi dan jiya dana gansu tare bakiji yanda zuciya ta take zafi ba Daria leema tafashe dashi tace wallahi kema kinfada pinky cikin rashin fahimta tace nafada mene leema tace son captain mana harararta pinky tayi tace Allah ya kiyayeni dason wannan bakin mugun amma leema kinma cuceni pillow din kusa da ita tawurga ma leema tace Allah yamun tsari da son wannan mugun duk da baida aibu matsalar shi daya mugunta tamai yawa !

Ranan Sunday da yamma jirgin su yatashi zuwa Lagos dayake achan yake aiki suna sauka daya daga cikin yaranshi sukazo suka dauke su kai tsaye gidanshi dake epetedo suka wuce suna karasawa wanka kawai yayi yasanya uniform dinshi subhanallah kada kuso kuga yanda kayan sukama captain AJ kyau dan zan iya cewa uniform din yafi mai kyau fiye dakowa.

yau kwana biyu kenan kome takeyi saita tuno da AJ tashi tayi zaune daga kwancen da take tace idan ma wani mugun abun kake shiryawa akaina Allah yafika ina ga shiyasa nake yawan tunaninka mtsw taja tsaki tace toma meya shafeni dashi dazan ringa tunaninshi tashi tayi tasauka downstairs Dan bazata iya da tunanin wannan mugun ba

[10/10, 22:30] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 39

dayake yau weekend ne yana gida babu inda zashi yana kwance a daya daga cikin

kujerun parlorn zuly tafito daga bedroom tsanye take da wainsu fitinannun English wears Dan zan iya cewa komi nata a bayyane yake duk da ita din bawani cikane da ita ba tana dai da dukiyar Fulani Saidai basosai ba a yangace takarasa inda yake tsira mata ido kawai yayi dan bata fiye shiga irin hakaba tafi sanya normal a atamfa tayi zamanta amma yau kam ta birgeshi tashi yayi tsaye yabude mata hannayenshi tashige ciki sosai ya matsewa a jikinshi yana shakan kamshin jikinta me dadi gashi ta tada mai da shaawa duk da Tana da saurin gajiyawa wajen harka shikuma mutum ne me tsananin bukata shiyasa sometimes yake tunanin zuly ba kalar macen da yake so bane tun a parlor yafara rikita ta dayaga parlorn bazayyi ba daukanta yayi cak yayi bedroom da ita saida ya ajiyeta akan gado yana niyan cire kayan jikinshi zuly tace baby yanzu fa nayi wanka kuma zaka sa nakuma yin wani ko saurarenta bayyiba dan baima jin abunda take cewa sosai ba !

bayan angama harka ne sukayi wanka Suka shirya yace mata zasu fita zuly tace baby da yamma haka saida suka shiga mota harsun fara tafia yace daga nan wajen aiki yana mun nisa shiyasa zamuyi parking Zuwa Victoria island murmushi tasaki dan daman batasan mutane anan epetedo ba amma tasan mutane a Victoria island .

Kuma zatafi jin dadin cen!

bayan sunje yanuna mata inda zasu koma daga nan suka wuce sukayi shopping a Maryland sannan suka wuce gida!

daga yau zuwa Sunday sunsha soyayya sosai duk da bata jurewa sosai wajen uzurin sa! Dayake yau Monday tunda wuri yafita sabida ana jiranshi a office.

Suna da meeting bayan sungama meeting dinne yakoma office dinshi saidai sam yakasa tabuka komai ayau daya fara aikin tunanin pinky zay hanashi gashi yau wata daya kenan rabonshi da ita gashi kuma kwanakin nan ana aiki sosai balantana yace zayje abj ko kwana dayane yayi bamasai su mami sunsan da zuwanshi ba haka yagama tsarawa a zuciyan shi saidai yabar tafiyan zuwa ranan Friday da yamma sai yatafi!

ABUJA

yau gidan faiza pinky tawuni sukasha hira sabida gidan yana mata ba dadi tunda leema tayi tafia

Shiyasa ma kwana biyu take wuni a guest house din minister!

dayake yau tunda wuri AJ zay fita zuly bayan tarako shi tadan jingina da jikin motan tace baby jiya mukayi waya da mum wai zamu je dubai yin shopping kasan perfumes dina Sun kare sannan zaama farida shopping din birthday dinta wani mugun kallo yawatsa mata sannan yace babu inda zaki dan babu wanda yakemun iko da matata saini dan haka matsa mun daga wajen mota intafi yauko magana takasa yi janyo murfin motan shi yayi yabar gidan yaukam harga Allah yabata haushi wato bazay dinga bin umarnin iyayen taba bazayma yuyuba dole da ita zaayi tafiyan tunda dai tasa rai !

Parlour tawuce tadauki wayarta takira lambar hajia bugu daya tadauka dagacen tace

zulaiha kuka zuly tasaka mata tafada mata yanda sukayi da AJ hakuri mum tabata hade dacewa yanzu zankira shi dolema yabarki ayi tafiyan nan dake !
Godia Tama mum dinta sannan sukayi sallama yana shiga office kiran wayan hajiyar zuly nashugowa daukan wayan yayi yakafa akunnan shi yagaida ta cikin ladabi kaman tana gabanshi dagacen tace alamin zulaiha takirani tana mun kuka wai kace baza tayi tafiyan ba girgiza kai AJ yayi tuni ranshi yabaci kenan karanshi takai wajen mahaifiyarta aiko babu inda zataje tunda shi yake iko da matar shi bawani ba.
A fili sai cemata yayi gaskiya mum kiyi hakuri amma babu inda zata yana gama fadan haka yakashe wayan !
[10/10, 23:04] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 40
Shida na yamma yatashi a office yawuce gida yauko tarban da zuly take mai batayi ba shima banza da ita yayi bayan yayi wankane yasanya doguwar jallabia baka yawuce dinning room yazauna yafara bude food flask din tsaki yasaki dan abincin kuku ya ishe shi daidai lokacin zuly takaraso wajen taja kujera tazauna tace baby sannu dazuwa yauwa kawai yace sannan yace nifa nagaji dacin jagwalgwalan kuku gwanda kidage kifara dafa mun abinci dakanki !
shagwabe fuska tayi tace baby kasan fa ban iyaba haka nan zaka ringa hakuri kana cin na kuku dan bansan tayaya zanfara girki ba dogon tsaki yasaki sannan yamike tsaye yawuce kitchen yahado tea yawuce parlour itama parlorn tamike tabishi !
kusa dashi tazauna tace Dan Allah baby kabarni inje tea dinshi yaci gaba dasha sannan daga baya yace wato harda karana kika kai wajen mum toh bari kiji babu wanda ya isa yasani inyi abunda banyi niya ba dan haka nagama magana zulaiha babu inda zaki !
shuru tayi nadan lokaci sannan tace shikenan Tunda kace bazanje ba na Hakura saidai harsu auntie Aisha zasuje mazajen su sunbarsu batare daya kalle taba yace dani da mazajen su ba daya bane ni nasan mena keyi!
Batun girki kuma dole ki koya dan bazan juri cin abincin kuku ba kallonshi tayi kamar zatayi kuka tace saidai kayi hakuri baby Dan wlhi agida ko kitchen bana shiga harararta yayi sannan yatashi yabar mata parlorn !

Kamar yanda AJ yace yau ranan Friday da yamma ya tafi abuja saidai yacema zuly wani aiki zashi a Benin
yana sauka yasa aka kawo mai mota kai tsaye gidansu pinky yawuce yana horn aka wangale mai gate din yashiga yafaka motarshi wannan Karon ko sawa akira mai ita bayyiba kai tsaye hanyan shiga parlorn yayi

abakin kofan parlorn yatsaya yayi knocking leema ce tazo tabude mai kofan tana ganinshi tasaki murmushi tagaidashi hade dacemai tana ciki bismillah shugo bayanta yabi har cikin parlourn yana shiga itama kuma tana fitowa daga kitchen hannunta rike da katon trey tsayawa tayi cak shima haka kallon juna suka farayi leema ce tace ga wuri kazauna dasauri pinky tawuce dinning tana jera kulolin leema Kuma barin parlorun tayi saida tagama jera abincin tajuyo takalleshi sannan tace ango kasha kamshi dagowa yayi

yakalleta sai yaga yau takara mai kyau dayake gajeran wando ne a jikinta sai yar half vest juyar da kanshi yayi sannan yace zaki taimaka kije kichanza kayan jikin ki !
pinky dake tsaye tace sorry bazan iya ba tunda ba ajiyeni kayi ba murmushi yasaki sannan yace inhar bakije kincire kayan nanba yanzu zandau babban mataki akanki
Pinky tace hmm a gidana fa kazo kasameni zaka wani mun iyayi mikewa yayi daga kan kujeran yakarasa har inda take tsaye yace gidan kine amma yanzu zaki barshi bata ankara ba sai gani tayi yadauketa cak ihu tasaki Tafara mai magiya akan yasauketa saida yakaita har cikin mota yarufe sannan yashiga yatada motar sukabar haraban cikin gidan
Goodnight fan's
[10/11, 20:34] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 41
Suna barin gidan pinky tace wallahi zanma ihun barawo AJ baisan sanda yafashe da daria ba sannan yace in zaki shekara kina ihu a banza dan babu wanda zay jiki kuma kimun shuru da bakinki dan banson surutu.
Hararar shi tayi tajuyar da kanta gefe .
wuse market yawuce daidai wani katon shago yafaka motarshi sannan yazare key din yafita yakulle dayake motar akwai tintac babu wanda yake ganinta har yaje yadawo yasanya kayan daya tsiyo abayan mota sannan yashiga yatada motar sukabar wajen suka wuce .
Daidai bakin gate yatsaya yayi horn megadi yawangale musu gate din suka shiga a parking space yafaka motar sannan yakalli pinky da sauran kadan tafashe dakuka yace muje hannunta takai tabude kofan tafita tana binshi abaya har bakin kofan parlour sannan yabude kofan suka shiga kitchen yawuce da kayan sannan yadawo parlour yakalleta Tana tsaye tayi folding hannayenta Tana turo baki .
zama yayi yadaura kafa daya kan daya sannan yace yanzu dai ba tsayuwa zakiyi ba sai kace soja kitchen zaki shiga kimun girki juyawa tayi dasauri takalleshi hade dacewa wall...
Bai bari takarasa ba yace kizaba cikin biyu kimun girki ko kuma kiyi tsallen kwadon dayafi na ranan kuma babu tausayi .
sannan ki tabbatar kinyi me dadi inba hakaba yin tsallen kwado babu fashi .
kunkuni tafara yi tayi hanyan kitchen din .

tana shiga tace sai son mugunta fal ciki bude ledojin tashigayi sannan tawanke kayan miya ta nika bayan tagama tawanke kayan cikin .
jalof din talia tadaura saidai tasaka su carrot da green beans da sauransu hakan yakara ma jalof din taliyan kyau dakuma dadi sannan ta yanyanka hanta tasaka aciki .
Bayan nan kuma tayi ferfusun kayan ciki dayasha kayan kamshi tuni gidan yabide da kamshi dan pinky bada ga nanba wajen iya girki saida tagama gabaki daya tasaka su acikin kuloli sannan tahada mix juice na kayan itatuwa tana gamawa takwashi kulolin takai dinning tajera sannan takoma tadauko plate da cups ta dawo ta ajiye .
cikin tsiririyar muryarta tace nagama juyawa yayi yakalleta hade damikewa tsaye yakarasa dinning din yazauna yace Allah ya ceceki yarinya yanzu sai kije kidaura wata riga kan wainnan kayan kidawo ..

Barin wajen tayi tana harararshi harta wuce upstairs cikin dogayen rigunan daya tsiyo mata ranan cikinsu tadauka daya tazira sannan tasauko downstairs takarasa dinning har taja kujera zata zauna yace bakiyi serving dina bafa turo dan karamin bakinta tayi tace sai wani sani aiki kakeyi sai kace wannan mummunar matar taka banza yamata danshi burinshi baiwuce yaji cikinshi a cike ba Dan yunwa yakeji tana gama zuba mai ta tura mai plate din kusa dashi hade da mix juice din .

Jan kujera tayi tazauna tana harararshi tagefen ido tunda yafara cin abincin bayyi magana ba Dan abincin ba karamin dadi yamai ba cikin zuciyarshi kam cewa yayi dama zuly ce ta iya abinci haka

Yana gama cin abincin yakora da mix juice din sannan yace alhamdulillah ba laifi yadanyi dadi amma ba sosaiba .

Pinky tace kamace bayyi dadi ba mana baisan sanda yasaki murmushi ba hade dacewa taimakonki nayi yarinya danaci abincin nan dan kar azubar tunda babu Wanda Zaa bamawa kuma kinsan da ban iya cinyewa ba dole kiyi tsallen kwado .

mikewa tsaye tayi tace nidai ka maidani inda ka daukoni kallon rainin hankali yamata sannan yanuna kulolin abincin yace wakuma zakibar ma wannan yacinye ai ko nanda kofa baza kijeba saikin zauna kinci abincin nan kema inba hakaba kuma Saidai ki kwana anan kuma kiyi tsallen kwado Dan bazan iya zubda abinci ba.

komawa tayi tazauna tasanya abincin dan daidai sannan tafara ci daman yunwa takeji saida taci takoshi sannan tasha juice din Tamike ta kwashe kayan takai kitchen tawanke tamaida komi inda yake sannan tadawo parlour ta taddashi Yakunna TV tsaya mai tayi akai tace nagama tashi ka maidani inda kadaukoni tunda naga alaman kana jin dadin tsatar mutane .

wajen zama yanuna mata da hannu yace saina huta zanbar gidan nan babu yanda ta iya haka takarasa tazauna tana hade fuska dan ba karamin shiga hakkinta yayiba.

saida suka kusan mintina goma babu wanda yama wani magana sannan kaman daga sama taji AJ yace ina kike zuwa da kullin baki zama agida .

. kuma ina iyayenki suke dahar suka barki kina abunda ranki keso duk a lokaci daya yajero mata tabbayoyin .

Saida tadau lokaci sannan tace bazan iya amsa maka tabbayoyin kaba tunda ba zamanka nakeyi ba kawai malam tashi kamai dani gida.

Wani mugun kallo yawatsa mata yace zaki shekara anan kenan idan har baki amsan tabbaya taba...

juyar da kanta tayi sannan tace zaman kaina nakeyi Dan banda iyaye sannan batun fita kuma wajen mutanan harka na nake zuwa.

Dasauri yace subhanallahi auzubillahi.

kenan kedin kamar yanda nake tunani kedin karuwa ce ......

babu abunda ta tsana sama da akirata da suna karuwa kuma yanda ta fahimta yasan yanda zayyi yabata mata zuciya tuni taji haushinshi yakamata a hasale tace bakayi karya ba nidin karuwa ce tabbas babu karya aciki dan haka tunda nabaka amsan tabbayarka saika tashi kamaidani gida .

girgiza kai yayi hade dacewa bangama tabbayar kiba .

yana gama fadan haka ya kara fuskatan TV yaci gaba da kallonshi hankali kwance ganin yana neman ya raina mata wayone .

Tace nifa ina da inda zani gwanda ma kayi kayi kagama tabbayarka intafi ko kallonta bayyiba balanta tasamu amsa daga gareshi .

wayar shice tayi ruri hannu yakai yadauka hade dacewa wifey lafia kalau na iso dagacen zuly tace Allah yadawo mun dakai lafia gani sai missing naka nakeyi .

shima cikin wani mayaudarin muryarshi me rikita ma mata lissafi yace wifey nikaina bakisan halin danake cikiba a yanzu amma karki damu gobe zandawo saida sukasha hira sosai na soyayya sannan sukayi sallama pinky gabaki daya sai taji ranta yabaci kuma tarasa dalilinta najin hakan yana ajiye wayar tasaki wani dogon tsaki da batasan tasaki ba .

fuskar shi dauke da murmushi yajuya yakalle ta harara ta galla mai sannan tasanya pillow tarufe fuskanta dashi shi shi daria ma tabashi .

sai cen yamma likis sannan yace mata ta tashi sutafi cikin sauri tamike tsaye tana cika Tana batsewa gaba yayi tabi bayanshi har sukabar parlorn wajen me zaman banza tabude tashiga shikuma yashiga wajen driver yatada motar sukabar haraban cikin gidan saida sukayi nisa Sosai sannan yace yanzu kenan ina ajiye ki agida zaki fice .

Juyar da kanta tayi tana kallon gefen titi sannan tace kwarai kuwa dan zaman gida bai dace daniba.

AJ yace hmm gaskiya ne kuma fa inaga gwanda kawai injuya mukoma cen gidan saiki tazama ke kadai kinga ba daman fita kenan dan rufeki zanyi

Dasauri tace Dan Allah kayi hakuri nifa wasa nakeyi murmushi yasaki sannan yaci gaba da driving .

Suna zuwa bakin gate yayi horn megadi yawangale gate din suka shiga yana parking tayi saurin kai hannunta zata bude murfin motan tafita yayi locked din shi hade dacewa .

Daga yau kada inkuma ganin kafarki awaje idan har kina son kwanciyar hankali Dan naji labarin kinfita duk abunda namiki ke kika ja ..

Kallonshi takeyi irin na ya raina mata wayon nan tace hmm sai kace ubana ko wani mijina wlhi fita yazama dole tunda ba zamanka nakeyi ba .

hade fuska yakuma Yi sannan yace nidai umarni nabaki idan kuma baki jiba shikenan zakiga abunda zay faru .

Yana gama fadin haka yayi unlocked yace mata fitar mun amota hararar shi tayi sannan tabude murfin motan tafita .

ta tura mai murfin kofan dakarfi tayi cikin parlour tsaki yasaki yace zanyi maganin kine sannan yabar cikin gidan kai tsaye gidansu Faisal yawuce Dan Sun kwana biyu basu haduba .

tana shiga parlorn leema dake zaune a dinning tafashe da Daria tace lallai Romeo n Juliet tsuke fuska pinky tayi hade dawuce wa upstairs.

Sai dare AJ yabar gidansu Faisal yakoma gida saida yayi wanka sannan yakwanta dayake yayi dinner agidan su Faisal .

Tunanin pinky ne cike acikin zuciyar shi wani bangaren na zuciyarshi yasan yafada ma son pinky wani bangaren kuma yana mamakin ta yanda akayi yayi saurin kamuwa da sonta alhalin ga irin sanaaar data keyi.

washe gari flight din safe yabi zuwa Lagos karfe sha daya daidai tamai a Lagos yaran shi ne sukazo daukanshi kai tsaye gida suka wuce dashi.

Suna faka motar zuly tafito dagudu takarasa tayi hugging dinshi hade damai kiss abaki batare dawani kunya ba yadauketa cak sukayi cikin parlour saida yakaita har bedroom sannan yadireta yasanya bakinshi cikin nata yayi kissing dinta hade dafada mata yanda yayi missing dinta itama sosai tayi enjoying sabida rashin shi da tayi jia .

Bayan Sun kimtsa ne sunyi wanka sannan suka fito parlor suka zubai akan kujera kanta ta daura akan cinyar shi .

Yau tunda ta tashi taji bata jin dadi gashi tunanin AJ ya dameta yauko downstairs bata sauko ba dan tana bukatar kadaicewa !

Haka rayuwa taci gaba da tafia duk da a yanzu AJ yana ko karin mantawa da pinky a zuciyarshi ita ma anata bangaren haka dinne sabida ta tattara hankalinta gabaki daya wajen exams din dasuke fama dashi a yanzu gashi final year suke sosai ta maida hankalinta danko fita yanzu batayi sai in zataje skool!

yauda matsanancin zazzabi zuly ta tashi Dan dakyar ma ta iya yin sallah shiyasa Tunda safe AJ yakaita asibiti suna zuwa sukaga doctor sabida sudin na musamman ne.

Bayan Sun shiga office din doctor Samuel ya dan mata tabbayoyi tabashi amsa sannan ya ibi jininta yaba wata nurse akan takai lab agwada bayan haka Kuma Zuly tamai complain akan yawan ciwon cikin da take fama dashi bada dadaiwa ba nurse tadawo da result tabawa Dr .

Saida yagama karance karancen shi sannan yadago yakalli AJ yamika mai hannu yace Congrat ur wive she's 2month pregnant AJ sabida sabagen murna baisan sanda yayi hugging zuly ba yafara gode mata .

Dr Samuel yace ta tashi suje zaymata scanning tashi tayi tabi bayanshi baa wani dadaiba suka fito daga dakin scanning din komawa mazauninta tayi sannan Dr yakalli AJ yace sorry Sir matarka bazata iya rainon Kwan dake jikin taba sabida kwayakwayan haihuwanta basuda karfi dan cikin zay iya zubewa ako wane lokaci nandanan fuskan AJ yachanza yace what bayani sosai Dr yamai harya fahimta hade dacemai dakyar ta iya samun wani cikin ma nangaba kuka zuly tafashe dashi .

Dafe kanshi AJ yayi yace Dr yanzu babu taimakon dazaka iya mana girgiza kai Dr Samuel yayi sannan yace taimako dayane saidai idan akwai wacce zata iya taimakonku acire Kwan haihuwar ajikin matarka asa mata saita rainan muku dan dake cikinta har zuwa haihuwanta .

zufa ne ya keto ma AJ sannan yace toh shikenan Dr mungode zamuyi shawara duk

yanda ake ciki zakaji mikewa tsaye sukayi atare yarike hannun zuly suka fita tunda suka dau hanyan komawa gida babu Wanda yama dan uwanshi magana sbd kowa da irin abunda yake tsakawa acikin zuciyanshi .
pinky ne tafado ma AJ a rai dasauri yace wifey nasa man mana mafita
[10/12, 17:26] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 43
cikin murna zuly tajuyo tana kallon AJ tace menene mafita murmushi yasaki hade dacewa yau yau dinnan zamu tafi Abuja sai mubi flight din karfe shida kallon rashin fahimta zuly tamai tace badai su mami Zaka gaya mawa ba girgiza kai yayi sannan yace Mace daya zata iya mana wannan aikin ita kadaice na yarda zata iya zuly !
Bayan sunkoma gida a parlour suka yada zango hade dazuwa kitchen yahado ma zuly tea da kanshi yake bata harta shanye sannan takwanta ajikin shi tace inaga baby kai kadai yakamata kayi tafiyan nan tunda kadai ji abunda Dr yafada zamu iya losing baby dinmu shafa mata cikinta yashigayi yace bazan iya tafia inbarki ke kadaiba zuly tace karka damu tafiyan kwana daya bawani abu bane sannan akwai masu aiki zasu kula dani .

Karfe biyar da wani abu aka kai AJ airport shida jriginsu yatashi zuwa Abuja kamar wancen lokacin yauma sawa yayi aka kawo mai mota kai tsaye gidansu pinky yawuce yanata addua Allah yasa yasameta .
Daidai bakin gate din yatsaya yayi horn megadi yabude mai gate din yashiga haraban cikin gidan daidai lokacin pinky tafito da alama fita zatayi cikin sauri yafito daga motar tsayawa tayi tana kallonshi harya karasa inda take cikin sanyi yamata magana yace pinky please magana me muhimmamci nake son miyi wani kallo ta watsa mai sannan tace fita fa zanyi .
Tsaki yasaki sannan yaja hannunta tana tirjewa dakomai yakaita cikin mota yarufe sannan shima yashiga yatada motar sukabar haraban cikin gidan .
A hasale tace nifa nagaji da Zaka ringa zuwa kana saceni ahe wlhi nagaji baikula taba yaci gaba da driving dinshi dan baison suyi fada sabida da lallashi yau zay bita abakin gate din gidan yatsaya yayi horn gate Man yawangale musu Gate din suka shiga cikin haraban gidan yana parking yakalli pinky data hade rai kaman zata fashe yace muje kara gyara zama tayi tace babu inda zani tsaki yaja sannan yace kina da matsala rufe kofan yayi yazagaya yabude murfin motan yariko hannunta dakarfi yajata har cikin parlour sannan yamaida kofan yarufe.
kallonta yayi sannan yace kizauna turo baki tayi hade dasamun waje tazauna shima zaman yayi sannan ya fuskance ta .
A tsanyaye yakira sunanta dagowa tayi takalleshi taga shima ita yake kallo yace wani taimako zaki mun kuma ko nawa kike son zan baki ke koma menene zanbaki yanzu dai ina son ki nutsu kiji abunda zangaya maki.
Gyara zama yayi sannan yafara mata bayanin hade dacewa ki taimakeni ki mana rainon cikin a firgice ta mike tsaye ta dafe kirjinta tace bazan iyaba bazan taba iya waba .
rike kanshi yayi daman yasan zaysha wuya wajen amincewar ta mikewa yayi yakarsa inda take hade da rike mata hannu yace kigaya mun kome kike so zanbaki koma menene

kina haifa mun dana zaki kama gabanki Kuma namiki alkawarin zan fita daga rayuwarki .
Batasan sanda hawaye yabata mata fuska ba tace kayi alkawarin kome nakeso zaka bani dasauri yace zanbaki sannan yariko hannunta suka karasa kan kujera yace fada mun abunda kike bukata .
Share hawayen fuskanta tayi tace sannan tace iyayena kawai nake son kafin na Haifan maku yaran ku ko yarku kanemo mun iyayena sannan bayan haka ina son kafita a rayuwa ta ka kyaleni .
rike kanshi yayi yace babbar magana pinky murmushi tasaki tace bazaka iya ba kenan fine sannan tafara kokarin mikewa tsaye rikota yayi yace zan iya .
Murmushi tasaki sannan tace kayi alkawari daga mata kai yayi alamar eh .
hade dacewa gobe yakamata muje ayi aikin pinky tace naji amma bazan iya zaman Lagos ba dasauri AJ yace ina kike son kizauna pinky tace gidana girgiza mata kai yayi sannan yace bazay yuyuba dole kibar duk wani saurayinki har sai kin haifo mun yarona kinbani Kuma Lagos zaki zauna sabida komi naki Zay dawo hannu na .
Pinky tace naji Allah yakaimu goben lafia kaima daga gobe yakamata kafara naka aikin sannan Tamike tsaye tace saika maidani inda ka daukoni murmushi yasaki yace ba dole naba atare suka jera suka fita daga parlourn suka karasa suka shiga mota sukabar cikin gidan !
har gida yamaida ita sannan yace flight din safe zamu bi saiki zauna cikin shiri ok tace sannan tabude murfin motan tafita shikuma yabar gidan.
Tana shiga mama magajia da leema suka ce baidai miki komai ba daga musu kai tayi Sannan tasamu gu tazauna tarike kanta mama magajia tace Beauty yadai kallonta pinky tayi sannan takwashe komi tagaya musu mama magajia tace anya bakiyi kuskureba kuwa girgiza kai pinky tayi tace bana tunanin haka inhar zanga iyayena leema dogon numfashi tasaki tace tabbas pinky kinyi babban kuskure gaba nake jiye maki mikewa tsaye tayi hade da daukan handbag dinta tace babu wani kuskure danayi Kuma daga baya kwa dawo Lagos din idan na haihu sai mudawo nan.
Tana gama fadan haka tawuce upstairs .
AJ kam tun a hanya yakira zuly yafada mata farin cikine yacika mata zuciya tuni taji zazzabin yafara sauka dakuma wata damuwa
[10/12, 18:36] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 44

Tana shiga dakinta tayi wurgi da handbag dinta sannan tarage kayan jikinta kayan ta tafara hadawa a dan Kit mai dan girma zay daici kaya kaman kala biyar haka tana gama shirya komai tahaye kan gado!
Washe gari kamar yanda yace karfe bakwai tamai agidan su pinky yana shiga haraban gidan taleko ta upstairs ta duba taga ko shine daman tariga tashirya gyalen kayan kawai tadauka sannan tadauki handbag dinta da wayarta tasauko downstairs leema da mama magajia suna zaune a parlor .
Leema tashi tayi ta tari pinky tace wallahi jiya banyi bacci ba ina tunanin anya bakiyi kuskuren yarda da uzurin captain ba kuwa murmushi pinky tasaki hade dacewa karki damu nasan babu wani kuskuren danayi wajen taimaka ma wasu.

Sannan ta kwalawa me masu guga kira tace yadauko mata akwtinta a upstairs har wajen mota su leema suka rakata akan zasu taho zuwa nextweek idan leema tagama exams tunda ita pinky tagama bayan ansa akwatin ne abayan mota pinky tashiga baya AJ Kuma yana wajen me zaman banza sannan driver dinshi .

Daga musu Hannu sukeyi har sukabar haraban cikin gidan kai tsaye airport suka wuce jirgin karfe takwas suka hau zuwa Lagos.

karfe goma suka isa Lagos suna sauka driver yazo yadauke su .

zuly kam tasa an shirya musu kayan breakfast tana jin horn din mota tafito dasauri daga parlour suna parking AJ yafito takarasa dasaurinta tayi hugging dinshi pinky ma fitowa tayi daga bayan motan tana kallon yanda zuly take ta shigewa jikin AJ juyar da kanta tayi dan bazata jure kallon suba sabida zuciyarta wani zafi yake mata data rasa dalili.

peck yakai ma zuly a kumatu hade da daukanta cak sannan yakalli pinky yace muje Bin bayansu tayi zuciyarta nawani zafi har cikin parlorn suka karasa sannan yadire zuly murmushi tasaki tace daga jia zuwa yau har nayi missing dinka kugunta yarike yana murmushi sannan yajata kan kujera suka zauna yakalli pinky dake tsaye har a lokacin yace zauna mana .

Zuly juyawa tayi takalle pinky danhar saida taji gabanta yafadi sabida ganin kyawun pinky fuskanta a tsake tace sannu dazuwa murmushin karfin hali pinky tasaki sannan tace yauwa mikewa zuly tayi tace baby muje kuyi break nasan dai bakuyi ba jan hannunshi tayi sannan takalli pinky tace taso muje dakyar pinky ta iya tashi tabi bayansu har zuwa dinning din zuly dinne tayi serving dinsu sannan takoma kusa da AJ tazauna suna ciyar da juna abinci .

Abincin kadan pinky taci Tamike tsaye tabar wajen basu masan takoma parlour ba saida suka gama suka ankara .

Komawa parlorn sukayi suka zauna sannan AJ ya gabatar mada zuly pinky a matsayin wacce zatayi rainon cikin su murmushi tasaki sannan tace baby baka fada mun sunan taba shafa kanshi yayi dan ya rasa sunan dazay fada mata dan baison tasan asalin pinky.

Pinky da taga haka cikin tsiririyar muryarta tace sunana farida murmushi zuly tasaki tace amma mungode sosai AJ ne yakalli agogon hannunshi sannan yace wifey dauko gyalenki kizo muje time yana wucewa mikewa tayi tawuce bedroom !

bata jimaba tafito tsanye da katon gyale mikewa tsaye sukayi AJ da zuly suna rike da hannun juna har suka karasa wajen mota dakanshi yabude ma zuly wajen me Zaman banza sannan yazagaya yabude mazaunin driver yashiga pinky ma tashiga sannan yatada motan sukabar haraban cikin gidan!

Tunda suka fara tafia suke hirar su dan har mancewa sukeyi akwai mutum abaya a haka suka karasa reddington hospital yana parking pinky tayi saurin fita dan zuciyar ta sam babu dadi!

suma fitowan sukayi sannan suka karasa ciki kai tsaye office din Dr Samuel suka nufa cikin kankanin lokaci aka gama komai aka maida cikin jikin pinky !

Dr shawara sosai yabasu akan kula da pinky har zuwa ranan dazata haihu godia suka ma Dr Samuel sannan sukabar asibitin suna barin asibitin gida suka wuce saida sukayi

sallan azhar sannan zuly da AJ suka shiga bedroom sukabar pinky azaune !
Bayan Sun shiga bedroom AJ yace yanzu zanje inkaita gidan da zata zauna sabida bana son zama Dakowa zuly tace badamuwa hakan ma yayi amma dole saida me aiki AJ yace nasani nariga nasa an Nemo mun wata dattijuwa !
Bayan sungama magana ne sukayi sallama da pinky sannan suka wuce wajen me zaman banza pinky tashiga tazauna tuni zuly taji wani kishi balantana ma yanda taga sunyi kyau dajuna dakyar ta iya daidaiita kanta tadaga musu hannu sukabar haraban cikin gidan!

tunda suka fara tafia babu wanda yama wani magana har suka isa wani katafaran Dan karamin gida horn yayi abakin gate din aka wangale musu suka shiga saida yayi parking sannan yabude murfin motan yafita yazagaya yabude ma pinky kofan hade da tsakar mata murmushi ita ma murmushin tasakar mai sannan tafito rike da handbag dinta shikuma booth yabude yadauki akwatin kayanta sannan suka jera suka karasa bakin kofan parlorn yasanya keys yabude sannan suka Shiga atare .
dakuna uku ne Kuma ko wanne akwai toilet aciki sannan sai dinning room dakuma kitchen a gefen shi !
Har cikin bedroom yakai mata akwatin sannan yadawo parlour yasameta yace zaki iya zama ke Kadai kuwa .
Hararar wasa ta watsa mai hade dacewa meka maidani AJ dake jingine ajikin bangon parlorn yasanya hannayenshi acikin aljihun wandon shi yace matsoraciya mana .
turo baki tayi alamar shagwabea shikuma yasakar mata murmushi sannan yace duk abunda kike bukata akwai idan ma kina bukatan wani abu ma saiki kirani sannan zuwa gobe da yamma zaa kawo maki me tayaki hira .
OK tace sannan tashiga bedroom din da taga ya ajiye mata akwatin ta komi na dakin fari ne hakan yasata tsakin murmushi hade da ajiye handbag dinta akan kujeran dake gefen gadon .
Sannan tafito parlour inda tabarshi nan tasame shi wajen dinning tanufa hade dacewa yamma yana kara yifa kada madam dinka ta tajiran ka murmushi AJ yasaki hade da karasawa inda take yace yanzu dai ba wannan ba dame zakiyi dinner sai in miki take away .
Yamutse fuska pinky tayi tace ban fiye cin abincin waje ba yanzu ma kitchen zanshiga In daura kaje kawai saida safe.
Tana gama fadan haka tawuce kitchen shima Bin bayanta yayi dasauri yace kinsan fa baa son kina aiki sosai kifada mun abunda kike so in yaso sai in dafa maki dakaina kinsan fa nidin gwani ne wajen iya girki juyowa tayi suka hada ido tayi murmushi tace aa nagode bude fridge tayi tafito da nama leda daya sannan ta ajiye AJ harde hannayen shi yayi yace kigaya mun abunda zan tayaki dashi pinky tace toh ka yanka mun albasa .
store yashiga yadauko albasa sannan yafito yadauki wuka .
A ranan dai tare sukayi duk wani aiki hade dakai kayan dinning suka jera sannan pinky takalleshi tace lokaci yanata tafia kada madam dinka fa tafara kiranka .
Kara gyara zama yayi hade dacewa zantafi amma sai naci abinci pls zo kiyi serving

dina .

serving dinshi tazo tayi sannan itama tazuba jalof din kuskus din Dan kadan tazauna hira sukeyi kadan kadan har AJ yagama yamike yace nizan tafi dagowaa tayi takalle shi hade dacewa mu kwana lafia.

murmushi yasaki hade dacewa babu ko yar rakiya kenan make kafada pinky tayi tace uhm a gajiye nake fah saida safe kawai OK yace sannan yafice tabi bayanshi dakallo tana ji yabar gidan !

Dogon ajiyar zuciya tasaki sannan tamike takwashe kayan takai kitchen sannan tawuce daki miss calls tagani a wayanta leema tafara kira Sun dadai suna hira sannan daga baya suka yi sallama!

ranan Kwanan kadaici pinky tayi dan dakyar bacci yadauketa a bangaren AJ kam soyayyar su sukasha shida zuly!

Washe gari ruwan Tea kawai yasha zuly tarakashi har wajen mota hade da kissing nashi sannan yabar gidan kai tsaye gidan da pinky take yawuce !

Horn yayi megadi yabude mai Gate din yashiga saida yayi parking sannan yafito yakarasa cikin parlorn da sallama yashiga amma baiga kowa ba motsin da yajine a kitchen yasashi karasawa tsaye yayi yana kallonta tana ta kiciniyar hada abun break gyaran murya yayi dasauri tajuyo takalleshi tace zuwan sassafe haka daga mata gira yayi sannan yace badole naba naringa zuwa duba ki kullin murmushi tasaki tace sabida babyn ku dake cikina dai kazo .

Batare daya bata amsa ba yakarasa kitchen din yashiga tayata aiki atare suka gama komai sannan sukayi breakfast suna gamawa yamike yana duba agogon hannunshi yace idan nadawo office zanbiyo OK tace hade dacewa adawo lafia!

Cikin kwanakin nan gaba ki daya agidan pinky AJ yake wuni Kuma komi tare sukeyi kaman mata da miji ga kuma wata muguwar shakuwa da suka karayi dan yanzu AJ hira yake zama suyi sosai da pinky ita kanta tayi mamakin sauywan shi amma tasan duk akan babyn su dake jikin tane !

yauma kamar kullin yana tashi a office kai tsaye gidan pinky yawuce da sallama yashiga parlorn ita Kuma tana kwance akan kujera daga ita sai yar karamar blue gown daya tsaya mata daidai gwuwa .

tana ganinshi tayi saurin tashi zaune tace sannu da zuwa murmushi kwance akan fuskar shi yace yauwa hade da samun waje yazauna !

Cikin tsiririyar muryarta tace wallahi nidai nagaji da zaman gidan nan haka nan kullin ina gida sai kace matar kulle AJ yace yaza kiyi tunda dai banga wajen daza kibi langwabe kai tayi tace uhmm ko shopping ne mana muje Kuma mani shaawar amala nakeji Kuma irin na Yoruba dinnan daria AJ yafashe dashi hade dacewa yanzu ina zan samo maki wani amala koda asa iya ta tsiyo maki girgiza kai pinky tayi tace tare zamuje dakai dan me zafi nakeso kuma miyan yaza mana akwai yaji sosai !

shafa kanshi yayi sannan yace toh tashi ki chanzo kaya saimu tafi tashi tayi dan har

tana hadawa dasauri tawuce daki shikuma yabi bayanta da kallo dan yaga takara wani cikane gakuma cikinta yafara tasowa tunda yanzu cikin yana na cikin na wata hudune!

Bata jima ba tafito tsanye da doguwar riga har kasa sannan ta nada gyalen sai takalmin data tsaka me shegen tsini dasauri AJ yatashi tsaye yace ina zakije da wannan takalmin kallon rashin fahimta tamai sannan tace bangane ina zanje dashi ba alhalin kaganshi a kafana !

AJ yace gaskiya baza kifita da takalmin nanba dan kawai ki mana asaran baby .

Hararar shi tayi tace toh ni wallahi dashi zanje komawa yayi yazauna akan kujera yace indai dashi zaki fita babu inda zamuje turo baki tayi tace muguntar dai tana nan bazaka chanza ba daman nasan Dan cikin dake jikina ne yasa baka mun muguntan daka saba shikenan sai afasa fitan katafi gida kawai tana gama fadin haka takoma bedroom.

Dafe kanshi yayi yace pinky rigima tashi yayi yabita dakin zaune ya tadda ita abakin gado tana cika tana batsewa .

Gyaran murya yayi sannan yace tashi muje kisa kome kikeso juyar da kanta tayi tai kaman bata ji shiba saida yakara magana sannan ta tashi tadauki handbag dinta suka fita a waje suka tadda iya pinky tace iya saimun dawo

[10/13, 17:49] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 46

wajen me zaman banza tabude tashiga shikuma yashiga mazaunin driver yatada motar suka bar Haraban cikin gidan kai tsaye the lagoon restaurant suka nufa yana parking suka fito atare suka jera zuwa cikin restaurant din tunda suka fito idanun mutane akansu yake har suka karasa ciki suka zauna sannan AJ yasa akawo ma pinky amala baa jima ba aka kawo mata aka direshi agaban ta AJ yace gaki ga amala sai kibada himma murmushi tasakar mai sannan tawanke hannunta tashiga cin amalan nan ba kakautawa tana cinyewa tana kalli AJ daya zuba mata ido tace wallahi ban koshi ba Daria yayi sannan yace akaro kenan daga mai kai tayi alamar eh .

girgiza Kai yayi sannan yasa aka kawo mata wani shima saida ta cinye shi tass sannan tayi gyasa Tasha ruwa tawanke hannunta AJ yace gaskiya ban taba tunanin kina dacin abinci haka ba sai yakuma fashewa da daria .

Itama kuma dariyan da yake mata ne yabata haushi ta galla mai harara tace ai dole kamun daria tunda kaida matarka kun cuceni gashi kamanni na sai chanzawa yakeyi ina zama yar lukuta kayana duk sunfara mun kadan .

Sai tafara hawaye saurin kai hannunshi yayi yadaura akan bakin ta yace yi hakuri kibari mufita anan sai kiyi kukan .

Harara ta galla mai hade dakai hannunta tacire hannunshi tace wallahi nafara dana sani ashe gaskiyan leema ne da mama sunfini gaskiya gashi kullin hsnnunshi yakai yakuma toshe mata baki sannan yasanya dayan hannunshi a aljihun shi yacuro kudin su yamika musu sannan yadauke ta cak suka fita waje mutane kam sai munsu da kallo sukeyi ita Kuma sai tawani langwabe a jikinshi tana hawaye sata amota yayi.

Yayi saurin zagayawa yashiga yatada motan dan yaga kunya take neman bashi agaban mutane saida sukayi nisa AJ yace ci gaba ina jinki kuka tafashe dashi tace kullin kasala bacci amai ni wallahi nagaji nafasa taimakon muje kawai acire cikin amaida ma matarka

abunta itama taji yanda nakeji wannan karan kam jikin AJ sanyi yafara yi bakin hanya yasamu yafaka motar sannan yajuyo yakalle ta hade dakai hannunshi yadago fuskanta yashiga share mata hawayen fuskanta yace kiwa girman Allah kiyi hakuri ki Haifa mana abunda ke cikin ki Dan Allah idan kuma kayane yanzu sai muje asiyo maki wainda zasu maki daidai !

kukan ta sagaita dashi sannan cikin muryan shagwaba tace Kuma ni bana son wainnan dogayen rigunan dan damuna sukeyi English wears zaa tsiya dasauri AJ yace naji ai kome kikeso haka zaayi murmushi tasaki hade dacewa batun aman fa dakuma kasalan da nakeji da yawan bacci dole mukoma wajen Dr yabani magani !

AJ a zuciyan shi yace Tab gaskiya rigiman pinky yawane dashi .

A fili Kuma sai yace hakuri zakiyi har ki haihu kina haihuwa zaki daina jin kome zaki dawo normal .

Saida ya tabbatar ya kwantar mata da hankali sannan yatada motan suka wuce !

Mega plaza mall suka wuce yana parkin yajuya yakalli pinky yace toh dan gyara fuskan ki kada agane kinyi kuka hararar shi tayi tace haka zantafi tunda ba ajiyeni sukayi ba !

AJ da yaga batada niyan gyara fuskan hannunshi yakai bayan mota yadauko handbag dinta yabude yako ci saa akwai powder da lipstick bata ankara ba sai jin hannunshi tayi akan fuskanta yashiga guge mata fuskan tsira mai ido kawai tayi har yagama yadauko powder yashafa mata sannan yadauko lipstick yace oya bude bakin batasan sanda tasaki murmushi ba tace bani insa dakaina girgiza mata kai yayi yace ai tunda nafara nizam gama bude ko bakin tayi yashafa mata sannan yagyara mata gyalen yarufe mata gashinta yasakar mata murmushi yace toh madam rigima muje ko turo baki tayi tace niche me rigima AJ dasauri yace bake ba sorry madam muje ataree suka fito daga motan suka jera sukayi cikin mall din bangaren English wears suka nufa maza ne da mata kala kala awajen gashi an tsira masu ido hannunshi yakai cikin nata yarike juyawa tayi takalleshi shi kuwa gabanshi kawai yake kallo !

Har suka karasa inda zata ringa chanza kayan wainsu riga da Wando aka bata taje tagwada saidai ko kugunta wandon bai kaiba yatsaya ji tayi kaman tayi kuka rigar kuma ta matseta sosai batasan sanda tace captain sunmun kadan miko wani daria yafara yi ciki ciki Dan yasan duk cikin kayan babu wanda zay mata rigima ne kawai irin nan pinky saida tagwada kaya wajen kala goma basuyi mata ba daga karshe tamaida kayanta tafito tafashe dakuka hade dazama akan kujera !

AJ yace meye na kuka basai and tsiya wainsu ba me kula da wajen English wears ne takaraso tana murmushi tace matarka tacika shagwaba English wears baza suyi mata ba saidai gown kallon juna AJ da pinky suka farayi suna jin wani abu yana ratsa duk wani jijiyoyin jikinsu dakyar AJ ya iya cema matar akawo gown din .

Gown din takawo aiko pinky tana gwadawa suka mata cas maaikaciyar wajen tayi murmushi tace your wife looks so beautiful Masha Allah perfect match Zaku haifa yara masu kyau tsit sukayi jin abunda matar tace sannan AJ yace tahada musu kayan takai ayi totally wajen biyan kudin suka karasa ATM dinshi yabada aka cire amount din kudin kayan sannan suka fita aka kai musu kayan har cikin mota sannan sukabar haraban wajen .

Tunda suka fara tafi kowa da abunda yake tsakawa acikin zuciyar shi har suka karasa gida yana Kai mata kayan parlour yace saida safe daga mai kai kawai tasamu damanyi !

[10/13, 20:43] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 47

Har yaje gida tunanin pinky yakeyi !
yana parking yafito saidai yau zuly ko zuwa taren shi batayi ba
A parlor ya tadda ita tacika tayi fam da alama tun dazu take jiran dawowan shi
Sannu da zuwa tace mai yauwa yace hade dasamun waje yazauna kallon shi tayi tace Captain tsakaninka da Allah yau ina ka tsaya dagowa yayi yakalleta dan tabbayar rainin wayo tamai !
saida takara maii tabayyar sannan yakalle ta fuskanshi a hade yace ina kike tunanin zan tsaya zuly da kishi ne fal acikin zuciyanta tace wajen farida mana tayaya kullin Zaka ringa zuwa wajenta bayan akwai me kula da ita gaskiya da tsake dole kadaina zuwa wajenta idan yaso in takusa haihuwa sai adinga zuwa ni wallahi da anbar mun cikina dan nafara dana sani daga ganin ta wannan zata iya kwace miji ni banma san a ina kasamo taba!
Ran AJ tuni yafara baci dogon tsaki yasaki hade da daka mata tsawa yace dole inje sabida cikin mune ajikinta mu takema dawainiya danme bazamu kula da ita ba gwanda tun wuri kicire duk wani kishi a ranki Dan babu abunda zay shiga tsakani na da ita yana gama fadan haka yatashi yawuce bedroom rai bace !
Tuni jikin zuly yayi sanyi tayi data sanin fada mai maganar gashi captain baida saurin sauka idan yayi fushi .
Dakyar tamike tawuce bedroom tana zuwa tafada jikinshi tashiga bashi hakuri tureta yayi ajikin shi hade dacewa kiyi saurin cire duk wani zargi acikin zuciyanki Dan babu abunda zanyi da yarinyan nan tana haifan abunda Ke cikinta zata Kama gabanta !
marairaice fuska zuly tayi tace kayi hakuri insha Allah bazay kara faruwa ba murmushi yasakar mata hade da kissing dinta!
sannan yace su abba suna damuna akan rashin mu zuwa hutu gashi bansan yanda zamu bullo ma abun ba tunda nagaya masu kina da ciki
Shuru zuly tayi sannan tace ce musu zakayi Dr yace kada in ringa yawo har saina haihu shi kadaine shawara AJ yace uhm Allah yasa mami kada tace zata zo dan abba suna da meeting next week !
Zuly tace baby ina ga kawai kace ina US naje ganin Dr !

haka rayuwa yaketa tafia dan cikin pinky har yashiga na wata 8 kayan baby tun daga dubai akayi order dinsu hade da kayan maman daza tayi fitan suna dan cen gidan suma cemusu tayi suna US .
saidai tunda cikin yashiga na wata 8 pinky batada sukuni dan yau lafia gobe ciwo kuma kullin sai sunyi waya dasu leema tunda mama magajia tace baza su zoba Kuma a yan kwanakin nan ne AJ ya baza hotunan pinky da take jariria a duk wani gidan TV na Nigeria Dan samo mata iyayenta!

Dakyar ta tashi daga kan kujeran da take sabida nauyin da cikin yamata daidai lokacin AJ yashugo dakin Tana ganinshi tasakar mai harara dan haushin shi takeji daga shi har matar shi murmushi yasaki hade dacewa maman twins hararar shi takumayi tace

indai yan biyune wlhi saidai afasa haihuwan Daria yayi dinning taje tadauko abu sannan tadawo tazauna shima zaman yayi tace har yanzu banji kana maganan ganin iyayena ba AJ yace insha Allah kin kusa haduwa dasu Dan harda phone number na nabada insha Allah zaa dace yanzu dai tashi zakiyi mufara zagaye gidan nan waro idanuwa tayi tace wallahi captain bazan iyaba ko tausayina bakaji bakaga yanda kafana ya kumbura bane daga ta ma dakyar nakeyi.
[10/14, 17:39] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 48

zay Kuma magana kenan wayarshi tafara ruri daukar wayar yayi hade dakai wayar kunnanshi !

Sallama yayi dagacen kuma aka amsan sallaman hade dacewa sunana sadiq Hashim ruma .

AJ yace eyya gashi bangane kaba dagacen sadiq ruma yace da dai zamu hadu inaga zayfi Dan akan yarinyan da ake cigiyar iyayen tane dasauri AJ yace a ina yakamata muhadu danni yanzu haka ina Lagos dagacen sadiq ruma yace ni ina abuja amma inaga gobe zan taho Lagos sabida ina son haduwa dakai OK AJ yace sannan yamai kwatancen inda zay same shi zuwa goben .

Suna gama wayan AJ yakalli pinky fuskan shi dauke da murmushi yace inaga anfara samun nasara nan dai yagaya mata yanda sukayi da mutumin daya kirashi awaya.

Farin cikine ya lullube ma pinky zuciya dan bata masan sanda tasaki murmushi ba !

Mikewa tsaye AJ yayi yace sai kita addua Allah yasa daya daga cikin yan uwan kine murmushi pinky tasaka hade dacewa naji ajikina gab nake da haduwa da iyayena duk da sun aikata babban laifi a gareni !

AJ girgiza mata kai yayi yace kokin hadu da iyayenki dole kibasu uzuri dole akwai dalilin dayasa suka yarda ke dan babu yanda zaayi uwa tahaifi da dakanta sannan ta yarda shi nizan tafi dafatan zaki chanza shawara Dan iyaye iyaye ne Sun wuce duk yanda kike tunani yana gama fadin haka yawucee yabar parlorn hade dakarasawa bakin motarshi yashiga yabar haraban cikin !

tunda yafara tafia tunanin pinky yakeyi dan yasan gab suke da rabuwa da juna duk sai yaji zuciyarshi bata mai dadi sam a haka yakarasa gida yana parking zuly tafito da saurinta ta tareshi kamar yanda tasaba hade da shigewa jikinshi shikuma yadauketa cak suka wuce parlor saida sukaje har tsakiyan parlour Sannan yadireta yana mata cakulkuli ita Kuma tana daria Tana shigewa kirjin shi saida suka gaji sannan suka zube akan kujera !

Zuly tace baby ya farida fah dazu sai tausayi take ta bani dan tun jia daka gaya mun yanda takoma duk sai naji babu dadi kaman mun zalunceta ko baby shuru yayi hade da rumgomota jikinshi yace zulaiha babu wani zaluntan ta damukayi tunda da yarda ta komi yafaru !

zuly tace amma duk da haka ni har tunanin abunda zan saka mata dashi nakeyi

murmushi AJ yasaki yace kibari harta haifan mana abunda ke cikinta sai kifara tunanin abunda zaki mata .

Zuly tace kuma fah hakane Allah dai yasauketa lafia yanzu dai tashi muje inyi serving dinka danyau zagewa nayi nama girki dakaina amma fa da taimakon kuku daria AJ yayi yace Allah yasa dai yayi dadi turo baki tayi irin shagwaban nan tace koma bayyi dadiba nadaiyi kokari tunda sabida kai nafara shiga kitchen Jan hannunta yayi yace ai koma bayyi dadiba yayi dadi suna karasawa dinning yaja mata kujera tazauna sannan yace dakaina zanyi serving namu sha zamanki kihuta murmushi tasaki harya zuba musu white rice and stew hade da ferfesun kaji dansai Zuba kamshi sukeyi atare sukaci abincin har suka gama AJ yace baga shiba yayi dadi haka nan zaki ringa dafa mun ina ci !

ranan dai in takaici maku zuly da AJ sunsha soyayya duk da daman mutanan kullin cikin soyewa suke washe gari dawuri zuly ta tashi tashiga kitchen kuku yana nuna mata harta gama hada abun break din sannan takaisu dinning tajera komai daidai lokacin AJ yafito daga bedroom yana waya yana gamawa yakarasa dinning din yaja kujera yazauna serving dinsu tayi soyayyen dankali ne da ferfesun kifi.
Suna gamawa tarakashi har bakin mota saida taga yatafi sannan takoma cikin gida !

kai tsaye office yawuce sai zuwa karfe biyu kiran sadiq ruma yashugo wayarshi dasauri yadauka hade damai kwatancen gidan pinky suna gama waya yayi saurin hada komi nashi yabar office din Kai tsaye gidan pinky yawuce Dan kusan atare suka isa shida sadiq ruma AJ yana ganinshi yaga tsantsar kamannin da sukayi da pinky dasauri yafito daga motar shima sadiq fitowa yayi suka gaisa cikin tsakin fuska sannan AJ yace mukarasa daga ciki har cikin parlour Suka shiga Saidai basu tadda pinky ba har AJ yatashi zay Kirata tafito daga daki tana tafia dakyar suna hada ido da sadiq ruma gabanta yayi wani mummunan faduwa shima hakan ta kasance a gareshi karasawa tayi tagaidashi sannan tasamu gu tazauna !
AJ kallonshi yayi yace meye tsakaninka da yarinyan da kaga gani a news dogon ajiyar zuciya sadiq yasaki yace kanwa tace uwa daya uba daya Dan yanzu haka inada hoton ta ranan da aka haifeta aka daukemu hoton mubiyu hannunshi yasaka cikin aljihun shi yacuro hoton yamika ma AJ shikuma yamika ma pinky da tuni tafara hawaye tana ganin hoton tafashe dakuka tace yaya shima tashi yayi dasauri yakarasa kusa da ita suka fashe da kuka !
[10/14, 18:07] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 49
saida sukayi mai isar su sannan sukayi shuru dan kansu sadiq ruma kallon AJ yayi yace badai kai bane mijinta kallon juna pinky da AJ suka yi irin na marasa gaskiyan nan sannan daga baya AJ ya girgiza kai yace ba matata bace kallon rashin fahimta yama AJ yace bangane ba matar ka bace gashi Kuma naganta harda ciki rasa bakin magana sukayi dan basusan me zasu ceba .
saida yakara magana sannan AJ dakyar yace ba matata bace sadiq ruma yace toh ina mijin nata hawaye sosai pinky takeyi AJ yace batada miji bude baki sadiq ruma yayi AJ

yace ina son kazauna ka fahimceni komawa sadiq yayi yazauna sannan yace ina jinka labarin haduwar su da pinky yabashi har izuwa yanzu mikewa tsaye sadiq yayi yace sam bazay Taba yuyuba haka kawai kabata ma kanwata rayuwa wato kai matarka tahuta kanwa ta Kuma ta wahala dole ma su abba suji wannan maganar kuma yau zamu koma Abuja tare da little a razane pinky da AJ suka kalli juna pinky zatayi magana kenan sadiq yace little kada kice komai yau zaki bar garin nan Kuma dole adau babban mataki Dan bazaka batawa kanwata rayuwa ba yana gama fadin haka yacema pinky ta tashi taje tashirya tazo sutafi .

kuka tafashe dashi tace yaya wallahi kafana ko iya dagata banyi Dan Allah kayi hakuri har in haifa abunda ke cikina sai intafi girgiza kai yace bazay yuyuba AJ yace Dan Allah katsaya ka fahimce ni baana son kowa yasan wannan maganar murmushin takaici sadiq yasaki yace bazay yuyuba koda nabar little anan dole fa sai magabata Sun sani dan haka yau zankira su ammi da abba ingaya masu komai .

Shuru pinky tayi taci gaba dakuka AJ kam rasa abunda zayce yayi dakyar ya iya bude bakinshi yace idan mr president yasani zay dauki fushi dani kallonshi sadiq yayi yace dole kam yasani Dan yazama dole ka auri little mikewa tsaye AJ yayi pinky Kuma shi take kallo yanda taga hankalinshi gabaki daya yatashi .

Kafin sukuma magana har Yakira iyayensu yamusu bayanin komai hade dacewa Dan gidan Mr president ne dagacen abba yace yanzu zankira shi inmai bayani kar kuma kama ammin ku magana dan nafison sai zuwa gobe idan anhadu ayi maganar gaba daya kuma ka tabbatar kataho da farida gida gobe suna gama wayan sadiq yace bazan bar little anan ba har AJ zayyi magana wayarshi tayi ruri hannunshi yakai yadauka yaga abban shine tuni hankalinshi yatashi saidai babu yanda zayyi haka nan yadauka .

Dagacen kuwa Mr president rufeshi da fada yayi hade dacewa ya tabbatar Sun taho abuja gobe shida zuly baijira cewar shiba yakashe wayan.

hankalinshi atashe yayi saurin fita daga parlorn yawuce yashiga motarshi yabar gidan
[10/14, 19:08] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 50

yana barin gidan sadiq yace kidaina kuka komi yazo karshe daga mai kai tayi alama toh sannan suka Fara hira duk da rabin hankalinta yana wajen tunanin AJ.

Dakarfi yake horn dagudu megadi yaje yabude mai gate din yana parkin zuly tafito zata tareshi taga fuskanshi a daure gakuma alamar damuwa a tattare dashi haka nandai takarasa tayi hugging dinshi tureta yayi ajikinshi yayi saurin shigewa parlour Bin bayanshi tayi dasauri hankalinta tashe tace baby meke faruwa banza da ita yayi sannan yawuce bedroom itama bedroom din tabishi tana kuma tabbayar shi abunda yafaru da yaga zata matsa Maine yace zulaiha Dan Allah kyaleni kije dakinki gobe idan Allah yakaimu zakiji komai jikinta duk yagama mutuwa tafice daga dakin.

Washe gari kamar yanda sadiq yace karfe sha daya yazo yadauki pinky hade da kayanta tunda private jet zasu hau zuwa abuja karfe daya yamusu a Abuja suna sauka

driver yazo yadauke su a bangaren su AJ kuma sai sha biyu suka isa airport hankalinshi gabaki daya baya tattare dashi Dan dakyar ma yake bama zuly amsa idan tamai magana.
Sadiq abba yakira yace su hadu a gidan Mr president shima AJ kai tsaye gida suka wuce zuly kam hankalinta yafara tashi gashi babu daman ta tabbaye shi wani abu suna shiga gidan ba da jimawa ba su AJ suma suka shugo.
dakyar pinky take tafia har suka karasa bangaren mami parlorn cike yake da mutane saidai gabaki dayansu bakin fuskoki pinky tagani cikin dake gabanta kowa yabi dakallo samun waje sukayi suka zauna dan pinky dakyar ma ta iya zama suma bayan shugowan su zuly samun waje sukayi suka zauna.

Sannan aka gaigaisa Mr president ne yakai dubanshi gun AJ yace alamin yi bayani muna sauraron ka AJ bayani yafara yi tunda ga haduwar su da pinky har izuwa yanzu sadiq yana hawaye yace ammi abba ga little kuna kallo a gabanku ammi dasauri ta taso tarumgume pinky tana kuka itama pinky kukan takeyi saida sukayi me isar su sannan Mr president yayi gyaran murya yakalli AJ yace alamin dole Kayi hakuri ka auri yarinyan nan wani zufa ne yaketo ma AJ saidai baida daman musa ma abban shi zuly kam hankalinta In yayi dubu yatashi balantana da tagama jin labarin pinky .

Pinky ce ta dago da fuskanta tace Dan Allah kuyi hakuri kada ku hada auren nan Dan bamu Taba son juna ba dakatar da ita sadiq yayi yace dole fa ya aureki Dan baza kiyi wahala a banza ba ahe kuka tafashe dashi .
Abban tane yayi gyaran murya yace farida kiyi shuru yanzu sadiq kutashi mutafi gida idan munje cen akira ita magajia muji ta bakinta mikewa sukayi hade dayin sallama dasu mami Mr president kuma yakara basu hakuri sannan sukabar gidan a hanya sadiq yasa pinky takira leema tabashi yabata address din gidansu.
zone ii suka nufa wani katafaran gida suka dosa sukayi horn gate man yabude musu gate din suka shiga cikin haraban gidan suna parkin ammi tafito dasauri takarasa bangaren da pinky take tariketa sukayi cikin gida su abba kuma sukabi bayansu har zuwa cikin katafaran parlorn .
Daya daga cikin kujerun parlorn ammi takai pinky tazauna hade damata sannu abba dasauri yakarasa kusa da ita shima yana mata sannu sadiq kuma fridge yanufa yadauko mata ruwa yakawo mata shima yana binta dasannu tarairayanta kawai sukeyi sannan daga bisani ammi dakanta ta taimaka ma pinky suka je bedroom din ammi din .
Dan tasamu tadan huta !

suna fita Mr president yahau AJ dafada yace tayayaa zakuyi abu batare da kun nemi shawaran muba hakuri AJ yafara bashi Mr president yace kuma auren ka da yar wajen ruma babu fashi yana gama fadan haka yatashi yabar parlorn mami ma tashi tayi dan bazata goyi bayan danta ba kuka zuly tafashe dashi wani mugun kallo AJ yawatsa mata hade da tashi yabar parlon yawuce sashin shi itama tashi tayi tabi bayanshi !
[10/14, 19:56] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

pinky tana kwanciya bacci yayi awan gaba da ita Dan akwai gajia sosai a tattere da ita tun kafin ta tashi ammi dakanta tashiga kitchen ta dafa mata abunda zataci .

Tana gamawa tasamu su abba a parlor suna tattaunawa saidai duk akan maganar pinky ne waje itama tasamu tazauna abba yace nakira su yaya nasan zuwa anjima zasu taho ammi tace uhm ni rayuwar nan tsoro yake bani tunani na har yakare amma har yanzu banyi tunanin wanda yayi sanadin bacewar little ba abba yace ai mugu baida kama Allah dai yatoni asirin koma waye ya aikata hakan ameen suka amsa dashi .
Sannan ammi tamike tace sadiq kaje kataho dasu hajara tunda yanzu dai kahuta murmushi yayi hade dacewa ammi tun dazu sukace zasu taho inaga ta Tsaya dauko anwar ne a skull .
daidai lokacin me gadi yayi sallama yace alhaji anyi baki sadiq yace suwaye megadi yace wata yar dattijuwa tare dawata yarinya dasauri abba yace kashugo dasu .
Koda ammi tashiga Dakinta harta tadda pinky ta tashi daga baccin murmushi tasakar mata tace little tashi kiyi wanka ko zakiji dadin jikin ki pinky shagwabe fuska tayi tace ammi kafana ciwo sukeyi dan dakyar ma nake iya dagasu da anbar Wankan nan zuwa anjima murmushi ammi tayi hade da karasawa kan gadon tazauna tariko hannun pinky tana hawaye tace da harmun cire rai da ganinki farida Allah ya isar mana dan duk wanda yake da hannu awajen saceki Allah bazay barshi ba kuka pinky tafara yi hade da kwantawa ajikin ammi tace yanzu babu wanda zay iya aurena a yanda nake ammi nidin fa ammi karuwa ce duk da wacce ta rikeni bataso in taso a yanda nagan Taba gashi su abba suna neman hada aurena da captain alhalin nasan cutar dashi akayi Dan nidin ammi saurin rufe mata baki ammi tayi tana girgiza mata kai tace kada inkuma jin kin kira kanki da karuwa Dan duk wanda yakalli faridana yasan macece Kamila kuka pinky tafashe dashi hade dakara shigewa jikin ammi sadiq ne yashugo dakin da sallaman shi yace aa ammi da yar autar ta badai ciki zaki komaba murmushi pinky tasaki ammi tace inta koma cikinma ba laifi bane daria sadiq yayi yace marikiyan little ce tazo dasauri pinky ta daga kanta daga jikin ammi tace Allah sarki mama .
Ammi kinsan mama tasoni fiye da kowa tasani a islamia da Boko tun ina karama saida nagama ss3 ne naga hidima yana ma mama yawa shiyasa kawai nafada har ...
Dasauri sadiq yarufe mata baki hade dasanya hannunshi yana share mata hawayen dake zubowa a idonta ammi tace nagaya maki kidaina kiran kanki da sunan da bai dace dakeba maza tashi muje bathroom in wanke maki fuska daria pinky tayi tace Kai ammi sai kace wata yarinya sadiq yace toke mecece inba yarinyan ba Daria tayi hade da tashi tawuce bathroom ammi tabita dakallo duk sai taji tausayin yar tata yakamata sadiq shi kanshi tausayin pinky saida yakama shi fita yayi daga dakin hade dacewa ammi ku ake jira!

Tana wanke fuskan ta tafito ammi takalleta tace kada inkuma ganin hawaye a idonki Dan yanzu yin hawaye yakare murmushi pinky tayi a zuciyar tako godiya tama Allah daya

hadata da iyayenta masu sonta.
Rike mata hannu ammi tayi sannan suka wuce parlour leema tana ganin pinky tasakar mata murmushi hade da tashi ta tarikota suka karasa suka zauna mama magajia pinky tagaida hade dacewa mamana nayi kewar ki mama magajia murmushi kawai tasaki leema kam da pinky suna manne dajuna .
Mama magajia labarin yanda akayi ta tsinta pinky tabasu hade dacuro Dan karamin diamond din Tamika ma ammi dake hawaye abba shi kanshi saida yayi hawaye.

wani Dan karamin yarone yashugo parlon dagudu yana daddy wajen sadiq yakarasa yahaye jikinshi yana Daria yana nuna kofa ammi tace ina ka bar maman taka .
daidai lokacin hajara tashugo parlorn da sallama fuskanta dauke da murmushi gaida kowa tayi hade dakallon ammi tace ammi ina little din take anan nuna mata pinky tayi tashi hajara tayi takarasa ta rumgume pinky hade dakallon sadiq tace gadai little kinga yayan nan naki kullin sai yayi maganarki murmushi pinky tasaki .
[10/15, 12:11] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 52

sadiq yace she's my half dole kullin inyi maganar little daria pinky tayi tace kai yaya daga mata kai sadiq yayi hade da kallon anwar yace anwar ga second mummy dinka hannu pinky taware tace my boi dagudu yakarasa yafada jikinta ita kuma ta rumgume shi tuni taji son yaron yashigeta .
Ammi ce ta tashi tace little bari inkawo maki abinci kici sadiq yace kai ammi ansamu little kuma Zaa manta dani abba yace kato dakai me kake so ammin naku tamaka pinky tace ato abba gaya maidai hararar wasa sadiq yawatsa mata hade dacewa auren captain dole sannan yamata gwalo hawaye tafara yi takalli abba tace abba kagan shiko ni wallahi banson wannan AJ din leema dasauri tace aa pinky kidai fadi gaskiya duka pinky takaima leema abba yace kunsan Allah idan Baku kyale mun auta ba ni dakune sannan yakalli pinky yace rabu dasu babu wanda zay takura maki akan auren wanda baki so .
Daria akayi duka parlon ammi ce takaraso rike da katon trey tace hajara kuje dinning akwai abinci kizuba masu Dan ni yau dakaina zan bawa little abinci mikewa sukayi hade dayin daria yarage daga little sai ammi a parlorn ammi dakanta taringa bama pinky abinci har takoshi sannan tamika mata ruwa tasha tace saiki huta kiyi wanka turo baki pinky tayi tace wlhi ammi wankane ban iyawa yanzu da dai abari sai dare nayi sai inkwanta gaba daya.

Abangaren AJ kam yana shiga dakinshi yazube akan kujera yana fitar da wani iska me zafi zuly ce takaraso inda yake tasamu gu tazauna zata fara magana kenan yayi saurin daga mata hannu hade dacewa ki koma bangaren Mami bana son surutu .
Girgiza mai kai tayi tace ka tsaya ka saurareni batare data bari yayi magana ba tace hukuncin da abba ya yanke yayi daidai Allah yasa hakan shi yafi zama mafi alkhairi yakuma baka ikon kyautata mana tuni AJ yaji jikinshi yayi sanyi tabbas yasan zuly macece

me hankali da  hangen nesa  baisan sanda  yajawo  ta  jikin shiba  yace  Aameen  wifey yhu r too much  Allah  yabar  mu tare  murmushi  tasakar mai  hade dacewa  Aameen.

Sannan  tamike  tace  oya  tashi  muje  muyi wanka  sai  muzo  muci abinci hannunta  Tamika mai  shikuma yasaka hannunshi  anata  yajanyota  tafada jikinshi  yashiga  kissing  dinta  daga nan  kuma sai  zance  yachanza  Dan  AJ ba  baya ba  wajen  bukata.

Ammi  tace  gidan da  aka baki  kyauta  mamanki yakamata kibawa kyautar shi  murmushi pinky  tasaki tace  Ammi ai  tuni nagama tsara  hakan  a raina  saidai dole sai  ansamu me  aiki .

Suna  cikin  magana  leema  tashugo  parlon  tace  Ammi  zamu  tafi mama ta matsa  Ammi tace  ahaba  ai  yau nan zaku  kwana bari  intashi inje in Sameta tashi  ammi tayi Tabar parlon leema  kuma  tazauna tana  fuskantan  pinky  tace  naji  dadi  sosai da Allah  ya hadaki da iyayenki  bazance captain  AJ bayyi  kokari ba  yayi kokari sosai tunda ta  dalilinshi  kika  hadu da  iyayenki  fatana kawai  ki  yarda da  hukuncin da aka yanke  akan  hada aurenku da  captain .

Murmushi  pinky  tasaki  hade  dacewa  hmm  yayi kokari kam  Saidai dole zan fuskanci matsala  sabida kinsan  ko waye  AJ leema  tace  zay  Chanza idan  har  kinayin  abunda  yake so  tabe  baki  pinky  tayi tace  yanda yake son  matar nan  nashine zay wani  kulani uhm  .

Happy weekend

Goodnight fan's

[10/15, 20:09] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕

PAGE 53

Ammi  dinning  takarasa  tace  maman  little  aiko  kwana zakuyi  Dan  little  baza  taji  dadin tafiyar  kuba  mama  magajia  tace  toh  shikenan  Tunda kince  haka  .

da  dare  kunsan kwana  su  pinky  sukayi  suna  hira  .

washe  gari  kam  tunda pinky  tayi  sallan  asuba  data koma bacci bata  tashiba  sai sha daya  nasafe dakyar  ta  iya  saukowa daga  kan  gadon  daidai  lokacin ammi  tashugo  dakin tace  little  harkin  tashi  .

Daga  kai  pinky  tayi  hade  dacewa ammi na  ina  kwana  lafia  kalau  ammi  ta amsa  dashi hade  dacewa  bari  in hada  maki  ruwan wanka sai kiyi  breakfast.

Bathroom  ammi  tawuce  tahada ma  pinky  ruwan wanka sannan  tafito  tace  oya  tashi  kije kiyi wankan ko  kyaji dadin  jikinki.

Shagwabe  fuska  pinky  tayi  tace  wlhi ammi  kafana  ciwo take mun  sosai  .

Ammi  tace  inkin  fito wankan  na  gasa  maki  kafan  daman  dole  kiji  haka.

tashi  pinky  tayi  tawuce  bathroom  ta  jima  sosai  tana  gasa  jikinta  sannan  tafito  daure da  tawul  tana  turo  cikin kan  gado  takarasa  tazauna  ammi  tamata  sannu  hade  dacewa ga kaya idan kinshafa  mai  sai  kisa  bari  inje  wajen abbanki  in  bashi  kayan break  .

VILLA

Tunda sukayi sallan asuba sai goma suka tashi daga bacci AJ yadauki zuly yakaita bathroom yace ke zaki mun wanka nikuma namiki daria zuly tayi hade da bubbuga mashi kirji cire mata rigar baccin jikinta yashigayi ita kuma tacire matsa kayan jikinsa suka fadan cikin jacuzzi saida suka sha soyayyan su tunkuna sukayi wanka suka fito kowa shafa ma dan uwanshi mai yayi sannan suka shirya AJ cikin kananun kaya zuly kuma riga da sket tasaka na atamfa suna gama shiryawa suka karasa dinning sukayi Breakfast bayan sungama suka tashi suka wuce bangaren mami da sallama suka shiga parlourn mami tana ganinsu tasaki murmushi zuly a kunyace tagaida mami hade dasamun waje tazauna AJ kuma shafa kanshi yayi hade dacewa mami ina kwana antashi lafia Lafia kalau ta amsa dashi sannan tace tun dazu abbanku ke jiran ka gashi harya fita .

cikin kwanakin da pinky tayi agidan su tasan cewa babu abunda yakai iyaye dadi sabida duk abunda take bukata ana mata Dan kusan kullin sadiq da anwar da maman shi suna gidan su ammi .

mama magajia da leema Kuma suna maitama gidan da minister yabama pinky duk da itama leema kullin tana hanyar zuwa gidan su pinky.

Dayake yanzu ciikin pinky yashiga na wata tara ranan haihuwa kawai ake jira .

ammi dake gyasa ma pinky kafa da ruwan zafi tace ciki sai kace na yan biyu Daria pinky tayi tace ammi me kika gani ammi tace naga yanda cikin yayi girmane sosai Allah dai yasauke ki lafia kema kihuta Aameen pinky ta amsa dashi.

A bangaren su AJ kam sai shirye shiryen zuwan baby akeyi dan daki na musamman suka ware ma babyn agidansu suka cika shi da Teddy's .

Yauda matsanancin ciwon ciki pinky ta tashi sannan sai wani ruwa dake fitowa ta kasanta ammi ce tashugo dakin taga halin da pinky take dasauri tajuya taje tagaya ma abba shima arude yabiyo bayanta hade da daukan makullin motarshi .

Su biyu suka kamata har wajen mota sannan suka bar gidan asibiti mafi kusa zakuje ansan gaggawa aka mata sabida tafara fita hayacinta ana shigar da ita dakin haihuwan bada jimawa ba Dr din yafito yana share zufa dasauri su abba suka karasa gunshi ammi tace tasauka lafia ko Dr yace lafia lau tasauka saidai baby girl din data samu takoma yanzu zaa kaita dakin hutu yana gama fadan haka yabar wajen .

Abba wayarshi yacuro yakira sadiq yagaya mai hade Dace mai yakira alamin yafada mashi dan susan halin da ake ciki .

dakin da aka kai pinky su ammi suka karasa kwance suka tadda ita saidai idonta biyu dasauri ammi takarasa wajenta tazauna hade dakamo hannunta tace sannu little daga kai pinky tayi hade dacewa ammi ina abunda na haifa badai har captain ya anshi abun shiba girgiza kai ammi tayi tace saidai kuyi hakuri Allah ya amshi abunshi hawaye kawai pinky taji yana zubo mata da batasan dalili ba. Sadiq suna gama waya da abba yakira AJ bugu daya yadauka dan sai wani zumudi yakeyi yana dauka sadiq yagaya mai abunda ke faruwa hade dagaya mai asibitin dasuke zaman dirshan AJ yayi akan kujera hade da dafe kanshi zuly ce tafito daga kitchen rike da trey takarasa inda yake tace baby dagowa yayi yakalleta duk sai yaji tausayinta yakamashi hannunshi yakai yajanyota jikinshi ya rumgume hade da buga mata baya yace wifey kiyi hakuri zuly da bata fahimci komai ba tace baby meke faruwa ne kara matseta yayi ajikinshi sannan cikin sanyin murya yace wifey babyn da muka dadai muna ma tanadi Allah ya amshi abunshi zuly da tagama rikicewa bakinta narawa tace captain bangane abunda kake nufi ba matseta yakara yi sosai yace kiyi hakuri kuka tafashe dashi hade da rike rigan shi sosai tausayin zuly yakama shi dakyar ya lallasheta yace tashirya yakaita gidan su mami shi daga nan sai yawuce asibitin .
[10/15, 22:49] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 54
tun amota take hawaye har suka karasa gidan su mami .
Dan bakaramin sa rai tayi da babyn ba balantana ma idan ta tuno da maganar Dr sai taji zuciyar ta takuma mata ba dadi ahaka suka karasa villa yana kuma tausanta yana ajiyeta yace tashiga shi zayje yadawo .
girgiza mai kai tayi tace kabari inga ko fuskan tane pls captain bakasan halin da nake ciki ba ayanzu tausayin tane yakara kamashi OK kawai ya iya cewa sannan yaja motar suka bar gidan kai tsaye asibitin da sadiq yafada mishi suka Nufa .

dakin da babyn take aka kai zuly tana ganinta tafashe dakuka tafada jikin AJ lallashinta yashiga yi sannan sukabar dakin suka wuce dakin da pinky take pinky tana ganin zuly sai hawaye yafara ambalia akan fuskarta Dan tausayin zuly ne yakamata ammi ce ta tashi ta taro zuly hade daja mata kujera tazauna gaisawa AJ sukayi da ammi sannan suka fita daga dakin Shida sadiq dan zuwa tsitirce jaririyan.

Bayan barin su dakin zuly ta tashi takarasa inda pinky take tazauna hade dakamo hannunta tace nagode sabida da taimakonki naga jinina a dunia nagode sosai farida Dan bansan dawane baki zan iya gode maki ba murmushi pinky tasaki me hade da hawaye .
zuly tace ki taimaka ki yarda da hukuncin dasu abba suka yanke kada kiyi tunanin

wai ko captain mijina ne Dan Allah badan niba ki yarda da auren AJ.

Ammi dake jin maganan da zuly takeyi tuni taji yarinyan tashiga ranta tashi tayi tafita daga dakin tabasu waje .

Hawaye pinky takeyi sabida bata Taba ganin me kyaun hali irin zuly ba lallai dole ayaba mata .
zuly tace kinyi shuru pinky murmushi tasaki tace nayarda amma badan ina son hada kishi dake ba saidan kin rokeni sosai zuly tayi farin ciki tace nagode !
Allan yabamu hakurin zama da juna Aameen pinky ta amsa dashi .

a haka akayi sadakan bakwai duk da yanzu zuly takwantar da hankalinta saidai tasa tunani sosai a ranta
pinky kam kullin sai ammi tamata wankan jego har nakwana arbain.

dan tadawo yanda take da Dan yanzu har wani kyau takara da haske.
Mr president kam ya dage akan sati me zuwa zaa daura auren AJ da pinky tuni AJ yatada hankalin shi dan shikam harga Allah bai shirya ma auren acikin kwanakin nanba danma zuly tana kara karfafa mai gwuwa akan auren.

Kuka pinky ta tasa su ammi tana musu sadiq dake gefe azaune yace little kiwa Allah kiyi hakuri kiyi shuru ba gwanda andaura auren yanzu ba kihuta wani kukan takuma fashewa dashi abba yace ikon Allah nidai banga aibun alamin ba da kika tasamu agaba kina mana kuka ammi tace aikam alamin baida aibu tunda kowa yabonsa yakeyi kallonsu pinky tayi tace Allah wallahi ammi bakusan muguntan captain bane Daria ma tabasu .
Abba yace toh naji tunda baki sonshi wa kike so tsit tayi tarasa bakin magana dan dai ita ko ada bata Taba son kowa ba .
Abba yace yi magana ina jinki dakyar ta iya bude bakinta tace abba duk wanda kazaban mun ina so amma banda AJ abba yace toh shikenan shidai alamin dinne bakiso daga kai tayi alamar eh abba yace toh shikenan zankira Mr president muyi magana.
Murmushi tasaki hade da mikewa tsaye tace nagode abbana nagode ammi tace yar nema sadiq yace wallahi kada kidawo kina mana kukan wayyo captain kikee so shagwabe fuska tayi kamar me shirin yin kuka tace abba kagan shiko ammi tace yi hakuri kai kuma tashi katafi dare yanayi saida safe.

Daria pinky tayi hade dacewa yaya saida safe kagaida mun da yarona da auntie haja gobe insha allahu zanzo .
Sadiq yace kada insake inga kafarki agidana daria tayi tace nida gidan yayana hararar wasa ya watsa mata sannan yamike yace ammi abba saida safe.

jikinshi sosai tashige tafara mai magana a hankali tace baby ko yar hirar fa baka zuwa tsaki AJ yasaki yace kinsan ko kema ba kasafai nake zuwa zance wajen kiba zuly tace nasani amma ni ai muna da nisa ita kuma farida gari daya kuke yakamata Dan Allah gobe kaje tunda dai kaga su abba sunfara shirye shiryen biki OK yace hade dacewa kedai bansan wace irin mata bace yar aljanna daria tayi tace harka shigar dani kenan daga mata kai yayi hade da hade bakinta da nashi

[10/16, 06:43] saudah: 📚 WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕
PAGE 55

washe gari da yamma pinky tashirya cikin riga da sket na Atamfa Dan yanzu ammi tasaka an dindinka mata kaya English wears dinta saidai tasasu agida.

Kayan bakaramin zauna mata sukayi ajiki ba gakuma wani uban dauri da tasha sosai tayi kyau Dan Rambo color tahada key car dinta tadauka tafito daga dakin ammi ta tadda aparlor Itada wainsu baki gaidasu tayi sannan tace ammi na zanje gidan yaya ammi dagowa tayi takalleta tace adawo lafia kigaida mun da hajara kuma karki kai dare .
Insha Allah pinky tace sannan tafice daga parlourn kai tsaye parking space tanufa tama motar ta key har zata tada motan taga bakuwar mota tashugo gidan hakan yasata tsayawa .

Har wajen da ake parkin yakarasa yayi parkin sannan yabude murfin motan yafito manyan kayane ajikin shi maroon color yayi kyau sosai suna hada ido duk zuciyoyinsu saida suka buga .
Kokarin tada motar takeyi AJ yakarasa dasauri yasanya hannunshi yacire key car din.

Hararar shi tayi tace meye haka shima hararan nata yayi hade dacewa ina zakije uwar son yawo kallonshi tayi sannan tace inda ka aike ni nikawai kabani mukullin motata .

AJ yace naki na karfine murguda mai baki tayi hade dacewa nifa shishigine bana so kuma tunda yauba nasha gaya maka AJ yace kwana nan nan zanyi maganin bakin rashin kunyan nan .
Dan haka idan har kina son fita dole saikin gayamun inda zakije juyar da kanta tayi sannan tace gidan yaya zani oya bani key car na murmushi yasaki sannan yace bari ingaida ammi infito sai in kaiki har yafara tafia pinky tace ammi natare da baki juyowa yayi yace ok fito mutafi badan tasoba haka nan tafito daga motar ta tawuce tashiga motar shi shima yashiga yatada motar sukabar haraban cikin gidan saida sukayi tafia me nisa sannan AJ yadan Kalli pinky tagefen ido yace dakin daina yawan sa turaren nan Dan baida amfani Mace tawani feshe jikinta da turare in zata fita .
Banza pinky tamai wayar ta dake cikin handbag dintane yayi ruri hannunta takai tazage zip din jakan sannan tadauki wayar Dan har saida gabanta yafadi da taga me kiran nata Dan harga Allah batason yin magana ko haduwa da duk wani abokin harkanta ada barin wayan tayi yaci gaba da ringing .

AJ yace  wannan  karar wayar taki ta  dameni  In baza kiyi  picking ba  toh gwanda kisashi  a silent. Yana  rufe  bakinshi  aka Kuma kiran  wayar kuma duk  mutum  dayane  tsaki  taja  hade da daura wayar akan  cinyarta yaci  gaba da  ringing shi Kadai .

AJ hannunshi  yakai  kan  cinyarta  yadauki  wayar  sunan  minister  yagani akan screen  din baisan sanda  yasaki  tsaki ba  hade  da  kashe  wayan  gaba  daya  pinky  tace  meye nadaukar mun  waya banza  yamata  sannan  yafaka  motar abakin  hanyan yabude  wayar yacuro SIM  din  yakarya hade  da  watsi dashi awaje  kallonshi  takeyi cike da mamaki  tace kasan Allah bazay yuyuba saika  biyani  SIM dina  Kaiba mijina ba  kuma kaiba aurenka zanyi ba  amma  kawani  karya  mun SIM  dogon tsaki  captain  yasaki yace wayar ma  bazan  baki ba Dan na fahimci haryau bakiyi  hankaliba yana  gama  fadan  haka  yatada  motar sukabar wajen  juyar da  kanta  tayi  gefe Tana  ta  kumbure  kumbure  har  suka  karasa  gidan  sadiq abakin gate sukayi  horn megadi  yawangale masu  gate suka  shiga samun waje  yayi  yafaka motar  hade  dacewa  idan kingama ki amshi wayan  sadiq ki  kirani  banza  tamai takai hannunta tabude  murfin motan  tafita tana  kumbure  kumbure  sadiq ne  yafito  daga  parlour AJ yana  ganinshi  yasauko  yakarasa suka  gaisa  hade  dacewa  idan  pinky zata  tafi yakirashi zay dawo yadauketa  harararshi pinky  tayi tace  wallahi nagama  shiga motarka batare daya  ce mata  komaiba  yama sadiq sallama  yashiga  motarshi yatafi.

Atare  suka  shiga  parlorn  anwar dake wasa  yana  ganin  pinky  yatashi dagudu yana oyoyo mummy ita kuma taware  hannayenta  tana my boi oyoyo fadawa  jikinta  yayi  ita  kuma tadaukeshi  suka  karasa  cikin  parlorn  tasamu gu  tazauna  hade dacewa auntie  ina  wuni hajara  tace  lafia kalau  Ashe dagaske  dai  zakizo  sadiq  yace  aikuwa  gata  tazo Dan  abokin fadan tanema  yakawo ta  Daria  auntie  hajara tayi  tace amma  little bakida kirki ko kice yashugo  turo baki  pinky tayi  tace  ni  wallahi bama dason  raina  yakawo niba  takura mun yayi  kuma yama  riga  yawuce  ai  sadiq  yace ai Zay dawo anjima  sai kiyi  girki dashi  pinky tace  wlhi nidai  nikadai  zankoma tunda ba  aurena yakeyi ba  balantana  yaringa  shiga harkata.

Good morning fan's

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [11:02 ,10/16]

PAGE 56

Mikewa  tsaye  pinky  tayi  tace  auntie  me kika  tanadar  mun auntie  hajara  tace  pancakes nayi  da  donut sugar.

rike hannun  anwar  tayi  suka  wuce  kitchen  .

bayan  magrib  sadiq  yakira  AJ awaya aiko baa  jima ba  sai  gashi  har  cikin  parlor  sadiq yakaishi  shikuma  sadiq  yakarasa  dakin  hajara  yakirata  sannan  yace  little  kishirya  kizo kutafi waro  idanuwa  tayi  tace  yaya  fisabillahi  yanzu saida kakira bakin  mugun nan   hararar wasa  yawatsa  mata  hade  dacewa  kinsan dai  in baki  bishiba niba kaiki gida zanyi ba  kuma ammi  takirani  tace  leema nagida  tana  jiranki  wai  takira wayarki akashe  kara  turo baki  tayi tace badole  aji wayata akashe ba  tunda  Dan  iko yakarya  SIM  din  ai  wallahi saiya biyani

danba yarda zanyi ba auntie hajara da sadiq daria sukayi hajara tace kiwa Allah kada kimai rashin kunya kinsan dai kubiyu Zaku tafi sai kibishi a hankali mikewa pinky tayi hade da yafa gyalenta tadauki handbag dinta tayi waje dasauri hajara ta tashi tace little rigima bayan Sun gaisa da auntie hajara ne suka rakasu har wajen mota suka tafi .
Juyawa AJ yayi yadan Kalli pinky yace baki iya gaisuwa ba kenan naga alaman sai ammaida ke islamia turo baki tayi hade dacewa wallahi nidin ba jahila bace dan kabar ganina haka haddar AL Qur'ani ne akaina murmushi AJ yayi hade da girgiza kanshi yace Ashe kinsani kike take sani aiko me ilimi bazayyi abunda kika aikata ba .

Banza tamai Dan tasan tabiye mai zay iya bata mata zuciya shikuma har cikin zuciyarshi takalarta fada yakeson yayi amma tayi banza dashi saida suka kusa da gidan su pinky yace dazu abba yagaya mun wai bazaki aure niba babu damuwa daman ni zuly ta isheni .

Dan daman kedin sai daidai dake .
soya shirye shiryen biki hararar shi pinky tayi tace ba matsalar ka bace daria yayi yace OK ba Matsala ta bace kam .
Suna zuwa bakin gate yayi horn megadi yawangale masu gate din suka shiga yana parkin pinky tayi saurin bude murfin mota tasauka hade dacewa mugu dai baiji dadin halin saba zuly Tana fama dakai Tana gama fadan haka tayi saurin shigewa parlour murmushi yasaki hade da girgiza kai.
tana shiga parlor tazube akan kujera tana maida numfashi ammi tace ke lafiyanki kuwa girgiza kai pinky tayi tace wallahi ammi ki kira captain kigaya mai yakawo mun wayata ammi tace garin yaya wayarki taje hannunshi turo baki pinky tayi tace shiya kaini gidan yaya amma bada son raina nabishi ba murmushi ammi tayi hade dacewa tsakanin kune ni meye nawa aciki kitashi kije leema tana dakinki tana jiranki daukar handbag dinta tayi tawuce tana kara cewa wlhi ammi kigaya mai yakawo mun wayata?

su mimi cikin satin da muke suka dawo daga skull
kuma sosai suka ji dadin auren pinky da AJ Dan sudai daman suna sonsu tare.

mami kam kamar wancen lokacin komi nakayan lefe dana gani inaso duk a Dubai tasa akayi order dinsu .
zuly kam ana kano Dan AJ dakanshi yakaita kano taje tagaida su hajia .

hajiyan zuly saida tagama jin labarin komai sannan tace zancen banza kenan ina gadai zulaiha keba Mace bace tayaya Mace dake zakice wai kina son mijinki ya kara aure auren ma kuma karuwa zuly dai ita dukar da kanta tayi batace komai ba Dan batada abun cewa hajia tace toh bazan bari ina gani ahada yata kishi da karuwa ba sam baki gado hali naba .
Inbanda rashin hankali irin naki ina kika Taba ganin mata tabawa mijinta goyan bayan kara aure mtsw ni tashi kiban waje mara hankali kawai .
Hawaye zuly tafara yi tace hajia dalilin farida fa naga jinina adunia.

hajia tace ke gafara cen ina maki gata kina iskanci zuly tace nidai hajia bana son kiyi komai adduar kawai zaki mana Allah yahada kanmu tabe baki hajia tayi tace naji .

ammi tun daga maiduguri ta dauko me gyaran jiki kada kuso kuga yanda pinky takara kyau fatar nan tata tayi fess sai kace fatar jarirai .
Magungunan mata kuwa dana gyaran HQ tun daga sokoto ammi tasa aka hado magunguna .

duk da har yanzu pinky batasan wanda abbanta yazaba mata ba amma tasa a ranta koma wanene zata zauna dashi tunda yanzu ta fahimci mutuncin mace dakin mijinta .

Ammi fridge taje tadauko magani ta dawo tamika ma pinky dake zaban wainsu materials yamutse fuska pinky tayi tace kai ammi wlhi maganin nan dacin balai ne dashi hararar ta ammi tayi tace ni ansa gata nake maki maza kishanye sannan takalli leema da faiza tace akwai kayan daza akawo anjima leema sai kije ki anso zanbaki address din Faiza ke kuma kibiyoni daki tashi Faiza tayi tabi bayan ammi pinky tace sai wani maganin mata ake bani alhalin ko mijin dazan Aura bantaba gani ba daria leema tayi tace badai kinbarwa abba zabi ba nasan captain yanacen shida matar shi suna shan soyayya tuni pinky taji zuciyarta namata wani zafi .

Yauda yamma aka kawo kayan lefe dozen goma sha biyu kuma ko wanne cike yake da kaya masu sadan gaske da motar da aka kawo lefen har da ita duk na amarya ne .

pinky data gama kallon kayan tace wane irin mijine abba yazaba mun haka me kudin gaske wani lefene harda sabuwar mota faiza tace koma wanene ranan daurin aure kya ganshi ni bari intashi inshirya Dan teddy yana kan hanya pinky tace toh sannu uwar son miji nima dai nakusa auren nan nafara shan soyayya leema tace idan kuma tsohone yaza kiyi tsit pinky tayi Dan babu abunda ta tsana sama da ache ta auri wani tsoho .

a bangaren su AJ kam shiri sosai akeyi duk da bawani events zaayi ba walima kawai zaayi duk wainsu frnds dinshi dana waje dana gida saida yakai musu IV.

Faisal dake kan bayan mota a zaune yace Allah Yakama ka AJ yace yakamani ame Daria Faisal yayi yace gashi tun baaje ko ina ba Zaka kara aure kuma ma da crush dinka tsaki AJ yaja yace kaidai banza ne ai gwanda ni namayi auren kaifa haryau bakayi ba kazama tuzuru Daria Faisal yayi yace gab nake da aure insha Allahu .

AJ motar shi yama key yashiga yace nina tafi Faisal yace OK sai mun hadu ranan daurin aure .
Jan motarshi AJ yayi yabar gidan kai tsaye gida yawuce zaune ya tadda zuly dasu mimi suna ganin dinkunan dasuka anso awajen tailor zuly tana ganinshi tasaki murmushi tace baby sannu da zuwa yauwa yace sannan su mimi ma suka mai sannu zama yayi akan kujera su mimi tashi sukayi suka wuce upstairs .
Zuly karasawa tayi tafada jikin AJ tace baby Kasha wuya ko murmushi yasaki hade dasa hannunshi acikin gashin kanta yace ina sonki dayawa wifey Allah yabar mu tare ke wata bangare ce tajiki na sabida kedin Mace tagari ce murmushi zuly tasaki tace nagode sosai baby da yabawarka .
WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [13:04 ,10/16]
PAGE 58

Ranar sati dinbin jama'a suka sheda auren captain alamin junaid da amaryar sa farida tahir ruma.
Inda yatara manya manyan jiga jigan Nigeria dama na kasashen waje duk wani meji dakudi a Nigeria saida ya halalci bikin mutanan biki me cike da din bun tarihi .

AJ sai gaisawa da mutane yakeyi ana tayashi murna .
Leema ce tashugo dakin da pinky take tare da kawayenta tace Masha Allah an daura gaban pinky ne yawani fadi batasan sanda tafashe da kuka ba tafara tunanin AJ tuni taji tana son kara sashi a idonta kafin akaita gidan mijinta .
Ammi ce tashugo dakin tace leema kushirya ta yanzu ango zasu iso dashi da abokanan shi toh leema tace hade da fara buda tana rera wakar amarya haushi ne yakama pinky faiza tace amarya menene na kuka tunda an riga da andaura banza dasu tayi sannan leema Tamika mata wani leshi tace gashi kisa ansa pinky tayi tasaka kayan aiko sosai suka zauna mata ajiki sai sheki ko takeyi mamz ce ta zauna ta tsantsara mata kwalliya tuni pinky tachanza kamanni takuma kara kyau saida aka gama mata kwalliyan aka shiryata tsaf sannan auntie hajara tashugo tace frnds din groom fa sunzo suna falon abba .
tashi sukayi dikansu suka tsanya pinky a tsakiya hade da rufe mata kanta dawani gyale kalar leshin .
Falon abba suka nufa abakin kofan sukayi sallama abokanan ango suka amsa suka zuba ma kawayen amarya ido Faisal kam idonshi nakan leema tun da suka shugo kujera daban suka zaunar da pinky sannan suka gaggaisa da abokanan ango Faisal ne yafara mikewa tsaye yace toh sai abar amarya da angonta su gana tuni gaban pinky yakara fadi dan tana ta fargaban ganin angon nata .
Fita sukayi suna tsokanan pinky bayan fitan sune palon yadauki shuru zuwa na yan mintuna sannan daga baya AJ dake tsanye dawata dakakkiyar shadda fara yayi gyaran murya yace amarya kinsha kamshi gaban tane yafadi hade dakai hannunta ta yaye gyalen da aka rufeta dashi ido biyu sukayi da AJ dake tsakar mata murmushi mamaki ne Yakama ta tawaro Manya manyan idanuwanta .

AJ yace kina mamaki ne dukar da kanta tayi irin kunyar nan girgiza Kai yayi yace toh kima daina mamaki nine dai mijinki .

Tuni taji zuciyar ta tamata fess farin ciki yakamata tashi yayi tsaye yace inada baki ayi walima lafia Kafin tabude bakinta tace wani abu tuni yafice daga palon murmushi tasaki dan har saida dimple dinta yalosa bayan fitar shine su leema suka shugo dakin pillow tadauka ta wurga ma leema da faiza tace amma bakuda kirki daria sukayi sukace ba laifin mu bane sadiq ne yashugo dakin yace jaira daman nasan kina sonshi murmushi tayi hade da boye kanta a tsakankanin cinyoyinta .

Da yamma aka hada gagarumar walima agidan Mr president zuly kam anci uban kwalliya sai kace itace amaryar fuskar ta dauke da faraa mutane kam sai mamakinta sukeyi bakin ciki kuwa ya ishi yan uwan zuly ganin ko ajikinta ma akan kishiyar da aka kara mata su mimi kam shiryawa sukayi su yo gidan su pinky .

Har dakinta suka shiga suka sameta murmushi tasakar musu mimi tace Wow auntie farida kinga yanda kikayi kyau kuwa sumy tace bari inyi snapping dinta intura ma ya yaganta murmushi pinky tasaki suka ringa daukanta pictures suna tura ma AJ yana bude whatsapp dinshi yaci karo da hotunan pinky da sumy ta turo mai murmushi kawai yayi hade da cigaba da kallon hotunan yaga tawani kara kyau tuni yakosa dare tayi.

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [17:17 ,10/16]

PAGE 59

Gagarumin walima aka hada Dan angayato wata shahararriyar malama kuma sosai tayi tuni akan zaman aure da nasihohi kala kala jikin pinky yayi mugun sanyi .

bayan magrib aka fara shirye shiryen kai amarya gidan ta wani hadaddan orange material pinky tasaka me matukar daukan ido kada kuso kuga yanda kayan yazauna mata tafito cas abunta ga fuskan nan tata sai wal wal takeyi tana kyalkyali duk da bawani makeup sosai aka mata ba

Mota hudu ne kawai suka zo daukan amaryan sabida abba yace basai anje kai wani amarya da mutane dayawa ba .

nasiha sosai ammi tama pinky tuni jikinta yayi sanyi tafara hawaye fadawa jikin ammi tayi tafashe dakuka babbareta akayi daga jikin ammi suka kaita palon abba shima yamata nasiha sosai me shiga jiki sadiq ne yadaga ta yana lallashinta har yakaita bakin mota yasata yayar abba ce dakuma kanuwar ammi suka tsanya pinky a tsakiya Sannan su leema suka hau sauran motocin motar su pinky yafara fita daga gidan Sannan nasu leema tana gaba tare da Faisal sai zuba soyayya sukeyi har suka karasa katafaran ratsassan gidan dake wuse II

a parkin space sukayi parkin sannan suka fito hade da pinky da fuskanta arufe yake part uku ne agidan daya na pinky daya na zuly sannan daya name gidan .

Bangaren ta pinky aka wuce da ita da kafar dama akace tafara shiga dakin hade dayin addua har cikin katafaran bedroom dinta aka nufa da ita su auntie hajara ma nasiha suka kara mata sannan suka tafi suka barta da kawayenta goma daidai abokanan ango dashi kanshi ango suka shuga dakin amarya tsokanar AJ kawai sukeyi balantana Faisal

daya gaji da shakiyancin sune yace muje in rakaku leema da sauran kawayen tashi sukayi sukama pinky sallama a haraban gidan ne AJ dakanshi yacuro bandir din dubu guda uku yamika ma leema yace na tsiyan baki .

Kowa motarshi yashiga yabar Haraban gidan yan uwan zuly suma tuni Sun tafi duk da kowa yatafi da takaicinta .

shafa kanshi yayi hade dasakin murmushi sannan yakoma sashin pinky yanda yabarta haka yadawo yasameta gudundune acikin katon gyalen murmushi yasaki hade da karasawa kan gadon yazauna sannan yakai hannunshi ya yaye gyalen baisan sanda yabude baki yace subhanallah ba hade dakai hannunshi yadago da fuskanta suka fuskanci juna murmushi yasakar mata tuni yaji wani sonta yana ratsa duk wani jijiyoyin jikinshi cikin rikitacciyar muryarshi yace Masha Allah tashi muyi sallah mugode ma Allah daya kawo mu wannan rana .

Kara dukar da kanta pinky tayi bata Ankara ba sai ji tayi ya yaye gabaki daya gyalen hade da daukanta cak yayi bathroom da ita yadire kunya ne duk yabi yakamata AJ yace kisamu ki watsa ruwa sai kiyi alwala tsayawa tayi kikam takasa yin komai rike mata kugu AJ yayi yace yau kuma kunyana kike ji tun yanzu bakin rashin kunya yarufo shuru tayi batace komai ba danko hada ido dashi baza ta iya ba murmushi kawai yayi sannan yabar bathroom din yana fita tamaida kofan tarufe tana tsakin murmushi shikam dakinshi yawuce cikin sauri tayi wanka tayi alwala tasanya tawul tafito daidai lokacin yaturo kofan dakin dasauri tahaye kan gado taja bargo tarufe jikinta murmushi kawai yasaki danshi har mamakin pinky yakeyi yanda yaga tachanza lokaci daya waishi takejin kunya ajiye katon trey din yayi sannan yajuya yafita dogon ajiyar zuciya tasaki sannan tasauko daga kan gadon tayi saurin sanya doguwar rigar bacci me Shara shara hade da zumbula katon hijab daidai lokacin AJ yashugo dakin yasameta zaune agefen gado shi abunma daria yabashi .

cemata yayi ta taso suyi sallah tashi tayi takarasa inda yake suka tada sallan suna idarwa yamusu addua sannan yamata tabbayoyi akan addini sosai tabashi amsa shikuwa mamaki sosai tabashi bayan sungama ne dakanshi yaciyar da ita abinci saida takoshi sannan yakwashe kayan yakai kitchen inda yabarta nan yadawo yasameta rufe idonta tayi shikuma yadauketa cak yakaita kan gado.

A hankali yarada mata akunne yace sai kace matar malam irin wannan zumbulelan hijabi haka bata Ankara ba sai ji tayi yafara cire hijabin yana neman rabata da rigar baccin dake Jikinta kara rufe idonta tayi shikuma yahau wasa da ita tuni yafara ruda ta dan tun da take bata taba jin yanda taji a yanzu ba.

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [17:49 ,10/16]

PAGE 60

bakinshi yakai cikin nata yafara tsotsa cikin wani salo sannan yafara kissing din duk wani bangare na jikin ta har yazo kan cibiyarta shima yafara latsa yana wani lumshe ido .

sannan yakoma kan dukiyar fulaninta nanfa yafara fita hayacinshi Dan tunda yake bai taba ganin boobs irin na pinky ba gasu a tsassaye numfashi sama sama pinky takeyi dan tuni yagama ruda ta nanfa zance yachanza kala yashiga mata sabbatu duk da ba

wannan bane rana nafarko da dana miji yataba sanin Taba sai datasha kuka sabida magungunan da ammi tahada mata har dana maida bazawara budurwa .
A ranan dai in takaici maku pinky bakaramar bakar wuya tasha ba !

washe gari kiran sallan farko a kunnan mutanan biyu Aka yishi AJ dakanshi yadauki pinky yakaita bathroom yayi mata wanka hade da gasa mata jiki hawaye kawai takeyi Dan kasanta bakaramin zafi yake mata ba barinta yayi tayi wankan tsarki shikuma yawuce dakinshi yayi wanka sannan yawuce masallaci koda yadawo bangaren zuly yashiga Dan bude ma yatadda kofan bedroom yashiga yasameta tana karatu tana ganinshi tasaki murmushi hade dayin addua tashafa sannan tace baby ina kwana murmushi yasakar mata hade dakarasawa kusa da ita yahadeta da jikinshi yace lafia kalau wifey ya kwanan kadaici murmushi kawai tasaki hade dacewa ya farida .
AJ yace she's fine hope dai komawa bacci zakiyi girgiza kai tayi tace aa breakfast zan fara shirin hadawa yanzu .
Girgiza kai AJ yayi hade da daukanta yakaita kan gado yakwantar da ita sannan yaja mata bargo yarufeta yace ki koma bacci kuku zasuyi komai OK sannan yakai mata peck a kumatu yafita daga dakin yawuce bangaren pinky zaune yatadda ita tana karatun AL Qur'ani saida tagama sannan kanta aduke tace ina kwana tashi yayi yakaraso inda take yace lafia kalau sarkin rashin kunya yanzu bakin rashin kunya yarufu ko shuru tamai ta turo baki hannunshi yakai yaja bakin auch tace sannan yadauketa yakaita kan gado yakwantar hade daja masu bargo yarufesu matseta sosai yayi ajikinshi sai kace ance zaa sace mashi ita
WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [14:00 ,10/17]
PAGE 61
AJ yana fita zuly ta tashi tabar dakin kai tsaye kitchen tawuce Dan harta tadda kuku yafara aikace aikace .

Cike da girmamawa yagaida ita sannan tace yaje kawai zata yi dakanta.
Bayan fitan kuku a kitchen zuly tafara kokarin daura abun break dayake yariga daya gama fere arish din tsoyawa kawai tayi sannan tasoya kwai .
Tana gama wa tadaura hadaddan ferfesun kifin ruwa sannan tasanya ruwan zafi a flask .
Goma saura tagama komai tasa masu aiki suka kai babban parlour dake bangaren AJ.
Sannan tashiga wanka tana fitowa tazauna tayi normal makeup hade dasanya wata dakakkiyar shadda purple color sannan takashe dauri takoma Palo zaman jiran su AJ.

Pinky ce tafara tashi hade da kafe shi da Manya manyan idanuwanta Tana tsakin murmushi Dan wani sonshi taji yana ratsa duk wani jijiyoyi na jikinta dakyar tasauko daga kan gadon tawuce bathroom .
Bude idonshi yayi yaga bata kan gadon sai zuban shower dayaji a bathroom shiya tabbatar mai da tana wanka shima tashi yayi yawuce bangarenshi Dan har sha daya takusa.
koda tafito daga wanka bata tarar dashi ba shiyasa cikin sauri tashirya tasanya wainsu

riga da siket da sukayi matukar zauna mata sannan tazauna agaban dress mirror ta tsatssara kwalliya hade da kashe wani uban dauri sannan tafeshe jikin ta da turaruka fiye da kala biyar tana zaune agaban madubin AJ yaturo kofan dakin yashugo sanye yake da kananun kaya kuma sunyi matukar yi Masa kyau suna hada ido yasakar mata murmushi itama maida mai tayi sannan yace taso muje bangaren wifey nasan tana cen tana jiran mu wani abune yabigi zuciyarta da taji yace wifey dinnan tashi tayi Suka fice daga dakin atare suka jera har bangaren zuly dake kwance akan kujara tana tunanin AJ knocking dinnm da taji anyine yasanyata tashi takarasa tabude kofan tana ganinsu tasaki murmushi AJ kam baisan sanda yajawo ta jikin shiba a hankali yarada mata a kunne wifey kinyi kyau murmushi tasaki hade dacewa kawa Allah ka kyaleni gabanfa amarya muke kara matseta yayi har suka karasa cikin palon suka zauna pinky kam gabaki daya sai taji kanta kaman juya mata yakeyi dan wani kishi daji sosai a ranta .

Dakyar zuly ta babbare AJ daga jikinta sannan takalli pinky da kanta aduke yake tace amarya antashi lafia dagowa pinky tayi suka hada ido sannan cikin tsakin fuska tace lafia kalau ina kwana amsawa zuly tayi hade dakallon AJ tace baby muje kuyi break farida taso muje AJ yana rike da hannunta har suka fita daga sashin zuly pinky kam tana gefen su tana kallon yanda AJ ke nunama zuly soyayya agabanta hakanan ta danne zuciyarta har suka karasa bangaren AJ dakanshi yajama zuly kujera tazauna sannan yaja nashi zay zauna zuly tamai alama da ido akan yajama pinky itama murmushi yasaki sannan yaja kujeran kusa dashi yace madam batare data kalle shiba tazauna dan gabaki daya ranta yagama baci tashi zuly tayi tafara serving dinsu pinky Tamike zata tayata zuly tace aa yi zamanki aisai captain yakulleni in yaga nasa amaryarshi aiki murmushi kawai pinky tayi takoma tazauna saida tagama serving dinsu sannan ta ajiye ma kowa nashi takoma tazauna .

AJ yace yau kuma wani sabon salone kinfa san tare muke cin abincin nan dake make kafada zuly tayi tace yau kaci da amarya girgiza mata kai yayi hade da daukan spoon dinshi yasanya acikin abincin nata yace oya bude baki zuly tace kabarshi zanci dakaina kaidai kabawa farida bata rai yayi yace kibude mana bude bakinta tayi yafara bata abincin har saida takoshi Sannan yafara cin nashi pinky kam Dan dole taketa tura abincin tanata kokarin danne kishinta Dan yanda yake bama zuly Kulawa a gabanta abun yayi yawa kuma harma dacin fuska .



zuly gabaki daya bataji dadin abunda AJ yake mata agaban pinky ba gashi babu yanda zatayi dashi pinky tana gamawa tamike tafara kwashe kayan zuly tamike dasauri tace dakin barshi nakwashi pinky tace aa taya zan zauna inbarki kina aiki murmushi zuly tayi sannan suka kwashe kayan suka kai kitchen suka wanke sannan pinky tadawo tagoge kan dinning din sannan takoma kitchen zuly tace sannu da aiki pinky tace kece da sannu jerawa sukayi suka fito daga kitchen din suka karasa cikin palo AJ yana zaune a 3seater yana kallon news a tsakiya suka sakashi daman kaman jira yake yasanya hannunshi yajanyo zuly tafada jikinshi yace yaudai naga alaman rowan kanki ki kemun zuly

girgiza mai kai tayi sannan a hankali tayi magana tace captain abunda kakeyi ba kyau wallahi Dan Allah nidai ka tsakeni muyi hira kallonta yayi ya harareta yakuma matse ta a jikinshi yaci gaba da kallonshi pinky da tagaji da zama tashi tayi tace bari inje daki zuly tana kokarin tashi AJ yakuma matseta batare data jira jin abunda zasuce tabar dakin tayi hanyan sashinta dasauri dan saura kadan tafashe da kuka a zuciyan ta kam cewa tayi wannan wane irin kishine Dan ita kam bata dauki zuly a matsayin kishiya ba sai yar uwa Tana shiga dakinta tazube akan kujera hawaye suka biyo kunchinta daman tasan dole ta fuskanci wulakanci kala kala awajen AJ Ashe jiya yaudarar ta kawai yayi da yaringa ce mata I love you .

bayan fitan pinky daga dakin ne zuly ranta abace tace gaskiya captain abunda kakeyi baka kyautawa murmushi yasaki yace menene aciki danna rumgume matata hararar wasa zuly ta watsa mai tace baka dai kyauta ba .

Kokarin mikewa takeyi yajanyota tafada jikinshi yace kina nan babu inda zakije hannunta takai tana bubbuga mai kirjin shi tace Allah captain bana son haka cin fuska nefa .

AJ yace naji Allah yamiki albarka ina sonki sosai wifey kidin yar aljanna ce murmushi kawai tasaki sannan tamai wayo ta tashi daga jikinshi ta daura dankwallinta tace kaje kuyi hira da amarya tana gama fadin haka tayi saurin barin dakin tawuce sashinta .

Shiko shafa kanshi yayi yasaki murmushi sannan yamike tsaye yakashe TV sannan yawuce sashin pinky zaune ya tadda ita tana karanta wani English novel let's talk about sex in Islam na shahararriyan marubuciyar nan umm zakiyya tana ganinshi yashugo amma ko daga kanta batayi ba balantana takalle shi !

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [17:01 ,10/17]
PAGE 63

da rana ma zuly dakanta tashiga kitchen tadaura abinci saida tagama komai sannan tadauki wayarta takira AJ tace baby kuzo kuci abinci ko nan bangaren farida zankawo maku AJ dasauri yace aa wifey kinsan fa bana son kina wahala gamu nan zuwa yanzu yana kashe wayan yakalli pinky da hankalinta gabaki daya yana kan littafin da take karantawa yace uwar son s3k banza tamai saida yatashi yakarasa inda take yace dake fah nakeyi kaudar da littafin tayi sannan ta tashi zaune tace menene AJ yace mele ne me hali dai bazay Taba Chanza halin saba inkin ga dama sai kitashi muje part din wifey hararar shi tayi sannan tadauko littafin zataci gaba da karantawa sai kuma ta tuna da nasihohin da aka mata ajiyewa tayi Sannan tamike tabi bayanshi har bangaren zuly .

yanzu kam lahia lau sukaci abincin su dan AJ ko taba zuly bayyi ba ita kuma taji dadin haka suna gamawa suka kwashe kayan kaman dazu sukaje suka wanke sannan suka dawo Palo wannan karan hira sukeyi sosai saidai ba sosai pinky take saka masu baki ba

abincin dare ma tare sukaci sannan suka zube anan palon captain suka fara hira sai sha daya saura zuly tamike tace ni bari inje inkwanta saida safen ku mikewa AJ yayi yakarasa inda take yadauketa cak yayi waje da ita saida yakaita har bedroom dinta

sannan ya direta harara ta sakar mai tace wlhi nidai kadaina mun haka agaban farida nagaya maka ba kyau pinky kam suna fita ta tashi itama tawuce bangaren sabida tana son yin wanka kafin takwanta saima data gama takwanta sannan taji shugowan AJ doguwar jallabiyan shi fara yacire yarage daga shi sai gajeran wando sannan yahaye kan gadon yakwanta kallon pinky kawai yakeyi yanda komi nata ya bayyana tuni yaji shaawar shi ta motsa a hankali yakarasa inda take ya rumgumo ta tabaya ita kuma rufe idonta tayi kamar meyin bacci shafata yafara yi sosai yana latsan dukiyar fulaninta sosai yafara fita hayacin shi saida yazo gabda HQ din sai kuma yatsaya cak sabida minister daya fado mai arai saurin cire hannunshi yayi daga jikinta hade da sauka daga kan gadon yawuce bathroom yasakar ma kanshi shower tuni yaji zuciyar shi namai wani zafi nandanan yaji ko kara taba jikin pinky baya iyayi .

Bin bayanshi tayi dakallo hawaye yabiyo kunchinta da taji alamar fitowar shine yasata rufe idonta ko kallon inda take bayyiba yafice daga dakin yatafi wani dakin yayi kwanciyar shi Dan sam zuciyar shi bata mai dadi meyasa yau yatuno da rayuwar da pinky tayi abaya why abunda yaringa fada kenan.

Bayan fitan shine ta tashi zaune tahada kanta da gwuwa tafashe da kuka sabida tasan dalilin dayasa AJ yaki kusantan ta ayau jiya ma kenan saa taci !

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [14:46 ,10/18]

PAGE 64

dakyar a ranan tasamu bacci yadauketa Dan tunanin captain ya hanata sakat sonshi da bigenshi duk ya cika mata zuciya batada burin daya wuce tajita a jikin AJ batasan tana tsananin kaunar shiba sai yau daya kaura ce mata kwana daya dayin bikin su .

Duk da shima a nashi bangaren ba karamar azabtuwa yayi ba danshi kanshi yasan yana son pinky kuma son da bai taba yima zuly irin saba shi kanshi yarasa wane irin so yake mata ji yayi kaman yatashi yakoma dakin nata sai kuma daya Tuna da minister duk sai zuciyar shi tamai zafi sabida tsananin kishi dakyar dai yasamu yayi bacci .

washe gari da asuba bayan AJ yayi alwala yabuga ma pinky kofa saida yaji ta tashi sannan yafita daga part dinta yawuce part din zuly saidai kunne ya tadda wutan palo shiya tabbatar mai da ta tashi shiyasa bai shiga ba kawai yawuce masallacin dake kofar gida

Bathroom tashiga tayi alwala sannan tafito ta tada sallah koda AJ yadawo masallaci bangaren pinky yakoma ji yayi kaman yashiga dakinta amma sai yafasa haka nan yawuce yakwanta ita kuma bayan tayi azkar ta tashi ta ninke sallayan sannan tafara tunanin zuwa gaida captain batare data cire hijabin dake jikin Taba tafice daga dakin saida ta danyi tafia sannan takarasa kofar dakin hannunta tasanya taburda Handle din hade dayin sallama tashiga yana kwance akan gado amsa sallaman yayi ita kuma takarasa har inda yake ta zukunna tagaida shi da lafia ya amsa kawai hade dajuya kanshi gefe ji kawai tayi tafashe dakuka bakinta narawa tace nasani dole kaji ba dadi a zuciyar ka sabida baka sameni a yanda kake bukata ba Dan Allah kayi hakuri kamance da komai

nasan nidin me laifi ce tausayin tane yadirar mai a zuciya duk sai yaji bai kyauta ba baisan sanda yatashi zaune ba yajanyota tafada kan fadeden kirjin shi yashiga lallashinta kuka takeyi sosai cikin bakin shi yabude yace I'm so sorry lefe nane da naki yarda da kaddara kuma nasan babu Wanda ya isa yawuce wa kaddarar sa sannan yadago da fuskanta suna kallon juna yace kishin ki yasanyani aikata haka sabida ina tsananin kishinki da sonki .

har tabude baki zatayi magana yasanya bakinshi cikin nataa yashiga sha saukar ajiyar zuciyar ta kawai nakeji daukarta yayi yakwantar akan gado hade dafara aika mata da wainsu rikitattun sakonni sannu a hankali yafara rabata da duk wani kayan jikinta tun daga saman kanta yafara Shanta har zuwa kasan ta tuni yafara mantar da ita abunda yafaru Dan itama zagewa tayi tafara nuna ma captain kalar tata soyayyan Dan bakaramin ruda shi tayi ba duk da yabata wahala sosai da safen amma sam bata nuna gajiyawan taba saima kara nuna mai wani salon soyayyar takeyi tuni takara shiga cikin zuciyar shi Dan yasan pinky tama zuly nisa dan zuly bata mai abunda pinky tamai ayau din .

bayan sungama nunawa juna soyayya dakanshi AJ yadauki pinky yakaita har bathroom in takaice maku dai tare masoyan sukayi wanka Dan pinky tacire kunyar shi da takeji ajiya dan yanzu mijinta zata dage tarike .

Tawul yadauka yarufe mata jiki dashi hade da daukanta cak kamar wata baby yafito da ita daga bathroom din yakaita har dakinta sannan ya direta yana tsakar mata murmushi hade da kashe mata ido daya yace kinsan kedin sarauniya ce murmushi pinky tasaki tace waceni in kwacewa sister sarautar ta batare daya bata amsa ba yace baby bari inje inshirya OK tace mai hade da hura mai kiss .

Bayan fitan shine tashafe jikinta da mayuka masu sanya jiki laushi da kuma kamshi sannan tafeshe duk wani lungu da sako nata da body spray da humra .

Bayan nan kuma tabude wardrobe tadauko wata hadaddiyar doguwar riga na atamfa tasaka kallon kanta tayi a madubi taga yanda kugunta yafito sosai Tommy dinta ko kamar bata cin abinci sai dukiyar fulaninta daya kara mata kyau acikin doguwar rigar murmushi kawai tasaki sannan tazauna ta kashe uban dauri hade da zubo da gashin kanta har gadon baya sannan takuma feshe jikinta da turaruka masu matukar kamshi tana gamawa tadauko slifas tasaka shima kalar kayan kada kuso kuga yanda pinky tayi kyau !

bude kofan dakin nata tayi tasauko downstairs daidai lokacin kuma AJ yashugo palon tsayawa yayi ya kare mata kallo yace Masha Allah zan iya cewa nafi ko wane namiji more mata masu kyau sannan yafara karasawa har inda take yasanya hannayen shi tabayanta yace you r cutie I love you so so much baby murmushi tasaki sannan tachanza murya tace I love more habibi.

Hannunshi yakai kan lips dinta yana zagayawa yace ina son lips dinki baby even ur eyes suna kashe mun jiki dukan wasa takai mai a kirji tace kai habibi Kana fasa mun kai dayawa fa captain yace bawani fasa kai yanzu dai kibani lips dinnan nashanye lipstick

dinnan da kika sa waro idanuwa tayi hade dacewa haba habibi daga mata kai AJ yayi yafara kai bakinshi daidai saitin bakinta hannunta tasanya tarufe bakin tace rufa mun asiri kada sister taganga da janbaki daria yayi sannan yace ina binki bashi kin yarda daga mai kai tayi tace nayarda yanzu dai muje nasan sister Tana cen tana jiran mu .

suna rike da hannun juna har suka karasa bangaren zuly!

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [15:49 ,10/18]



zaune suka tadda zuly akan kujera tana kallo dagowa tayi ta amsa sallaman sannan tamike tsaye tana tsakin murmushi tace baby ina kwana AJ tsakin hannun pinky yayi yakarasa inda zuly take yarike mata hannu hade dakai mata peck akan kumatu yace lafia kalau wifey Kin tashi lahia lafia lau ta amsa dashi pinky dake tsaye tace sister ina kwana amsawa zuly tayi sannan tace yaudai anan zamuyi breakfast AJ rike ma ko wacce hannu yayi suka karasa dinning kuma yaja ma ko wacce acikin su kujera zuly tayi serving nasu suna cin abincin suna hira suna daria har suka gama wani nishadi AJ yaji acikin zuciyar shi yanda yaga matan nashi Sun hada kansu sosai yaji dadi dan a zuciyar shi har cewa yayi yafi kowa saan mata dole ma ya matsa ma wancen tuzurun banzan yayi yayi aure

Yauma atare suka kwashe kayan suka kai kitchen Dan AJ ma saida yataya su pinky tana wanke kayan zuly tana dauraye wa tana bawa AJ yana goge wa sai yakife a haka har suka gama sannan suka koma Palo yace basketball yau zaa buga bude baki zuly da pinky sukayi atare sukace captain basketball kuma daga masu kai yayi yace yes duk cikin motsa jiki ne ai bari inje inchanza kaya zuly tace baby ina muka ga kayan wani yin basketball Daria AJ yayi yace kuje akwai kaya achan any color akwai yana gama fadan haka yabar palon yana daria kallon juna pinky da zuly sukayi pinky tace captain wahala kawai zay samu zuly Daria tayi .

acikin sati daya wata soyayya me karfi ne da shakuwa yakara shiga tsakanin pinky da AJ kuma lafia lau pinky da zuly suke zaune sabida komi tare sukeyi .

dayake yau AJ zay koma dakin zuly bayan sunci abinci bayan isha pinky tamike tana hamma tace bacci sister saida safe zuly tace yau bacci yahana mu hira tashi AJ yayi yace muje in rakaki sannan yakalli zuly yace wifey 2min rike mata hannu yayi sukabar dakin suna fita yadauketa cak suka wuce sashin pinky har bedroom yakaita sannan yasanya hannayenshi acikin rigar ta yace baby zanyi missing wainnan shagwabe fuska tayi tace nidai katafi saida safe girgiza mata Kai yayi sannan yace sai kinmun kiss zantafi Hararar wasa ta watsa mai yace toh shikenan ashe dai kina son inkwana anan dasauri takai bakinta cikin nashi sun dadai suna tsotsan bakin juna sannan daga baya pinky tajanye bakin ta tace toh saida safe cweet dreams murmushi yayi sannan yakai mata peck a kumatu sannan yafita yawuce sashin zuly .

Bai tadda ita a palo ba kawai sai yawuce bedroom daga ita sai yar karamar rigar bacci me sharashara gashi sai wani kamshi take zubawa karasawa yayi har inda take yarike mata kugu yasanya kanshi ajikin wuyanta yana shakan kamshin jikinta

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [14:33 ,10/19]

PAGE 66

washe gari tun safe leema takira pinky awaya tace mata zata zo shiyasa bayan Sun gama breakfast takoma sashinta tashiga daura ma leema abun motsa baki idan tazo tana kitchen taji sallamar leema dasauri tafito daga kitchen din ta tare ta suka rumgume juna leema bin pinky tayi dakallo tace kinga yanda kika kara kyau kuwa lallai na yanda captain ya iya kiwo Daria pinky tayi tace hmm kanki dai akeji ya mama fa leema tace tana gaida ki ciwon kafa yadame ta kwana biyu pinky tace Allah sarki mama na .

Aiko zangaya ma habibi sai muje mu dubo ta leema tace lallai kam abu ya kankama sannnan tasamu gu tazauna pinky tace ina zuwa komawa kitchen tayi ta dauko mata abun motsa baki takawo mata sannan itama tasamu gu tazauna .

Leema tace daga gidan su ammi nake ma pinky tace Allah sarki ammina nayi kewarta sosai daidai lokacin AJ yashugo palon Faisal nabiye dashi abaya shi AJ yace aa kice dai yau muna da manyan baki murmushi leema tayi hade da gaidashi sannan takalli Faisal da ya tsira mata ido pinky tashi tayi tawuce kitchen tadawo rike da trey ta ajiye agaban Faisal sannan takoma kusa da AJ tazauna shikuma yajanyota jikinshi yace Allah dai yakama ku Daria Faisal yayi yace kasan Allah bansan leema zata zoba AJ kallon pinky yayi yace kin yarda da maganar da nagaya maki Faisal da leema soyayya sukeyi Daria tayi tace haba no wonder yau aka kirani akace zaa zo leema tace wlhi banson Sherri AJ yace kadai dage kayi aure tunkan leema ta gujeka danka fara zama tuzuru Daria gabaki dayansu suka kwashe dashi sannan pinky tadan rada ma AJ magana a kunne tace bari muje bangaren sister su gaisa da leema OK yace sannan yasaketa tamike tsaye tace leema muje ku gaisa da sister tashi tayi suka bar palon bayan fitan sune Faisal yace abokina naga sai wani fresh kakeyi gaskiya auren nan ya karbe ka harfa dawani kiba ka kara daria AJ yayi yace angaya maka mata biyu wasa ne Faisal yace nafa fara tunanin auren mata biyu daria AJ yayi yace toh wlhi baka isa ba ai leema Kadai ta ishekaa trust me .

Bangaren zuly suka karasa a Palo ma suka tadda ta ita da me aikinta suna hira tana ganinsu tamike tsaye fuskanta dauke da faraa tace aa bakuwa mukayi ne pinky tace wlhi sister tace nace Bari tazo kugaisa zuly juyawa tayi takalli me aikinta tace je kitchen kidauko abun motsa baki sannan tajuya suka gaisa da leema me aikin ne takawo abun motsa baki sannan tafice daga palon nan suka fara hirar dunia .

Sai yamma likis Faisal da leema suka tafi .

AJ dake rike da hannun pinky yace kinsan wlhi naji dadin muamallan Faisal da leema

saidai yakamata takoma gida kafin manya su shiga cikin maganar pinky tace nima tunanin dana yi kenan dazu zan mata maganan insha Allah yau a bangaren pinky aka ci dinner sai sha daya su zuly suka tashi suka wuce pinky tarufe kofan ta .

Duk wani Kulawa AJ yana bawa pinky da zuly Dan so dayawa har mance wa sukeyi su kishiyoyi ne a haka har auren su yakai wata daya da sati biyu .

kamar yanda yasaba idan yana dakin pinky sai yaje yabuga ma zuly daki haka yauma yayi saida yabuga mata kofa sannan yawuce masallaci saidai abunda yabashi mamaki bai wuce ganin zuly bata tashi ba dan idan ta tashi tana kunna wutan Palo dana bedroom kara buga mata kofan yayi nanma yaji shuru abunda yatada matsa hankali kenan sunanta yafara kira da karfi amma shuru a rikice yakarasa bangaren pinky yace yana tunanin zuly batada lafia Dan yata buga mata kofa shuru hankalin ta atashe tabiyo bayanshi bangarenshi yanufa yadauko extra key din dakin zuly sannan suka karasa yasanya key yabude kofan palon atare suka shiga cikin palon pinky takunna wuta AJ yayi upstairs dasauri yana kiran sunan Zuly amma shuru pinky ma bayanshi tabi dan gabaki daya tagama rikicewa yana shiga dakin yaja yatsaya dan ganinta kwance akan gado tana ta birgima tana rike da cikin ta a rude dagashi har pinky suka karasa inda take saidai Sam bata masan suwaye akan taba hankali tashe AJ yadauketa yace ma pinky tadauko mukullin mota dagudunta takarasa bangarenta ta dauko key car din tabude gidan baya yasa zuly pinky kuma tashiga mazaunin driver taja suka bar cikin haraban gidan kai tsaye asibiti mafi kusa suka nufa suna isa Dr yana zuwa nandanan yasa aka kaita emergency room!

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [15:16 ,10/19]

PAGE 67

safa da marwa kawai pinky da AJ sukeyi da suka gaji da tsayuwan ne suka samu kujera suka zauna zuciyoyinsu ba dadi saida suka kusan hour daya da wani abu a zaune sannan doctor din yafito yana share zufa suna ganinshi suka tashi dasauri suka karasa wajen shi pinky ce tayi saurin cewa meke damunta hope taji sauki duk lokaci daya tama Dr din wainnan tabbyoyin kara share zufan dake fuskan shi Dr din yayi sannan yace saidai kuyi hakuri Allah yamata rasuwa AJ da hankalinshi gabaki daya yagama tashi shake dr din yayi yace karya kakeyi taya zakace ta mutu bayan ciwon bai yi tsananin da zaace tamutu ba Allah sarki AJ kamanta da cewa da ciwo ko ba ciwo idan lokacin mutum yayi sai yatafi kuka pinky tafashe dashi dakyar Dr din yakwace kanshi awajen AJ yanda kuka san karamin yaro haka yafara kuka dakin da zuly take suka shiga dakyar kwance yaganta kamar me rai sabida fuskan ta daya kara haske da kyau baisan sanda yakarasa yarikeeta sosai ba yafashe dakuka pinky dakyar ta iya daidai kanta tasamu aron waya sabida basu taho da wayoyin suba sabida hankali ba akwance ba takira sadiq tagaya mai shima hankali tashe yakira su ammi yagaya masu sannan abba dakanshi Yakira Mr president yagaya mai salati Mr president yaringa yi sannan Yakira mami tazo bangaren shi yafada mata hankalin ta ba karamin tashi yayi ba nandanan mutuwar zuly ya watsu

dan suma tuni Mr president yakira me martaba yagaya mai nandanan suka shirya suka biyo private jet hankali tashe su sadiq dasu abba dashi kanshi Mr president suka isa asibitin halin da suka samu AJ aciki bakaramin kara tada musu da hankali yayi ba Dan mutuwar ta matukar girgiza shi pinky tana kuka takarasa motar sadiq tashiga tazauna AJ kuma kamashi sadiq yayi yakaishi motar su Mr president sannan aka dauki gawar suka dunguma gabaki daya Zuwa gidan su Dan kafin suje har mutane suncika gidan Dan kowa kagani mutuwar zuly bakaramin tabashi yayi ba sabida kyaun halinta bayan Zuwan me martaba ne aka mata wanka aka tsitirceta hajiyarta tamata addua tana kuka sannan aka dauketa zuwa kaita gidanta na gaskiya AJ kaman ba namiji ba saidai aga hawaye yana zubowa a idonshi !

Ammi lallashin pinky take tayi Dan kukanta yaki tsayawa balantana data tuno irin zaman da sukayi da zuly sai takuma fashewa da kuka a haka aka dawo daga kaita nansu AJ suka zauna a haraban cikin gidan suna amsan gaisuwa saidai ko ammai gaisuwa dakyar yake iya amsawa .
Toh saidai ince Allah yajikan zuly yasa aljanna tazama makomarta mukuma Allah yamana kyakkyawan karshe Aameen

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [15:47 ,10/19]
PAGE 68

su hajiyar zuly saida akayi sadakan uku sannan suka koma kano cikin kwanaki ukun nan gabaki daya AJ baya cikin hayacinshi danko abincin kirki bayaci sai pinky tazaunar dashi tukunna dakanta tabashi a haka akayi sadakan bakwai shine ma yadan fara tsakin jikinshi yafara dawo wa kamar da bangarenta sam yadaina shiga dan yasama ankwashe kayan gabaki daya hotunan su kuma pinky takwashe ta ajiye .

daman rayuwar batada tabbas kana naka Allah na nashi gashi yanzu wata biyu kenan da rasuwar zuly komi yafara chanzawa .

AJ dake zaune akan kujera cikin pinky yake shafawa yace nifa ban yarda da wannan katon cikin ba daria tayi tace meka gani kashe mata ido daya yayi yace kamar nayi ajiya acikin nan daria tafashe dashi Dan ita kanta tana jin wani iri kwanakin nan
AJ yace yaushe rabonki da ganin period dinki nazari tafara yi sannan tace kaman so uku ken...
Tun kafin takarasa AJ yace maza tashi kishirya muje asibiti kallonshi tayi tace habibi menene na zuwa asibiti AJ yace gwada munke zaayi make kafada tayi tace menene sai munje asibiti tunda ga abu yafito fili AJ yace ban yarda ba saifa kin tashi munje shagwabe fuska tayi sannan ta tashi zaune tace toh Saidai ka goyani ka kaini har bedroom in sauya kaya Daria yayi yace abun me sauki zukunnawa yayi yace oya hau daria tayi sannan tahau tace habibi bayanka akwai dadi AJ yace anjima nima sai kinmun abunda yafi goyo bedroom yakaita dakanshi yacuro mata kayan da zata sa saida ta shirya sannan suka sauko downstairs pinky tace amma ni zanyi driving kallonta AJ yayi yace bafa ki isa ba

kinsan nakashe wannan tuntuni sannan yarike mata hannu suka karasa parking space family hospital dinsu suka nufa gwajin farko Dr yace tana dauke da ciki har na tsawon wata biyu da kwana hudu AJ rumgume pinky yayi yana kissing dinta sannan yace Dr kana da babban tukwuici zaka ji alert godia dr yamai sannan suka bar asibitin kai tsaye Villa suka wuce a Palo suka tadda mami dasu mimi suna cikata da surutu bayan Sun gaisane mami tace yau hala abishir din me aka maka kaketa washe hakora kanshi yashafa pinky kam tuni ta tashi tawuce bangaren su mimi dan tasan AJ zay aika yagaya wa mami ita kam bada ita ba wannan rashin na ido kara shafa kanshi yayi sannan yace daga asibiti muke mami nakusa zama baba murmushi mami tayi tace kaidai kunyanka ragagge ne alamin

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [16:15 ,10/19]

PAGE 69

acikin watan da muke ciki acikin sa pinky da leema da kuma AJ da Faisal da su ammi suka shirya Dan Zuwa ganin yan uwan leema dake kaduna tudun wada duk da bawani karban arziki aka musu ba amma hakan bai dame suba sabida Sudai burinsu leema tadawo gaban yan uwanta kafin aurenta da Faisal a hakan ne kawai zasu iya shiryawa da yan uwan nata yayan baban tane yashugo gidan ya tadda su ammi yakuma ga leema sunanta yakira yace halima kece Ashe zaki dawo hawaye yafarayi sannan yasamu waje yazauna yace in bamu nemi yafiyar kiba halima sai wutar Allah tacimu sabida Munci amanar da Dan uwan mu yabar mana Dan Allah ki yafe mana itama kukan takeyi tace babu komai baba Allah ya yafe mana gaba daya saida suka shirya da yan uwan ta sannan su ammi suka tafi akan ranan daurin aure sai ta taho abuja gaba daya .

nan aka fara shirye shiryen bikin leema da Faisal duk wani hidima pinky ne takeyi duk da cikinta yana cikin na wata hudu ne saidai bata laulayi bata komai tun daga dubai mummy Faisal tayi order din kayan lefe Kuma cikin satin da muke cikine aka kai lefen har kaduna leema Kam sosai take samun gata wajen yan uwanta .

ranan juma'a aka daura auren Faisal tahir da haleema dahiru kuma a ranan akaje aka dauko amarya daga kaduna zuwa abuja sabida zaayi dinner da dare wanda gabaki daya AJ ne yadauki nauyin komai .

Kada kuso kuga yanda leema tayi kyau tafito saf amarya da ita takwas aka fara dinner aka tashi karfe sha daya daganan direct gidan ta aka wuce da ita ana kaita Kowa ya watse aka bar ango da amaryar sa.

WAYASAN ASALINA 📚 SAUDAT IDRIS NOVEL 📕 📚 :سودة إدريس [16:35 ,10/19]

PAGE 70

leema da Faisal soyayyar su suke sha sosai Dan kome zatayi idan Faisal yana gida saiya tayata a haka auren yakai wata daya cikin pinky kuma yashiga na wata biyar tuni AJ yafara order din kayan baby daga dubai .

Ammi dake bangaren abba a zaune taji sallaman megadi lekowa tayi megadi yace wata

matace take  son ganin  alhaji ammi cewa  tayi  yashugo da  ita  sannan  takoma  tagaya ma abba  suna  zaune apalo tayi sallama tashiga su  abba  suna  ganinta suka  tashi  tsaye sukace bilki  hawaye tafarayi tace  nazone in nemi gafarar ku  tunkan in mutu  komawa  su abba  sukayi suka zauna  sannan  ita  tazauna  akan carpet  tace  kuyi hakuri ku yafemun  ammi  tace  me kika  mana  share hawayen  fuskanta tayi sannan tace  niche  nayi sanadiyan  bacewar  farida kuma dakaina nakaita har  kofar gidan  karuwa  salati su  abba  suka  dingayi ammi  tace  me muka miki kika  aikata  wannan babban laifi bilki tace sabida nasha  kaima  alhaji  hari  akan son dana  ke mai amma saidai kaman baisan  ina  yiba  Dan  sabida haka nakamu da ciwon hawan jini nikuma ne  alkawarin  nima  sai  nasashi  kuka kamar  yanda yasani ganin  yana matukar  son  farida  shiyasa  nadauketa .

Mamaki ne  Yakama su  abba  ammi  tace  toh  duk  munji bayanan ki  tashi  kitafi  Allah  ya yafe mana gaba  daya  abba  yace  wallahi babu  inda  zatace  saina  daureta  sai  an hukunta ta  hakuri ammi tafara bashi tace  kayi  hakuri tunda  anga  farida ai komi yawuce  dakyar ta rokeshi  sannan  takalli bilki su  tace  tashi kitafi  bayan  fitan tane  abba  yace  amma  ta cucemu  bazan  taba  yafe mata ba  saiki  kira  little kigaya mata  girgiza kai  ammi  tayi  tace ba amfanin  gaya  mata  tunda  yanzu  tasamu duk abunda  tarasa abaya.

ranan  lahadi  pinky  ta  sumbulo  baby girl  dinta  me kama da babanta aiko ranan  suna taci sunan  marigayiya  zulaiha  amma  ana  kiranta  amatullah  duk  wani  gata  shi  ake bawa amatu.

Bayan  shekara biyar  AJ yasa  mar  ma  pinky  makaranta  a  city  university  dake  US zata ci gaba  da  karatun  law  dinta shikuma  Ankara  mai babban  mukami .

saidai  tun  bayan  haihuwan  amatu bata  kuma  samun  wani  cikin ba  leema  kam yaronta daya  ana kiranshi  Khalifa  lafia  lau  suke zama da Faisal Dan  kullin sai  kara  kaunar juna sukeyi  .

Mama magajia Kuma ta  auri  wani  tsohon  saurayinta  da  suka  taba  harka ada  suna dai zaune a  wannan gidan da  pinky ta mallaka mata  .

Hajara ma  takara  haihuwa  tasamu  Mace  taci  sunan  pinky  wato farida ana kiranta  cutie  .

Dasauri  tafito  daga  dakin ta  tana  rike da  handbag  dinta  tace  gani nan  nafito  tsaki AJ yasaki  yace  flight din  karfe tara fa zamu bi  pinky  hade hannayenta  tayi tace  afwan  habibi gaba  yayi  tana  binshi abaya  gidan  baya  suka  shiga  driver  yajasu har  airport  suna shiga jirginsu yatashi  zuwa  sararin samaniya

Alhamdulillah